SHAGALALLIYA!

HADIZA D/AUTA

DEDICATE TO HANNAH SUHANA

Free book kuma Labarin barkwanci.

LAMBA TA FARKO.

Aguje ta isa dandalin matasan ta tsaya a kansu dafe da ƙirji tana haki, yayin da take so ta yi magana amma ta kasa tsabar gudun da ta sha. Dukansu suka bi ta da kallo cike da mamaki a kan fuskokinsu, suna jiran su ji abin da ya kawo ta, saboda sanin halinta. Musamman Mani da ya kasa ɗauke idanuwansa a kanta, masu ɗauke da ƙatuwar hararar da ƙiris ya rage ya kai mata hannu, saboda bai raba ɗaya biyu a kan cewa wurin sa ta zo. Ganin hakin ya ƙi barin ta ta faɗi zaune daɓas a cikin ƙasa tana rabon ido cikin rarraba magana da haɗiyar yawu ta ce masa,

"Ka..kawu Mani, inji Kandala..wai.. wai ta ce na kira ka asiri rufe ka je ka ci kwaɗon garin kwakin da ta..."

A zabure ya miƙe tsaye yana wurga mata daƙuwa kafin ya riƙe ƙugu cikin fusata ya ce,

"Wai ke wace irin tonanniyar yarinya ce ke? To don ubanki ki je ki ce mata ba na ci na ƙoshi!"

"An gama kwaɗon yanzu yanzun nan! Kuma ai kai ka ce idan an yi a sanar da kai tun kafin ya yi ruwa ya lalac..."

Cikinta ya yi kamar zai kai mata duka, ta yi hanzarin dunƙulewa wuri guda tana ihu, haushi ya saka shi shura talkamansa zuciyarsa cike da takaici ya bar wurin.

Saboda tonon sililin da ta yi masa a cikin abokan hirarsa. Hannuwansa zube a cikin aljihunsa ya sha kwana ko waige babu tsabar shaƙiyancin da abokan suke ta yi masa, a kan idan ba ya cin kwaɗon ya kawo musu tun kafin ya lalace. Amma hakan bai hana ta ɗaga murya ta sake cewa ba,

"Dumamen da ka ce a rage maka ma yana tukunya!"

Babu shiri wasu daga cikin abokan nasa suka fara dariya, yayin da wani daga cikinsu ya kalle ta a lalace ya ce,

"Ke kam Bintoto an yi watsatsiya! Shi kenan ba za ki iya rufa masa asirin ba, duk da jan kunnen da aka yi miki a kan ki kira shi asiri rufen?"

Ta miƙe tsaye tana turo baki ta shiga kakkaɓe zaninta da ya kwaso ƙasa tana cewa,

"To ai na faɗa masa asiri rufe ko kai ba ka ji me na ce ba?"

Ta ƙare maganar tare da murguɗa baki, zaburar da ya yi da nufin kai mata duka ya sa ta bazama da gudu tana faɗin,

"Allah Ya isana idan ƙato ya dake ni."

Ya bi ta da kalolin zagi tana yi masa gwalo. Sai da ta sha kwanar da za ta sada ta da gida ta zaro dogon kare a cikin karan da ke ƙofar wani gida, sannan ta fara yin mota da shi tana gudu tana faɗin,

"Ziiiiiiiiiih! Ba burki ba burki! Duk wanda na kaɗe yasin babu ruwana!"

Haka take ta zuba gudu da dogon karen tana nanacin babu burki har ta ci karo da wani yaro da ke ɗauke da bokitin awara a kansa, wanda fitowarsa kenan daga gida zuwa wurin talla. Babu aune sai jin ƙarar faɗuwar bokitin tare da tulin awararsa da

ke cike fam ko rufuwa ba ya yi. Babu jinkiri awara ta watse gabaɗaya ta baje cikin ƙasa. Yaro ya dafe kai yana tsalle tare da ihun faɗin,

"Wayyo ni awarata! Wallahi na rantse da Allah sai an biya ni awarata!"

Kafin ka ce me mutane sun fara taruwa wurin suna tambayar mafari. Bintoto ta rike ƙugu tana kallon awarar da ke watse cikin ƙasa tana huci tare da zaro ido ta ce,

"Kam buhun uban nan kai! Me kake nufi ne? Lalle ma ni ce zan biya ka awarar? Lalle ma yaro!"

Abin da ya faɗa ya harzuƙa yaron ya yi kanta cikin zafin nama ya ruƙunƙume ta yana ihun faɗin sai ta biya shi awararsa. Ta shiga kokawar ƙwatar kanta cikin fushi tana faɗin,

"Tun farko ba sai da na faɗa maka motar babu burki ba ka ƙi ji? To ai yanzu sai na ga uban da zai sa a biya ka awarar!"

Nan take dambe ya sarƙe a tsakanin Bintoto da mai awara, mutane suka yi dafifi ana ƙoƙarin raba su suna ƙin bari, har sai da wani dattijo ya nemo kare ya fara kai musu duka, sannan suka daina yunƙurin sake yin wani damben. Daga nan aka fara tambayar ba'asin mafarin rikicin, da aka gano Bintoton ce ba ta da gaskiya kai tsaye aka kwashe sauran awarar da ta rage. Saboda tuni yara sun daka mata wawa sun cinye mara ƙasa sai kaɗan aka bari.

Ƙeyarta aka tasa sai gidansu da bokitin awarar, tare da mai awarar da ke gaba yana rantsuwar ko da bala'i sai ta biya shi kuɗin awararsa.

Ɗandɗano.

Daga Alƙalamin D/Auta✍

SHAGALALLIYA!

HADIZA D. AUTA

Labarin Barkwanci.

LAMBA TA BIYU

https://chat.whatsapp.com/ICmrsyihZBzLrpXfmM7DyQ

Suna zuwa ƙofar gidan ta yi wuf ta faɗa cikin gidan tana faɗin "Wallahi Kandala ƙarya suke yi mini ba ni ce na zubar da awarar b..."

Mutumin da ya raba su faɗan ya bi bayanta da kallo cike da takaici, sannan ya fara rafka sallama wata bayan wata cikin ɗaga murya. Daga can ciki muryar Kandala ta fara tashi tana nufo soron gidan tana zuba faɗa, don tafiya take yi tana gyara zanin da ke ɗaure ƙugunta har cin tuntuɓe tana faɗin,

"Sai na ga wanda zai saka ni biyan awarar tun da an ce da ku kuɗin banza gare ni! Haka kawai a dinga ɗora wa yarinya jarfa kullum ba za a bar ta ta huta ba sai an ce ga abin da ta aikata? To ahir ɗin ku Wallahi Allah kurwar Bintotona kur take a

kanku duk sharar da kuka zuba mata sai na kakkaɓe ta! Don haka gane za ku gan ta don ta Allah ba taku ba billahillazi. Awara kuma sai na ga wanda zai saka ni biyan ta a kaf faɗin garin nan na Maidala! Tun da sharri ake yi mata ta ce ba ta san ta zubar ba."

Ta ƙare maganar tare da kwance ƙullin goronta da ke gefen kallabi ta gutsura, sannan ta mayar da shi a gefen zaninta ta ɗaure shi ta sake sokewa a jikinta. Ta shiga taunar goron tana ƙarewa kowa kallo ɗaya bayan ɗaya alamun ko daidai take da zamanin wanda ya ce cas.

Mutumin da ya jagoranci zuwan baki a sake ya dinga kallon ta kafin ya yi magana cikin tausasa murya ya ce,

"Inna kin ga yaron da ta zubar wa awara, ni zan wuce ne na ga suna rigimar shi ne na raba su. Sannan kin ga bokitin fa gabaɗaya ta zubar masa da kaya, saboda Allah hakan da ta yi kin ga ta kyauta?"

Ya ƙare maganar tare da nuna mata cikin bokitin awarar, in da sauran da ta rage ita ma ta nashe da ƙasa. Kandala ta bi bokitin da kallo a lalace sannan ta yatsina fuska ta ce,

"Ta ina ko zan ga rashin kyautawarta tun da ba a gabana aka yi ba?"

Sannan ta juya gefenta ta riƙo hannun Bintoto da ke raɓe jikinta tana muzurai, ta fito da ita gaban mutumin ta sake cewa,

"Fito tsakiya ki tsaya tsaf ki yi bayanin abin da ya faru, tun da dai ba kashe ki za a yi ba don kin zubar da awara."

Bintoto ta fito gabanta ta tsaya tana muzurai tana hararar yaron sama da ƙasa sannan ta turo baki ta ce,

"Kin san Allah Inna; idan har ni ce na zubar kwarankwatsa dubu ta faɗo a kan Malam Idi. Kuma idan har ni ce na zubar ba sharri suka yi mini ba; wallahi Allah Kandala na yarda aradu ta faɗo miki duk lokacin da aka yi hadari Kandala. Saboda ban ma gan shi ba, amma ya ce ni na zubar masa da awara don yana so a ce ni na yi wannan ta'asar. Kuma fa Innarsa ce ba ya so ta dake shi shi ne ya ce ni ce..sannan ai ke ma kin sani ba zan aikata ba ko Kandala?"

Ta ƙare maganar tana langaɓe kai ta koma alamun tausayi cike da son Kandala ta amince da zancenta. Amma maimakon ta yi nasara a kai sai Mutumin ya tari numfashin Kandalar da cewa,

"Ki faɗi tsakaninki da Allah Bintoto ba ke ce kike tuƙa motar kare kika kaɗe shi ya zubar ba?"

Kowa ya zuba mata ido a lokacin da ta shiga rantse-rantsen ba ita ce ta zubar ba, amma zancenta na ƙarshe da ta dire ya tona gaskiyar ƙaryar da take ƙoƙarin kartawa domin ta wanke kanta. Saboda kallon da ta ga ana yi mata ya sa ta fashe da kuka cikin maganar tana cewa,

"Sai da na ce masa babu birki amma ya tsaya motar ta kaɗe masa awara. Kuma tun da ba ni ba ce ai ya je wurin karen da ya yi aikin sai ya biya sh...Wallahi Kandala shi ne ya ƙi janyew..."

Mugun kallon da ta wurga mata haɗe da dundu a baya ya sa ta fasa ƙara tare da barin wurin da gudu ta yi cikin gida tana zagin mai awarar, tare da jera masa kalolin ba ta yafe ba tun da ya ta sa aka dake ta a banza.

Jikin Kandala yana tsima ta fara kumfar bakin faɗin, "In dai kuɗin awarar da kika zubar ne ko nawa ne zan biya shi tun da ba da tsiya na zo duniya ba. Kuma ko gobe kika zubar zan biya ai Allah ba azzalumin Sarki ba ne ba."

Sanin halinta ya sa Mutumin ya yi tsaye sai da aka ƙididdige awarar da ke cikin bokitin sannan aka haɗa kan kuɗin da wadda ya ce an yi masa lissafi gida tun kafin ya fito. A nan Kandala ta yi tsalle ta dire a kan cewa ba za ta biya shi kuɗin duka ba, sai dai a ware wadda ke cikin bokitin ya je ya wanke tun da shi ma da laifinsa.

Da lallami da ban-baki Kandala ta biya kuɗin awarar tana masifa sannan taron ya watse. Bayan ta gama dungure wa mai awara kai a kan duk ya kuskura ya bari ta sake zubar masa da kaya babu ruwanta.

Ta juya cikin gidan tana balbala faɗa tare da ƙwala wa Bintoton kira a kan ta ɗauko asusunta a fashe ta cire kuɗinta don ba kyauta ta biya mata ba. Bintoto da ke bayi ta sha jinin jikinta ko motsi ta kasa yi. Saboda sanin idan ta fito za ta iya dukan ta, hakan ya sa duk kiran da take yi mata bai sa ta yi motsin kirki ba. Sai da ta ji ta nufo bayin tana faɗa bayan ta gama bincike ta ko'ina cikin gidan ba ta gan ta ba.

Tsul Bintoto ta kama guntuwar katangar tasu ta dira ta bayan gidan daidai lokacin da Kandala ta faɗo bayin.

"Wayyo Allahna!"

Abin da ta faɗa kenan a lokacin da ta faɗi ƙasa ƙugunta ya daki dutse tsabar tsoron ta kama ta. Kandala ta leƙo kanta tana faɗin,

"Fitinanniyar yarinya! Ko ki dawo gida ki kawo asusunki na ɗauki kuɗina; ko kuma na tattara miki kayanki ki koma gidan Ubanki."

Bintoto ta miƙe riƙe da ƙugu ta fara ɗingisa ƙafafuwa tana yi tana waigen Kandala da ke tsaye katangar tana faɗa. Tare da yi mata kashedin kada ta je ko'ina ta dawo gida sai ta biya ta kuɗinta. Amma hakan bai hana ta tsallake gidan ta faɗa wani gida ba.

Kandala ta fito bayin ta shiga neman asusun lungu da saƙon ɗakinta. Saboda ba ta san inda ta ɓoye shi ba, domin duk lokacin da ta saka kuɗinta canza masa wurin ajiya take yi. Cikin sa'a ta ga asusun ta fito da shi tsakar gida tana cigaba da faɗan, kai-tsaye ta fasa shi ta haɗa kan kuɗin sannan ta cire nata ta naɗe mata canjinta a gefen ɗankwali. Zuciyarta cike da tunanin borin da za ta yi a lokacin da ta ga asusun nata a fashe, hakan ya sa ta tanadi dogon kare sannan ta zauna zaman jiran dawowarta.

Ga mai buƙatar group ɗina ga link

Domin samun littafin a kan lokaci kuma babu jira ya biya 1k ya same shi a Telegram. 1230094555 Access Bank Hadiza D Auta Ibrahim. Shaidar biya ta wannan layin: 08022014771.

D. Auta ce✍

SHAGALALLIYA!

HADIZA D. AUTA

DEDICATED TO HANNAH SUHANA

LAMBA TA UKU

https://chat.whatsapp.com/ICmrsyihZBzLrpXfmM7DyQ

Haka Kandala ta yi ta mita har zuwa yamma, inda take ta zuba idon dawowar Bintoton amman shiru kamar an shuka dusa. Dole ta saɓa zaninta ta yafa ta fita zuwa neman ta gida-gida, sai dai duk inda ta je ce mata ake yi ta zo amma ta fita, ko kukma a ce mata ba ta je ba. A jigace ta dawo gida tana sababin faɗa tare da cin alwashin irin dukan da za ta saka kawunta Mani ya yi mata idan har ta yi nasarar kama ta.

Sai dai abin da ba ta sani ba tun lokacin da za ta je wani gidan da ke maƙotaka da su; wasu yara suka shiga gidan da gudu suka sanar da ita ga Kandala nan zuwa, cikin rawar jiki ta miƙe daga wasar ƙasar da suke yi ta yi soron gidan ta ɓoye bayan

ƙyaure sannan ta sha jinin jikinta. Kasancewar soron da duhu hakan ya sa har ta wuce ba ta san da ita a saƙon ɓoye ba, sai dai tana ganin Kandalar ta shige gidan da bambamin faɗa ta fito aguje ta yi gida. A miliyan ta faɗa ɗakin Kulu ta shige ƙarƙashin gado tana sauke numfashin wahala.

Leƙo kanta ta yi daga cikin ƙarƙashin gadon tana sauke numfashin kamar ta shiɗe ta ce wa Kulun,

"Don Allah Kulu idan ta zo nema na ki ce ba ki gan ni ba."

Kulu da ke zaune tana ƙullin kukar miyar da take siyarwa; wani kallon raini ta fara yi mata sannan ta samun damar cewa,

"Wallahi ni kam ba za ki saka ni yi wa Inna ƙarya ba, haka kawai ki sa ta zo ta saka ni gaba da faɗa ina zaman zamana lafiya. Don haka sawunki a likkafa ki fito, saboda duk ta tambaye ni wallahi sai na faɗa mata gaskiya ba za ki saka ni yin ƙarya ba."

Bintoto daga can ƙarƙashin gadon ta murguɗa mata baki sannan ta ce,

"Ni ko na rantse da Allah sai na kashe miki ɗiyan kaji duk kika tona mini asiri."

Babu shiri Kulu ta kafe ta da ido a lokacin da take ƙoƙarin ƙulle wata ledar kukar da ke hannunta, kai-tsaye ta ajiye ledar ta fasa ƙullewar cikin masifa ta nufo bakin gadon gadan-gadan don daman cike take da kalolin rashin kunyar da take yi mata, a zafafe ta duƙa ta janyo ta ƙii iya ƙarfinta tana faɗin,

"Fitar mini daga ɗaki marar kunyar banza fitsararriya!"

Bintoto ta ƙara komawa tare manne jikinta riƙe ƙarafunan gadon ta ƙarƙashin gadon tana faɗin,

"Ai na rantse da Allah ba zan taɓa fita ba tun da ba daga gidanku kika zo da ɗakin ba!"

Ita ko Kulu ta nace a kan dole sai ta fitar mata ɗaki ko kuma ta jibge ta, da haka rigima ta kacame a tsakaninsu har Kulu ta ci nasarar fito da ita ta ƙarfin tsiya, saboda ƙarfi ba ɗaya don ta girme ta sosai ƙarfin hali ne kawai ɓarawo da sallama.

Ai ko fitowar Bintoto ke da wuya ta yi cikin Kulu da duka kamar wata mai ƙarfin gaske. Kulu ma ta cire tsoron Kandala ta saki jiki ta dinga jibgar ta iya ƙarfinta tamkar an ba ta umarni. Wuya ta sa Bintoto ta fara ihu tare da kiran sunan Kandala a haukace tana faɗin ta yi sauri ta zo Kulu za ta kashe ta. Amma ganin Kandalar ba ta zo ba kuma ba za ta iya da ita ba; hakan ya sa ta ratumi ƙwaryar kukar Kula ta juye mata kukar duka a jikinta, tun daga fuskarta har tsakiyar ɗakin duka kukar ta barbaɗe, sannan wadda ta ƙulla ita ma ta dinga farfashe ledodin tana zubarwa a tsakar ɗakin tana faɗin,

"Ni za ki daka? B ni kika daka a banza ba! To wallahi na rama ni ma!"

Tsabar baƙinciki da takaici ya sa Kulu tsayuwa riƙe da ƙugu tana kallon ta'adin da take yi mata baki a sake. Cike da mugun jin haushin ɓarnar da ta yi mata bayan asara; Kulu ta bi ta da kallo ranta a matuƙar ɓace ta yi kanta tamkar wata zakanya, cikin matsanancin fushi ta fisgo Bintoto sai jin ƙarar rugujewar kwanonin jeren ɗakin Kulu Kandala ta jiyo rifff. Wadda shigowarta gidan ke nan daga yawon neman Bintoton ranta a ɓace tana wassafa irin dukan da za ta yi mata idan ta riƙa ta.

Gabaɗaya kwanonin da aka yi wa Kulu jere da su duk sun zubo musu a jiki, don ko da Kandala ta shigo ɗakin ta tarar da Kulu saman Bintoto a tsakiyar kwananin ta taushe ta tana ta kai mata kalolin duka inda ranta ya yi mata daɗi. Ita ko sai ihun neman ceto take saboda har da kwanonin Kulu take haɗawa wajen hushe haushin ta ga Bintoton.

Babu zato ta ji muryar Kandala a saman kanta tana salati, hakan ya sa ta yi saurin zabura ta ɗaga Bintoton da ke ta kuka iya ƙarfinta tana faman kiran sunan Kandala ta zo za a kashe ta.

A firgice ta miƙe ta yi wurin Kandala tana ihun wayyo Kulu ta karya mata hannu, Kandala kam saboda mamakin irin abin da Kulu ta aikata mata ko motsin kirki kasa yi ta yi, sai da ta ga Bintoto da hannu a sage tana ihu sannan ta dawo natsuwarta. Cikin ruɗewa ta kalli Kulu a masifance ta ce,

"Allah ya toni asirinki munafuka! Ashe daman maganar da Bintoto take faɗa mini kullum a kanki gaskiya ce? To Wallahi bari Mani ya zo kin gama zama cikin gidan

nan baƙar almura mara imani... ke tun kafin ya zo ma maza ɗauki mayafinki ki bar mana gida tun da babu kuɗinki cikin ginin shi. Sannan ni Kandala uwar Mani daga yau na haramta miki zama cikinsa ki je na kore ki kuma na sake ki saki uku ringis ƙwarara. Gayyar na ayya gayyar tsiya wadda kakanki har ya bar duniya ko likkafanin da za a saka masa sai da aka bashi sadakarsa tsabar tsiya irin ta zuri'arku. Bayan ficika bai bar wa ubanki gado ba, haka ya bar shi yana watangaririya a cikin gari da riga guda ƙyalau-ƙyalau kullum rai da rai kamar fatar dabbobi."

Kulu ta fashe da kuka tana ba ta haƙuri amma Kandala ta kafe dole sai ta bar gidan, dole ta ja mayafinta ta fice tana kuka iya ƙarfinta. Bayan fitarta gidan Kandala ta dawo da kallon ta ga Bintoto hankali a tashe ta riƙo ta suka fito gidan tana ihu da kuwwar wayyo Kulu ta karya mata hannu.

Ba ta zame da ita ko'ina ba sai gidan mai ɗori, da ƙyar da walahaula aka gyara wa Bintoto hannun don Kulu ta goce ta, sannan suka dawo gida ta shinfiɗa mata tabarma ta kwanta sai nishi take yi tana sharar ƙwallah. Kandala tana mata fifita tare da jera mata sannu tana mita har ta samu ta yi bacci, sannan hankalinta ya kwanta ta dawo jimamin kuɗin da Bintoton ta sa ta kashe a wunin ranar don ta sani ficika ba za ta yi ciwon kai ba a cikin kuɗinta da ke asusu. Saboda har ta sayi wani sabo ta mayar mata da kuɗin kamar yadda ta gan su.

Tana zaune tana tsine wa Kulu a ranta, don daman can bala'in haushin kulun take ji, saboda yadda take cin zalin Bintoton a duk lokacin da ta fakaici idonta.

Sallamar Hari ce ta katse mata zancen zucin da ta ke yi, cikin sauri ta washe baki tana yi mata lale marhaban, saboda ba ƙaramin girmama Harin ake yi ba a cikin garin nasu na Maidala.

Shin wace ce Hari?

1k ne kacal ku mori laratunku babu jira. 1230094555 Access Bank Hadiza D Auta. Shaidar biya ta wannan lambar: 08022014771.

D. Auta ce.✍

SHAGALALLIYA

HADIZA D. AUTA.

LAMBA TA HUƊU.

Jikin Kandala yana rawa ta miƙe da nufin kawo mata sabuwar tabarma, amman Hari ta nufi wata kujera 'yar tsugunno ta dawo wajen da su Kandalar suke ta ajiye ta zauna, sannan ta ce da Kandala da ke ƙoƙarin shigewa ɗaki da nufin ɗauko tamarma ta ce,

"Ki dawo kawai Inna Kandala ai na samu abin zama."

Kandala ta waigo tana washe baki ta ce,

"Da dai kin bari na kawo miki tabarmar ta fi kujerar daɗin zama, ko ba komoi kya miƙe ƙafa ki sarara ga shi kin kwaso hanya."

Hari tana dariya ta ce, "Babu komai Inna, dawo abin ki ai nan ma ya yi mini, da ma can gaishe ki kawai na zo yi sauri nake yi, saboda ana nema na a can birnin."

Kandala ta dawo tana wasar baki ta ce, "Ai kin kyauta, gara da kika biyo a yi zumunci, ko banza Hausawa sun ce a rabu a gana arziƙi ne."

Hari ta washe baki tana cewa, "Haka ne Inna, ai ya zama dole gare ni na zo gaishe ki ko don ki yi mini addu'ar da kika saba."

Tana gama maganar ta kai kallonta ga Bintoto da ke barci ta sake cewa,

"Bintoto lafiya ko? Na ga tana barci da wannan yammacin haka Inna. Ko dai ciwo ta ji ban da labari? Na ga hannunta da sabon ɗauri.

Kandala ta dawo inda take farko ta zauna, sannan ta ɗauki mafefeci ta ci gaba da yi wa Bintoto fifita sannan ta ce,

"Kin san 'yar taku da rashin jinta Hari, to yau ma garin jan maganarta ne ta jayo matar Mani saura ƙiris ta nakasa ta a banza, don dai Allah bai nufa ba kuma ya ya tsare abin ya tsaya a gocewar hannu, kin gan ta nan; yanzu muka dawo daga wurin mai ɗorin, ta sha kuka kamar babu gobe."

Hari ta ɓata fuska cikin damuwa ta ce, "Ni na rasa wa Bintoto ta gado da wannan rawar kan nata, don kowa ya san daga Habi har Buba babu wanda yake da hayaniya a cikin su, amman ita kullum daga wannan sai wancan?"

Kandala ta goge guntuwar ƙwallarta da ta taru gefen idonta sannan ta ce,

"A kan rashin jinta yau har jikka uku da rabi ta sa na salwantar, ga shi sallah ta ƙarato duk tarin kuɗin da nake yi, ina yi ne kawai a kan ɗinkin da nake so na ɗinka mata ta fito kamar kowa, amman yanzu ta jawo kuɗin sun samu mugun giɓi, ban kuma san har yaushe zan sake tara wasu kuɗin ba."

Hari ta yi shiru na ɗan lokaci tana nazari sannan ta ce,

"Wai Inna ko dai za ki ba da ita na kai ta birni ta yi aikatau? Kin ga idan ta dinga aikin za ta samo muku abin da za ku dinga ɓatarwa ke ma ki huta faɗi-tashin da kike yi. Don a ganina gara aikin ya fi, da wannan yawon ɗaukar maganar da take yi miki a cikin gari."

Kandala ta yi saurin girgiza kai tana faɗin, "Ina! Ina! Daina faɗa Hari, ai ke ma kin san ba zan iya rabuwa da Bintoto ba, saboda ita nake kallo a madadin Habi idan na rasa ta kusa da ni ban san wane irin hali zan shiga ba. Don haka gara ɗaukar maganar da a ta yi mini nisa ba zan iya ba gaskiy...."

Nan take Kandala ta fashe da kuka wiwi har da fyace majina da gunjin kuka. hankalin Hari ya tashi ta fara roƙon ta a kan don Allah ta yi haƙuri ta daina kukan, saboda girman abin bai kai yadda ta ɗauke shi ba. Saboda kukan nata Bintoto ta tashi daga barcin da take yi, ta miƙe zumbur saboda ta manta da tana da wani ciwo a jikinta, ai kuwa sai ga ta da komawa ta kwanta babu shiri tare da fasa wata uwar ƙara tana faɗin,

"Wayyo hannunta!"

Kandala ta ja ta jikinta tana ci gaba da kukanta tamkar wadda aka ce a ranar za a raba su, da ƙyar Hari ta shawo kanta ta daina kukan, sannan ta dinga ba ta baki a kan ta yi haƙuri da maganar da ta yi mata, don da a ce ta san har haka ranta zai ɓaci da tun farko ba ta yi mata ba, cikin sanyin jiki Harin ta ciro kuɗi ta ajiye a gaban Bintoto sannan ta miƙe tana yi musu sallamar tafiya, cikin rashin sukuni suka rabu ko rakiya babu.

Hari ta fita zuciyarta cike da alhinin rabuwa da ƙawarta Habi mahaifiyar Bintoto, wadda suka taso tare tun suna 'yan yara, kafin mutuwa ta yi musu katangar ƙarfen da ta shata layi a tsakaninsu. Sannan Habin ita ce auta a wurin Kandala, kuma ita ce ɗiyar da ta fi so a cikin 'ya'yanta, garin haihuwar Bintoto Allah ya yi mata rasuwa, hakan ya sa ta damƙe Bintoto a hannunta ko ƙuda ba ta so ya taɓa ta.

Sannan kuma ta ɗauki son duniya ta ɗora a Bintoto, don ko shayar da ita da ƙyar ta bari 'yarta Jimmala ta shayar da ita, wadda ta zamo yaya ga mahaifiyar Bintoton, ana yaye ta ta karɓe ta ta dawo hannunta, tun daga lokacin hidimarta ta koma kanta, don a yadda take ji ko ubanta bai isa da ita ba ganin yadda take da matsayi a wurin ta. Dole ya zuba mata ido ya bar ta da ita, tsakaninsa da su ranar da ta ga damar kai masa ita ta ya gan ta, tun tana ƙarama har girmanta ya kawo kai.

Fitar Hari ya bai wa Kandala damar ƙyalla ido ta hango 'yan dubu-dubu da Harin ta ajiye mata a kan gefen tabarma, babu shiri ta share hawayenta ta kai wa kuɗin wawura, Bintoto ma ta yi saurin damƙe kuɗin da hannunta mai lafiya, saboda sanin idan suka shiga hannun Kandala babu rabonta. Ai kuwa Kandala ba ta yi ƙasa a gwiwa ba wajen ƙoƙarin ɓanɓare kuɗin a hannunta tana cije baki tana faɗin,

"Ai wallahi yau ƙwandala ba za ki ci a cikin kuɗin nan ba, tun da har kika jawo na yi asarar ƙudina a banza a wofi garin rashin mutuncin da kika saba."

Bintoto ta damƙe kuɗin iya ƙarfinta ita ma Kandala ba ta daina son ƙwace kuɗin ba, ganin ba za ta iya ɓanɓare kuɗin ba ta soka mata haƙorinta na gaba, wanda ya bindiro waje ko ta rufe bakin shi ba zai yiwu ya rufe ruf ba, babu shiri Bintoto ta saki kuɗin tana yarfa hannu tare da faɗin,

"Wayyo Kandala! Yanzu a kan kuɗi za ki huda mini hannu da haƙorinki mai wuƙa??"

Kandala tana haɗa kan kuɗin cikin sauri ta ce,

,"Ko mashi haƙorin nawa ya koma ba zan ji shayin soka miki shi ba a kan kuɗin nan, ballantana haƙorin da ko ko kaifi bai da shi amma kin kira shi da sunan wuƙa. To ba wuƙa ba ne zarto ne don malfar ubanki."

Bintoto tana ci gaba da yarfa hannun ta ɓata fuska ta ce,

"Ai da a ce zamanin yaƙi muke yanzu da wallahi ko shi zai yi jahadi wajen kashe miyagun arna, don tsaf zai iya komawa takobi ya kai sara ba tare da an tantance ba."

Wata muguwar dariya Kandala ta fashe da ita tare da buɗa gefen zanenta ta ƙulle ƙudin ta tsuke tsukut, sannan ta soke zanenta a jiki ta ɗauki mafefecin ta ci gaba da yi mata fifitar tana faɗin,

"Yanzu dai duk abin da za ki ce ki faɗa daidai kike. Ni dai kuɗi na haɗe musu kai na soke a jikina, idan kin isa ki tashi ki ƙwata mu gani."

Bintoto za ta yi magana kenan sai ga Kulu ta yi sallama ta shigo gidan, jiki a sanyaye ta nufo su gabanta yana faɗuwa, tana zuwa ta duƙa tana share hawayen ta ce,

"Inna, don Allah ki yi haƙuri wallahi ba da son raina na daki Bintoto ba. Tsautsayi ne da sharrin shaiɗan."

Kandala ta watsa mata wata muguwar harara sannan ta ce,

"Ai kuma tun da na riga da na sake ki to ki sani kin saku yarinya, abin da ya rage kawai ki kwashi tsommakaran haukarki ki koma gidanku, aure ya riga ya ƙare babu fashin barin gidan, ke da Mani haita-haita tun da kika dakar mini Bintoto. Don ko Mani ne ya yi mata abin da kika yi mata sai ya san ya aikata, ballantana ke 'yar karan kaɗa miya, ki zauna gidan naku ki ji idan da daɗi. Daga wannan karon Mani ya gama zama da ke, wallahi kin ji na rantse a kan Bintoto ban ƙi na tayar da garin nan ba."

Akafta😀

Na kuɗi ne. 1k kacal ku garzaya Telegram ku more karatunku babu jira. 1230094555 Access Bank Hadiza D Auta Ibrahim. Shaidar biya ta wannan layin: 08022014771.

D/AUTA ce✍

SHAGALALLIYA

HADIZA D. AUTA

LAMBA TA BIYAR

Kulu ta sake fashewa da kuka tana yi wa Kandala magiya a kan ta yi haƙuri ba za ta sake ba, amma hakan bai sa ta karya mata zuciya ba, ba illa ɗaga kai da ta yi sama tana kumbura hanci alamun magiyarta ko a jikinta. Ana cikin hakan sai ga Mani ya shigo ransa a ɓace saboda ya samu labarin Kandala ta kori kulun, takaici ya saka shi zuwa har gidansu ya roƙi iyayenta ta dawo ɗakinta. Saboda ya tabbatar musu shi bai saki matarsa ba, kuma yana son zama da ita.

Wannan dalilin ya sa ya ƙi biyo ta ya ce ta fara zuwa, ko da ya shigo gidan kallo ɗaya ya yi musu ya kawar da kai, don bai bi ta kansu ba ya nufi ɗakin Kulun kansa tsaye, Kandala ta bi shi da kallo cike da mamaki sannan ta ƙwala masa kira tana cewa,

"Ban gane ba Mani! Wai an yi yamma da kare, shin kana nufin ba za ka zo ka duba Bintoto a kan aika-aikar da matarka ta yi mata ba ne ko me kake nufi?"

Ba tare da ya juyo ba yana haɗe rai ya ce,

"Allah ya ba ta lafiya! Amma ni ban saki Kulu ba kada ta sake fita ko'ina ban amince b..."

Yana maganar ya shige ɗaki, Kandala ta riƙe baki tana juya zancensa a ranta, sannan ta ajiye mafefecin da ke hannunta ta miƙe jikinta yana rawa ta bi shi har ɗakin Kulun, labule ta ɗage ranta a ɓace ta ce masa,

"Kana nufin haushi na ka ji don na kori matarka?"

Mani bai ce da ita ƙanzil ba, hakan ya sa ta sake magana a harzuƙe, "To ai tun da ka ce ba ka sake ta ba to ta dawo ta zauna, amman ka sani babu hannuna babu ƙafata da lamarinku balllantana wani abu da zai shafe ku dukanku kai da ita! Kuma wallahil'azimi a kan Bintoto zan iya bar muku gidan nan sai ku cinye shi kai da ita! Tun da ka nuna ka fi son ta a kan ɗiyar ƙanwarka uwa ɗaya uba, kuma wadda ka saki nono ta kama."

Tana gama faɗar hakan ranta a ɓace ta saki labulen ta bar wurin, kai-tsaye ƙofarta ta nufa duk da magiyar da Kulun take yi ba ta kula ba, sai ma buta da ta ɗauka ta yi bayi saboda kiraye-kirayen sallar magaribar da aka fara yi a lokacin.

Amma har ta fito bayin ta gama arwalar ta shige ɗaki bakin Kulu bai yi shiru da ban haƙurin ba. Sai da ta fara sallah ita ma ta je ta yi arwallar ta yi nata ɗakin sum-

sum. Bintoto da ke kwance tana bin su da kallo ta bi ta da harara tare da murguɗa baki bayan ta yi ƙwafa a ranta ta ce,

'Munafuka! Ai ko haka aka bar ki kin sha wuya bak'ar muguwa, sai shegen baƙin ƙarfi tamkar wata zakanya, idan ban da Allah ya kawo Kandala da shi kenan sai ta ga na mutu za ta kyale ni...ai kuma wallahi sai kin sani don a kan kajinki zan huce haushina...ke duka ma sai na kashe su a gidan nan, ko kuma na yi ta jefa shegu a cikin masai suna mutuwa kowa ma ya huta.'

Gama zancen zucinta ke da wuya ta miƙe ta nufi wajen akurkin kajin Kulu ta jawo ɗiya biyu suna tsuwwa tsui-tsui, amma a haka ta je bayinsu cikin sauri ta jefa su masai, sannan ta rufe masan da murfi ta fito cike da jin daɗin ta yi ramuwar gayya.

Daren ranar suka yi kwanan takaici kowa da ƙuncin da ke damun shi, don Mani da dare sai da ya zo yana ta bai wa Kandala haƙuri amma ta ƙi kula shi, dole ya ƙyale ta ya koma wurin Kulu yana ƙara lurar da ita a kan yadda za ta zauna da Kandala da shalelenta ko don su samu zaman lafiya da su a huta da halinsu.

Haka rayuwa ta ci gaba da shurawa zaman lafiyar gidan ya yi ƙaranci, saboda kullum da sabon rikicin da Bintoto za ta jawo har ta sa a yi gagarumin faɗa a kansa.

Ana cikin hakan ne watarana ta ɗauki tallar goron da take yi idan ta ga dama, don sana'ar Kandala kenan siyar da goro da nono da man shanu, sai dai mafi akasari an fi zuwa gida a saye ba a cika fita zuwa tallar ba. Amma ranar da Bintoto ta yi sha'awar tallar don kanta tana ɗauka ta tafi yawon da ta saba yi da sunan tallar.

Hakan ta faru a ranar, Kandala ta lissafa mata goron a tire kowane da adadin kuɗinsa sannan ta rufe mata da wata raga mai riƙon ruwa. Wadda aka jiƙe sharkaf da ruwa don kada goron ya sha iska ya yi saurin bushewa.

Ta yi ɗana da tiren goron tana tafe tana wasa da wani zare a hannunta hankalinta gabaɗaya ya ɗauku a kan wasar da take yi. Babu zato ta ci karo da wani saurayi suka yi kiciɓis, Cikin tsautsayi kafin ta kamo tiren goronta tuni ya yi sama ya dawo ƙasa ya kife, kafin ta ankara ya watse ɗaiɗaya a cikin ƙasa.

A zabure ta ɗaga kanta cikin fushi ta yi magana tana zaro ido.

"Kan uban nan! Ai na rantse da Allah sai ka biya shi! Cabɗijam haka kawai ka sa na yi ɓari don ba ka da imani?"

Ɗan saurayin ya duƙa cikin rawar jiki ya fara tsince mata goron ɗaya bayan ɗaya yana sakawa a cikin tire har ya tsince duka, sannan ya ɗauko ragar ya saka mata a cikin tiren ya miƙe fuska babu yabo babu fallasa ya isa gabanta ya tsaya yana 'yar dariya ya ce,

"Don Allah ki yi haƙuri wallahi ba da gangan na yi b.."

Wani kalar kallo ta yi masa, tare da ƙura masa ido ƙur ko ƙiftawa babu riƙe da ƙugunta tana girgizar jiki, sosai ta so saka shi dariya, amma dole ya ƙumshe dariyar da ta so kufce masa saboda gudun ya ƙara tunzura ta. Ya koma gyara goron a cikin tire kamar wanda aka saka sai ya mayar da shi yadda yake. Sai da ta gaji da hararar sannan ta ja baya tana ce masa,

"Ai na rantse da Allah kuɗin gorona za ka ba ni gabaɗaya, na riga na sayar maka! Don haka ka biya ni kawai ka juye goronka sauri nake yi. Amma ka sani guda ɗaya ba zan karɓa ba don ni na sayar maka da shi duka kawai ka ba ni kuɗina na koma gida."

Ganin idan ya biye ta za ta iya tara masa mutane, hakan ya saka shi tambayar ta kuɗin goron. Sai da ta karkace kai gefe sannan ta zaftaro kuɗin da ya saka shi zaro ido yana ƙare wa goron kallo, saboda ta ce atafau ita goronta na dubu ɗaya ne, bayan kwata-kwata goron ko ɗari biyar bai kai ba. Saboda wani ma gyaran tsutsa ne wanda bai wuce ashirin naira hamsin ba, amma saboda a zauna lafiya haka ya saka hannu a aljihu ya ciro ɗari biyu guda biyu huɗu ya miƙa mata. Sai da ta kalli kuɗin sannan ta maka masa harara tana ci gaba da girgizar jiki kamar wata babbar budurwa ta ce masa,

"Ai wallahi tun da ba tsohuwa nake ba ni ko ba zan karɓi tsofaffin kuɗi ba! Haka kawai don mugunta ga sababbi nan ina gani ka ba ni su, shi ne za ka haɗa ni da waɗanda kafin na je gida sun yage? To ni kuma wallahi ba zan karɓe su ba ahe!"

Ta ƙare maganar tare da murguɗa masa baki tare da juya kai gefe, ba ƙaramar dariya ta so ba shi ba, amman ya dake ya nuna mata ko kaɗan bai ji haushi ba. Ya mayar da kuɗin ya ɗauko mata sababbin da take so ya miƙa mata, jikinta yana rawa ta fisge kuɗin sannan ta sake cewa,

"Allah Ya taimake ka ka biya da sai na yi maka dukan billahillazi, kuma ina zan juye maka goron ni sauri nake yi?"

Sai da ya mayar da sauran kuɗin a aljihunsa sannan ya ce mata ta je duka ya ba ta.

Bintoto ta zaro ido waje cike da jin daɗi da mamaki a kan fuskarta ta ce,

"Da gaske?"

Yana murmushi ya ce, "Da gaske mana, amman da sharaɗin duk lokacin da na zo gidanku za ki fito mu yi hira."

Bintoto tana dariya baki a washe ta ce masa, "Ai idan har za ka ƙara ba ni irin waɗannan kuɗin sababbi dole zan fito kai ma ka sani, don haka ka zo kawai."

Ya juya yana 'yar dariya ya fara tafiya, ta bi shi da kallo kafin ta ɗaga murya tana cewa,

."Don Allah ta wace hanya za ka bi gobe?"

Babu shiri ya waigo cike da mamaki ya jefo mata tambayar "Lafiya?"

Tana wasar baki ta ce, "So nake yi ka sake zubar da goron, ai na san za ka saya ko?"

Bakinsa ya dafe saboda dariyar da ta suɓuce masa, amma a haka ya ba ta amsa da cewa,

"Ki biyo ta nan za mu sake wani karon kamar yau. Amman fa a goben ko kin zubar da goronki ba zan biya ko ficika ba."

Bintoto ta murguɗa masa baki da hararar gefen ido ta ce,

"To na ji, shi kenan ta fi kawai."

Ya juya yana dariyar shirmenta, saboda sai da ta sake ɗaga murya ta jefo masa tambayar, "Amma dai kai ba ɗan garin nan ba ne ko?"

Ba tare da ya juyo ba ya ce mata "E, baƙunta na zo."

Ta bi bayansa da harara sannan ta ɗora tirenta a kai tana haɗa kuɗin wuri ɗaya tana cewa ,

"Ai dai na yi maka wayo, kuma duk ka kuskura muka sake haɗuwa gobe ma sai ka zubar, kuma dole sai ka sayi goron ka bayar da kuɗin sababbi. Baƙin mugu kana da kuɗi da yawa a aljhunka amma ka ce ba za ka biya ba don kada na ƙaru da kai. Hu'umm! ai yasin ba ka isa ba ma duk muka sake haɗuwa dole ma sai ka sake saya tun da wawa ne kai ba ka da wani wayo."

Haka ta yi ta sambatunta ita kaɗai kamar a gabansa take yi, sannan ta je wani gida ta wanke goron ta sake jera shi a tire yadda yake tun farko, sannan ta yi wurin tallar a ranta tana cewa,

"Ina ma na samu wani hamagon da zai sake zubar da goron ya biya ni. Yasin da gangan zan kifa wa mutum tiren na ƙwale masa kai kuma ya biya ni kuɗin gorona."

Ku ci gaba da biyo ni don wannan duka shimfiɗa ce a cikin littafin SHAGALALLIYA😊 1k ne kuɗin, za ku same shi a Telegram ba tare da kun yi jira ba. A WhatsApp ma ga mai buƙata PC saboda gudun hayaniya zai iya zuwa mu yi tsada. 1230094555 Access Bank Hadiza D Auta. Lambar waya don turo shaidar biya ko wani ƙarin bayani: 08022014771.

Akafta.

SHAGALALLIYA!

HADIZA D. AUTA

LAMBA SHIDA.

Ko da ta tafi tallar ko rabin goron ba ta sayar ba ta dawo gida, saboda ganin ana faɗa ta kasa ta tsare, har sai da aka gama faɗan kaf aka watse, tana ɗauke da tiren goronta a kai tana dariyar jin daɗi da mugunta. Cikin nishaɗi ta nufi gida tana ƙyalƙyala dariya a duk lokacin da ta tuno yadda aka ɗauki Innar Jamila sama aka kayar, sannan aka turmushe kanta cikin ƙasa tana tusoshin wahala.

Da dariya ta faɗa gidan ba tare da ta yi sallama ba, babu shiri dariyar ta tsaya mata cak a sanadin hango kajin Kulu a ƙofar ɗakin Kandala, suna ta caccakar wani abu a cikin kwano. Wanda ba ta raba ɗaya biyu a kan cewa nata ne aka ajiye mata, amma tsabar sun samu sake sukae yin watanda yadda suke so. Haushi ya sa ta yi mugun tsalle tare da kai musu shuri da ƙafa a cikin a rashin sa'a, babu zato sai ga tangal ta faɗi ƙasa warwas riƙe da tiren goronta gam-gam gudun ya zube, amman hakan bai hana goron yin tsalle ya watse ƙasa ba, cikin tsananin takaici ta yi magana a ƙufule tana cewa,

"Kan Uba! Ai wallahi yau sai kun san kun ci mini garin kwaki!"

Tiren ta fara ajiyewa sannan ta miƙe tsaye, cikin zafin nama ta damƙo mafefecin Kandala ta yi cikinsu da duka idonta rufe, a nan ta ci nasarar buge wani ɗan kaza ya faɗi yana shure-shuren mutuwa. Hakan ya yi dai dai da fitowar Kulu daga ɗakinta za ta ajiye kwanon da ta gama cin abinci, aguje ta saki kwanon ta yi kan ɗan kazarta da ke gangar mutuwa tana faɗin,

"Na shiga uku! Me kika yi masa Bintoto?"

Tana zuwa ɗan kazar yana daina motsi alamun ya mutu, cikin ɓacin rai ta ɗago fuskarta a cure ta ce mata,

"Wallahi ki ji tsoron Allah! Don idan kina zaton ni kike yi wa to kanki kike ɗaukar wa kaya, saboda duk zaluncin da kika yi musu ranar lahira sai Allah ya fitar da haƙƙinsu a kanki."

Ta ƙare maganar cikin matsanancin ɓacin rai da mugun jin haushin ta a ranta, don a yadda ta ji a lokacin idan ban da ta san taɓa ta zai jawo mata wani ɓacin ran da yafi mutuwar ɗan kazar; da ta saki jiki ta jibge ta iya son ranta. Amma dole ta ƙyale ta ta juya ta bar wajen cikin ƙunar rai saboda babu halin ɗaukar mataki. Bintoto kam kallo ta bi bayanta da shi tana murguɗa baki cikin tsiwa ta ce,

"Wa ya ce su je su ci mini garin kwaki? Ke yanzu ba ga shi kin ci naki ba har kin fito da kwano! Amma ni kike tura wa kaji su cinye nawa don baƙar mugunta da zalunc..to wallahi ko gobe suka taɓa mini abinci sai na lakaɗa musu ɗan banzan dukan da ya fi wannan!"

Kulu dai ƙanzil ba ta ce mata ba, ganin hakan ya sa Bintoton barin wajen tana harare-harare ta fara kwashe goron da ya zube, sannan ta kai tiren ta ajiye ta zauna tana gungunin faɗin,

"Ai na rantse da Allah ni ba zan ci garin kwakin nan ba, sai dai idan sayo wani zan yi na sha da sikari...haka kawai su je su ci kashi su dawo su saka mini baki a gari kuma ni na zo na ci? Tab! Lalle ma tun da an mayar da ni wawuya so dole na ci, uhum!"

Bayan ta gama surutan nata ta miƙe kamar wata kububuwa tana kumbure-kumburen fuska ta fice gidan. Wani garin ta siyo a cikin kuɗin goron da aka biya ta, har da sikari da ƙuliƙuli ta shigo gidan da 'yar waƙarta alamun jin daɗi. Ƙirjinta ya buga dam babu shiri ta yi turus saboda hango Kandala zaune saman tabarma a bakin ɗakinta, ta buɗe ƙafafuwa tana lissafin kuɗi. Cikin sauri ta ƙarasa tana faɗin,

"Kandala ina kika samo waɗannan kuɗaɗen haka?"

Kandala tana ta lissafinta ba ta tanka mata ba har sai da ta gama sannan ta ɗaga kai ta ce mata,

"Wurin Mandiya na je na karɓo kuɗin adashena, kin ga yanzu sai na je na sayo miki turmin atamfarki ta sallah a kai miki ɗinki, sauran kuɗin kuma zan ƙaro miki kwanoni na adana saboda aurenki, don kina samun miji zan aurar da ke na huta da halinki, saboda a kullum burina bai wuce na ga an kai ki ɗakin mijinki ba ke ma ki yi aure kamar yadda kowa yake yi."

Bintoto ta ɓata fuska tare da kwanciya kan cinyarta cikin sanyin jiki tana cewa,

"Ni dai Kandala wallahi ba na son aure yanzu, sai na tara kuɗin zuwa Saudiyya. Saboda ke ma kin sani mazan garin nan babu wanda zai iya kai ni Makka, ko ke ba ki so na je aikin hajji na sayo miki ɗankwali mai walƙiya?"

Kandala ta dungure mata kai daga kwancen cike da jin haushi ta ce,

"To sannu ɗanwake ka fi ubanka! Baƙin lissafin naki kenan da kika saba, idan ba ɗora wa kai wahala ba a garin nan namu duka mutum nawa ne suka aikin Hajji? Da har kike wannan dogon burin da ko'ina ba zai je da ke ba, ko an ce miki zuwa Makka wasa ne da har za ki je da kuɗin sata?"

Bintoto ta yi saurin tashi zaune tare da turo baki tana kallon ta ta ce,

"Sata kuma! Ni nake yin satar?"

"Kwarai ko!"

Kandala ta faɗa tana gutsura goro tare da kawar da kanta gefe, cikin muryar kuka Bintoto ta ce, "Wallahi Allah ni idan ban da sau ɗaya ban taɓa ɗaukar miki kuɗi ba, kuma Allah ma ya sani idan ba sau guda ba ne wutar saƙara da lazza ta ƙona ni!"

Kandala ta yi mata wani kallo tare da dungure mata kai sannan ta ce,

"Wai ke halan kin ɗauka ba na jin ki idan ina barci kina lalubar gefen zanina inda nake ƙulle kuɗina? To ina ganin ki idan kin ga zan tashi ki yi sauri ki saki, don haka kar nake kallon ki kada ki zaci kwanan gaske nake yi idona biyu yarinya."

Bintoto ta yi tsuru-tsuru da ido sannan ta ce, "Yanzu dai kina nufin ɓarauniya ce ni ko?"

Ta ƙare maganar cikin kuka, Kandala ta jawo ta jikinta cikin sigar rarrashi tana faɗin,

"Ke kam me ya sa ba ki san wasa ba? To wasa nake yi miki ai, don ni ban taɓa kama ki kina kwance ƙullin kuɗina ba ko sau ɗaya ma. Don ke ma kin sani a garin nan kaf babu wanda ya isa ya kira ki da ɓarauniya na ƙyale shi ballantana ni na faɗi hakan.. share hawayenki Allah ma ya kiyaye wannan rana."

Bintoto ta janye jikinta daga nata ta miƙe tana kumbura hanci ta jiƙo garin ta yi nesa da Kandala ta zauna tana sha tana zunburar baki alamun ta yi fushi.

Kandala kam har cikin ranta ba ta ji dad'in yadda ta ɓata mata rai ba, shi ya sa ta koma faɗin,

"Ina kuɗin gorona da kika sayar?"

Bintoto ta cire ɗankwalinta inda ta ƙulle kuɗin ta ciro su duka ta ajiye gefenta ba tare da ta ce komi ba ta ci gaba da shan garin kwakin, Kandala ta miƙe ta zo ta ɗauki kuɗin tana lissafawa, ganin ɗari shida sababbi kar ta zaro ido waje tana cewa,

"Ko kin sake komawa tallar bayan wadda na ɗora miki a farko?"

Bintoto ta yi mata kallon gefen ido sannan ta ce,

"Sauran kuɗina ne, ki cire kuɗinki da nake sata a ciki ki bani saura zan saka a asusuna."

Kandala ta zauna kusa da ita tana wasar baki ta ce,

"Daɗina da ke saurin ƙufula, yanzu wannan ɗan abin har ya kai ki yi ta fushi da ni Bintoto? To kwantar da hankalinki daga yanzu kullum na yi sallah zan yi miki addu'ar Allah ya ba ki miji mai kuɗin da zai kai ki Makka ki yi aikin hajji."

Babu shiri Bintoto ta yi saurin washe baki saboda jin daɗin maganar ta ce, "Ai ko wallahi da sai na sa an bugo miki akwatin zinari ki dinga saka tufafinki ki daina saka su cikin fanteka. Saboda ɓeraye su bar shiga suna yi miki kashi a cikin kaya."

Kandala ta yi dariya sannan ta ce "Ni dai ki bar akwatin zinarin, haƙorin azurfa nake so ki sayo mini na saka wa haƙorin nan nawa, kin ga ni ma sai na zamo Hajiya Kandala kamar ke."

Bintoto ta fashe da dariya har da riƙe ciki sannan ta ce,

"To ai ke Kandala haƙorinki irin na giwaye ne, ta ya za a samu haƙorin Makkar da zai yi masa daidai a duniyar nan?"

Kandala ta kai mata dundu a baya ta goce tana dariya ta ce, "Ke dai ki yi ta addu'ar idan na auri miji mai kuɗi na sa a cire shi a saka miki na ƙarfe wanda idan kin so za ki iya cirewa ki ci abinci da shi kamar cokali."

Kandala ta miƙe tana dariya ta ce,

"Bari dai na je na ɓoye kuɗina tun kafin Mani ya zo ya gan su ya saka ransa a banza, ga shi kuma ba ba shi zan yi ba tunda har ya nuna matarsa ta fi mu ni da ke, don haka idan dai Kulu ce ga ta nan ga shi, saboda ko kajinta aka bar shi da su sun ishe shi wahala, ballantana mugun halinta na zalunci da munafurci."

Bintoto ta kai cokalin gari a bakinta, wanda sai da ta ciko shi fam har ya yi tozo, sannan ta haɗiye da ƙyar tana cewa,

"Ai Kandala da ma kin ce ta mayar da su gidansu mu huta da su, kin ga ma garin da kika bar mini ko? To ko da na dawo duk sun ci rabi sun shige cikin kwanon suna ta wawaso."

Kandala ta yi ƙwafa cikin ƙarin jin haushi ta ce, "Sai ba ita ba! kaɗan daga cikin aikinta kenan baƙar muguwa, ai da kin karya 'yanbanza ma a huta."

Bintoto ta yi saurin faɗin, "Ai wallahi sai da na kashe mata ɗan kaza ɗaya yau, don ko gobe ma suka sake ci mini abinci ni ma sai na sake kashe mata wasu, kuma haka zan yi ta yi har sai sun mutu duka mun huta, tun da ita ba za ta iya ɗaure su ba."

Kandala cikin sanyin jiki ta ce

"Ke ko ki daina kashe su, amma ni na ce duk suka sake ci miki abinci ki ɗauki kare ki yi musu dukan tsiya."

Bintoto ta fashe da wata arniyar dariya sannan ta ce, "To kuma idan suka mace fa bayan kuma kin ce na daina kashewa?"

Kandala za ta yi magana kenan ta jiyo muryar Mani a soro zai shigo gidan, ta yi saurin tashi jikinta yana rawa ta faɗa ɗaki har da cin tuntuɓe saura ƙiris ta faɗi tsabar sauri. Bintoto ta yi tsalle ta faɗi kwance tana dariyar ƙeta har lokacin da Mani ya shigo zai wuce, cikin ɗaga murya da tsokana ta ce da shi,

"Kawu Mani ga Kandala can cikin ɗaki tana neman ka."

1230094555 Access Bank Hadiza D Auta Ibrahim. Don ƙarin bayani a taɓo wannan lambar: 08022014771.

Akafta😊

D. AUTA CE✍

SHAGALALLIYA

HADIZA D. AUTA

LAMBA BAKWAI.

Sai da Mani ya bi ta da harara har da ƙwafa sannan ya nufi ƙofar ɗakin Kandala, wadda ke cikin ɗaki tana ƙoƙarin yi wa kuɗin mugun ɓoyo. Da sauri ta fito bayan ta adana ta tsaya bakin ƙofar ɗakin tana faɗin,

"Lafiya na gan ka a nan?"

"Bintoto ta ce kina nema n..."

"Kul...Kulu ce take neman ka tun ɗazu, ka yi tafi ka ji wataƙila kazar da ta dafa take son ba ka."

Mani ya yi tsaye yana ƙumshe dariya, saboda ya gama gano akwai abin da take ɓoyewa wanda ba ta son ya gani, cikin dariya ya fara ƙoƙarin kutsa kansa da niyyar shiga ɗakin yana cewa,

"Akwai fura a ɗakin nan na sha?"

Kandala ta tare ƙofar tana faɗin,

"Je wurin matarka yanzu ta gama dama ta da zafinta."

Mani ya juya yana dariya ya ce,

"Bari dai na je na dawo Inna, wallahi yau aljihuna ƙaf nake ko kuɗin sayen dawar da za a yi tuwo babu a gidan nan."

Kandala ta bi shi da harara sannan ta ce, "Aikin kenan ba ni-ba ni kullum kai ba ka iya wani motsin arziƙi sai na zillo da dogon wuyan a ba ka a ba ka. Sarkin maroƙan duniya ma dole ya shafa maka lafiya a wajen son banza. Wallahi dai ka san ciwon kanka tun kafin lokaci ya ƙure maka, saboda watarana ake wa gudu idan ƙasa ta shafe idona. Don haka tun yanzu ka yi ta kuka tun da kai ba ka san yadda ake juya kwabo ya koma sisi ba."

Dariya kawai Mani ya dinga yi yana sosa kai, ba tare da ya juyo ba ya nufi ɗakin Kulu don ya saba da gorinta a duk lokacin da ya nemi wani abu daga hannunta. Kuma a haka yake shanye duk abin da za ta faɗa masa matuƙar za ta ba shi abin da ya nema. Saboda zuciyarsa a mace take da kallon abin da take da shi da abin da ta samu, shi ya sa yake zaman kashe wando a majalisin hira cikin abokansa masu zaman banza, ba su da aiki sai yi da mutane wane ya samu kaza wane kaza ya rasa.

Kandala ta gama faɗanta da Mani ta juyo kan Bintoto da ke ta ƙumshe dariya, don ta san ta gama tsokano fushin Kandala dole ta kama kanta ko kuma ta saka ta ɗaki ta rufe sai ta yi kuka ta gama jigata sannan ta fito da ita, don da wuya ta dake ta gudun ta illata ta, saboda ba ta iya dukan yaro ba idan ranta ya ɓace sai ta ji masa rauni take jin sanyi.

Cikin ƙufula ta ce mata,

"Idan ma ɓakin surutunki ya jawo ya karbi kuɗin to kin yi wa kanki asarar ɗinkin sallah, kina ji kina gani kowa zai fito da sababbi kayan sallah ban da ke, tun da ke ba a rufin asiri da ke sai kin tona mutane, to ki je ki ce ya zo ga kuɗin ya ƙwata tun da uban wani ya nema mini su! Wallahi ki kiyaye ni ko a cikin kwanan nan na mayar da ke gidan ubanki na huta da halinki."

Tana gama faɗar hakan ta janyo ɗakinta ta rufe da kwaɗo ta fice gidan, Bintoto ta bi ta da wani kallo tana zunɓurar baki wai ita ta ji haushin an zagi Babanta. Ta haɗa kai da gwiwa tana ta mui-mui da baki tana gungunin faɗar duk abin da ya zo bakinta da harare-harare. Daga nan ta ɓingire tana ta barci saboda garin kwakin da ta sha ya saka ta jin daɗin yanayin har da minshari, sai dai ko'ina barcin nata bai je ba ta ji kaji a saman jikinta suna tsuwa.

"Tsui! Tsui! Tsui."

A firgice ta farka tare da kaiwa uwar kajin da ke kusa da ita wani uban duka, a bisa tsautsayi kazar ta zille ita ta naushi ƙasa. Babu shiri ta fasa ƙara saboda hannun da Kulu ta ji mata ciwo ne, Mani da ke fitowa daga ɗakin Kulun ya nufo ta cikin sauri yana tambayar,

"Lafiya? Me aka yi miki kuma yanzu?"

Bintoto ta miƙe tsaye tana kuka riƙe da hannu ta fice gidan ko kallon shi ba ta tsaya yi ba, haushi ya saka shi kai kallonsa ga ƙofar ɗakin Kandala, ganin shi a rufe ya fice yana 'yar dariya don ya san a kansa ta rufe ɗakin ta fice, don ma kada ya fito ya same ta idan ya yi mata magiya ta ba shi kuɗin da ya nema.

Minti goma sha biyar da fitar Bintoto sai ga muryar Kandala tana ta surfa ruwan bala'i da tsine-tsine, tana shiga ba ta zame ko'ina ba sai wurin kara, ta ciro wani ƙaton karen dawa mai bala'in ƙwari ta bi 'yan kajin Kulu da gudu tana duka. Kulu da ke ɗaki ta fito saboda jin kukan kajinta, ganin Kandala da gudu tana dukan kajin ya sa ta sha jinin jikinta, don ta gama gano sun jawo mata wata sabuwar fitinar da take gudu. A ckin rashin sa'a Kandala ta bi uwar kajin da gudu tana duka, sai ga ta da cin tuntuɓe da ƙatuwar tukunyar ƙarfen Kulu, wadda ke cike taf da ƙasari babu zato ta

faɗi tim a ƙasa Sannan ƙasarin duka ya fantsama jikinta ya yi mata wanka. Kandala ta fasa wata arniyar ƙara dafe da ƙugunta tana faɗin,

"Wayyo ni Allah wayyo ni kaina! Ke kam Allah ya tsine miki Kulu daga ke har 'yan kajinki, wallahi yau-yau sai sun bar gidan nan ko kuma ke ki bar shi tun da ba gidan Isuhu mai mola ba ne!"

Kulu ta fito daga inda ta rakuɓe ƙirjinta yana bugawa, ganin irin faɗuwar da Kandala ta yi mai haɗe da mugun walle, cikin rawar jiki ta isa wurin tana ƙoƙarin ɗaga ta sama da niyyar taimaka mata ta miƙe, amma babu kunya Kandala ta saka ƙafa ta kai mata harbi a gefen fuskarta, babu zato Kulu ta faɗi daɓas saboda tsabar tsoron Kandalar ya shige ta ganin abubuwan da ke ta faruwa duk a sanadinta.

Da rarrafe Kandala ta miƙe da ƙyar tana faɗin wayyo, dafe da ƙugunta tana jan ƙafafu da jan numfashi ta koma faɗin,

"Dole na koma wurin Ɗantani mai gyaran karaya ni ma ya duba mini ƙuguna, wallahi Mani ka ci amanata da ka auro Kulu ka kawo mana ita a cikin gidan nan! Ke kam Kulu Allah ya wadaranki ya tsine miki albarkar dare da ta safiya. Wallahi na faɗa da babbar murya Kulu ban yafe miki ba! Saboda kin zamo mana fitina ke da tsinannun kajinki, marasa mutunci da rashin imani, kuma 'yan ƙasan wutar jahannama da ta hawiya!"

To fa! A taushi ƙugun Kandala kafin ta kasa tafiya mu shiga uku😂

1230094555 Access Bank Hadiza D. Auta Ibrahim. Shaidar biya ta wannan lambar; 08022014771.

SHAGALALLIYA!

HADIZA D. AUTA

LAMBA TAKWAS.

A haka ta fice gidan tana ɗangishi tare da ƙara tsine wa Kulu da kajin nata. Kulu kam duk da take cikin tsoron abin da zai je ya dawo hakan bai hana ta fito da dariyar da take faman ƙumshewa ba. Musamman idan ta tuno da irin faɗuwar da Kandala ta yi mai haɗe da walle, sannan da kalar harbin da ta kai mata da ƙafa har ta faɗi kamar wata 'yar wresteling. Tuno abin da ke gabanta ya sa ta ta samo buhu cikin sauri ta dinga kama ɗiyan kajin tana sakawa, sannan ta kamo uwarsu ta damƙe a hannu da sassarfa ta fice gidan zuwa gidansu. Da nufin koma can sa zama don ita ma ta gaji da fitina tana so ta huta, saboda masifar da suke jawo mata koyaushe rigima ta tashi cikin gidan a kansu ne ake yi.

Ko da Kandala da Bintoto suka dawo gidan ba ta dawo ba, don da tsaya bayar da labarin fitintinun da kajin suke ja mata. Bintoto ɗauke da hannu Kandala dafe da ƙugu, a haka suka nemi wurin zama kowa da kalar zogin da yake ji .

Zamansu ke da wuya Kulu ta dawo gidan kai-tsaye wajensu ta nufo da nufin yi masu sannu, sannan ta ba da haƙuri duk da ta san ba lalle ne Kangala ta yafe mata ba kamar yadda ta furta. Hakan ya sa tun kafin ta ƙarasa inda suke Bintoto ta fasa wata uwar ƙara tana cewa,

"Kandala ki hana ta zuwa wurin nan wallahi ba na son ganin ta!"

Kandala ta yi saurin kallon Kulu da jar harara tana faɗin, "Kul kada ki ƙaraso wajen nan! Baƙar azzaluma! Ki tafi kawai mun bar ki da Allah, idan muka je lahira a yi mana hisabi da ke a gaban bainar jama'u!"

Kulu ta marairece fuska tana faɗin,

"Don Allah Inna ku yi haƙuri, yanzu haka ma na kwashe kajin gabaɗaya na kai su gidanmu, saboda ni ma ba da son raina suke yin abin da suke yi b.."

Kandala ta buga wani uban tsakin da ya saka Kulu dire maganarta babu shiri, saboda ganin yadda take jujjuya baki tana mayar da shi gefe kafin ta ce,

"Ke dai kawai ki ce watan mutuwarsu ne ya kama, don ko tantama babu yunwa ce za ta yi ajalinsu a gidan naku, tun da ko su masu gidan neman abin da za su ci suke yi, ballantana a samu na bai wa tsinannun kajin."

Cike da bala'in jin haushin Kandala a kan cin zarafin da take yi wa gidansu koyaushe babu alkunya, Kulu ta miƙe tana ɓata fuska cikin gunguni ta ce,

"Ai duk tsiyarmu ba za mu rasa geron da za a watsa musu ba."

Tana maganar tana tafiya Kandala ta bi ta da ƙatuwar harara tana cewa,

"Dawo ki ci gaba da zagin nawa da kika saba tabbatacciya! Ai daman can ina sane da kalolin zagin da kike shigewa ɗaki kina yi mini, to billahillazi muddin kika ci namana a bayan idona kaf zuri'arku sai Allah ya ci banten ubanku! Tun daga kan Ɗan'azumi har zuwa kan Isuhu mola mai hular gado."

Takaicin cin mutuncin da Kandala take yi wa kakanta da Babanta, ya sa ta isa ɗakinta da gudu tana kuka. Bintoto ta fashe da dariya iya ƙarfinta tana faɗin,

"Ai wallahi da ma kin yi kukan jini kin huta, idan jinin ya tsiyaye ki mutu ki bar mana gidan mu wataya mu kaɗai yadda muke so, shikenan mun mun rabu da gaibu!"

Kandala ta buge mata ƙeyar kai cikin sauri ta zuƙe jikinta tana ci gaba da dariyarta, Kandala cikin haɗe fuska ta ce mata,

"Idan ba ki daina tsokanar ta ba kika jawo ta dake ki babu ruwana don ma ki sani tun yanzu. Ni ba na goyon bayan rashin gaskiya, don haka ki bar mu mu ji da iftila'in da ta jaza mana kafin ita ma tsinuwar Allah ta hau kanta."

Sai da Bintoto ta turo baki sannan ta ce, "To Wallahi ni ko ranar da kika ga ta kayar da ni don ban shirya wa damben ba ne, amma yanzu ko da ciwon hannun nan nawa zan iya tumurmushe ta, na yi ta jibgar ta idan ta sake taɓa ni."

Kandala tana kallon ta tana juye baki gefe ta maka mata tana faɗin, "Kurin banza! Ranar ma da ta so kashe ki ai da lafiyarki amma kika saki baki ta dake ki a banza, ballantana yanzu da kika zama musaka hannu yana shirin shanyewa."

Haushin maganganun Kandala ta sa Bintoto ta rungume hannunta mai lafiya ta soke kanta cikin hannun tana gunguni, tare dasharar ƙwalla. Fahimtar ta yi fushi Kandala ta ko ma jan ta zuwa jikinta duk da zamewar da take yi, cikin sigar rarrashi ta shafo kanta tana cewa,

"Ke fa ba ki san wasa ba, to ni wasa ce nake yi miki, ai na san ko ranar don ba ki shirya ba ne shi ya sa ta lungude ki son ranta, amma tabbas da kin shirya da ta sha baƙin mamaki a kan irin ƙarfinki na zaki wanda kike kashe mutane da shi a cikin mafark.... ai kin tuna shi ko?"

A nan Bintoto ta ɗago kai tana washe baki saboda tuno mugun faɗan da ta yi da wasu mutane a cikin mafarki duk ta kashe su. Hakan ya sa ta zabura daga zaunen tana kallon Kandala ta ce,

"Wallahi fa har da wuƙaƙe na yi faɗan Kandala, kuma na yi ta soke mutane ina kashe su suna faɗuwa ƙasa suna mutuwa. To kamar haka nan zan yi wa Kulu a cikin mafarkin ko da safiya za ta yi sai dai a gan ta matacciya."

Kandala ta gimtse dariyarta tana cewa, "To wai su mutanen da kike kashewa a cikin mafarkim Musulmai ne ko Kafurai?"

Bintoto ta yi saurin faɗin, "Ohon musu! Ni dai ko su waye na yi ta kashe su yasin babu abin da ya dame ni tun da suka zo kama ni. Na san su ma idan suka samu sa'a kashe ni za su yi."

Kandala tana dariya ta ce, "Gara dai mu ji idan kafurai ne, saboda muddin aka ce Musulmai ne da kaina zan kai ki kotun Musulunci a yanke miki hukunci irin na masu kisan kai a cikin mafarki, tun kafin kisan naki ya zo kan Kulu ki ja mana bakin mutane."

Bintoto ta ƙyalƙyale da dariya Kandala ma tana taya ta, haka suka ci gaba hirarsu mai cike da shagala tare da barkwancinsu da suka saba yi a tsakaninsu koyaushe.

***

Watanni a tsakanin da rigimar kajin Bintoto ta ji sauƙi, saboda hannun nata yana samun kulawa hakan ya sa ta yi saurin warkewa, sai ɗan abin da ba a rasa ba, wani lokaci ma har tallar goro tana fita. Kandala kuma kwana biyu ne ta yi da ƙugun ya koma daidai. Da ma can buguwa ce kawai babu abin da ya same ta.

Kamar koyaushe, Bintoto tana ɗauke da tiren tallarta tare da ƙawarta Jamila, wadda ita ma tiren tallar ne a kanta za su je cin kasuwar garinsu, suna ta hirarsu a kan hanya. Babu zato suka hango wata dalleliyar mota ta nufo hanyar da suke kai, cike da ƙauyanci suka bi motar da kallo baki a sake har da tsayawa gefen hanya idonsu a kan motar har ta wuce.

A hankali motar ta fara rage gudu tana dawowa baya har ta ƙaraso inda suke tsaye ta tsaya, mamaki cike da fuskokinsu har zuwa lokacin da suka ga mai motar ya zuge gilashin motar tare da leƙo kansa yana faɗin,

"Sannun ku 'yanmata, don Allah ta wace hanya zan bi na je gidan Hakimi?"

Ƙawar Bintoto ta fara yi masa nuni da hannu Bintoto ta yi saurin tsamuke ta a cinya da ƙarfi tana yi mata signal a kan ta yi shiru, sannan bakinta yana rawa ta ce da shi,

"Bari mu zo mu nuna maka hanyar don daga nan akwai tazara sosai da gidan, kwatancen zai yi maka wahalar ganewa. Buɗe mana motar mu shiga sai mu kai ka har gidan da kanmu."

Kasancewarsa babban mutum, kai-tsaye ya gano motar take so su shiga shi ya sa ta tsiro da wayon, yana 'yar dariya ya buɗe musu motar jikin Bintoto yana rawa ta afka ciki, garin rawar jiki sannan da rashin iya shiga motar kafarta da takalmi ta fara ɗorawa ta yi tsalle ta faɗa da ƙarfi, har tiren goron ya buge mata goshi, babu shiri ta kai hannunta saman goshin tana shafawa tana faɗin,

"Wash! Allahna!"

Sannan ta yi saurin gyara zamanta tana leƙo da kanta ta kalli Jamila da ke tsaye tana kallon ta gabaɗaya ta gama tsorata, saboda tana jin fargabar ta shiga a yanke mata kai kamar yadda ta ji labarin ana yi a birni, Bintoto ta maka mata harara tana cewa,

"Ke dallah ki shigo mu je mu nuna masa gidan! Kin ga sauri yake yi kada mu ɓata masa lokaci."

Jamila ta fara ja da baya tana girgiza kai alamun tsoro, cike da jin haushin ta Bintoton ta sake magana a harzuƙe,

"Idan fa ba za ki shigo ba mu tafiya za mu yi wallahi!"

Cikin ɗari-ɗari Jamila ta shiga motar da ƙyar jikinta yana rawa saboda ita ma ba ta iya shiga motar ba, mutumin ya fito ya rufe musu ƙofa sannan ya koma mazauninsa ya tayar da motar, har ya yi gaba Bintoto ta yi saurin cewa,

"Ba ta nan ake bi ba! Juya baya akwai hanya mai sauƙi ta can inda ka fito."

Mutumin cikin aminta da zancenta ya yi ribas ya koma baya har suka ɓulle hanyar, cike da jin daɗi Bintoto ta sake nuna masa wata hanya tana cewa,

"Yawwa bi ta nan!"

Mutumin ya bi inda ta ce, suna tafe tana nuna masa hanyoyin da zai bi kamar haka;

"Miƙe wannan hanyar, yawwa sha kwana, miƙe sha waccan kwanar, ƙara miƙewa sha kwanar, yawwa bi ta nan..."

Haka ta dinga yi masa kwatance Jamila tana kallon ta cike da mamaki da fargaba har aka kai su kasuwa, cikin sauri Bintoto ta kama abin buɗewa cike da sa'a tana jawo shi ta buɗe ƙofar, jikinta yana rawa ta fito cikin sauri tana ƙumshe dariya ta kalli Jamila da ke zaune duk ta gama tsurewa ta ce da ita,

"To ai sai ki fito Malama!"

Ta fito da ƙyar sannan Bintoto ta rufe masa ƙofarsa da karfin gaske har sai da ya kai kallonsa a kan murfin. Sannan ta zo ta gefensa tana ƙumshe dariya ta ce,

"Yawwa mun gode Alhaji! Allah ya saka da alheri."

Mutumin ya zaro ido cike da mamaki Bintoto ta dafe tiren goronta da ke kanta ta manna da gudu. Jamila kam sororo ta yi tana fargaban abin da zai yi musu ta kasa motsawa daga inda take tsaye, sai da Bintoto ta waigo cikin gudun tana cewa,

"Wallahi ki zo mu je idan ya yanke miki kai babu ruwana."

Jin haka ya sa Jamila bin bayanta da gudu ita ma, yana ta kiran su amma ina ko waigo shi ba su yi ba. Sai ma ƙara ƙaimin gudun da suke yi suna ƙoƙarin shigewa

cikin mutane. Bintoto tana gudu tana dariya har suka ɓace masa cikin dandazon mutanen da suka zo cin kasuwar.

Mutumin ya bi mutanen da ke kasuwar da kallo cike da tsabar mamakin da suka ba shi, babu shiri ya fashe da dariya shi ma saboda ko kaɗan bai yi tunanin za su iya yi masa wayo, hakan ya sa bai ji haushi ba. Asali ma shirmensu nasu nishaɗi ya saka shi, yana ta dariya har ya samu wani a cikin filin kasuwar ya tambaye shi ta inda zai bi ya isa gidan hakimin garin.

Mutumin ya yi masa nuni da hannu a kan ya koma cikin garin duk wanda ya tambaya zai kai shi gidan, ya yi masa godiya tare da ciro kuɗi ya yi masa alheri, sannan ya buga motarsa ya koma cikin garin.

Bintoto kam bayan sun daina gudun suka shiga sauke numfashin wahala, wata rumfa suka zauna suna dariya. Jamila tana nishi ta ce,

"Wallahi ke muguwa ce Bintoto, yanzu don mugunta kika hana mu nuna masa gidan kika saka shi ya yi wannan wahalar a banza?"

Bintoto dafe da cikinta tana dariya ta ce, "To ba mun sha lotonmu ba? Haka kawai sai mu bar banza ta wuce mu? Da fa yanzu ba mu isa zuwa kasuwar nan ba."

Jamila tana ci gaba da dariya ta ce,

"Kin san Allah; ban taɓa shiga mota ba sai yau, ashe haka ake ji idan an shiga wani shuuuuuu kamar ana tafiya cikin iska?"

Bintoto ta sake fashewa da wata arniyar dariyar sannan ta ce,

"Allah ya so ni ni kam na taɓa shiga sau ɗaya wannan ne na biyu, ai yasin da ban san ta yadda zan buɗe motar ba, da shikenan ƙaryarmu ta ƙare don wallahi tsaf zai iya tafiya da mu garinsu, ya kai mu a yanka mu da ranmu su sha daɗinsu."

Jamila ta miƙe tsaye tana faɗin, "Ni dai ta shi mu je kada ya zo ya same mu a nan mu shiga uku."

Bintoto ta miƙe tana cigaba da dariya ta ce, "Ke kam Jamila wallahi baƙar matsoraciya ce ke, shi ya sa ba koyaushe nake son fita da ke talla ba."

Jamila ta yi banza ba ita, har suka ci kasuwar suka siyar da komai ba su daina dariyar abin da suka aikata ba.

.

1230094555 Access Bank Hadiza D. Auta Ibrahim. Shaidar biya ta wannan lambar; 08022014771.

D/AUTA Ce✍

SHAGALALLIYA!

HADIZA D. AUTA

LAMBA TARA.

Bayan sun gama cin kasuwar, a kan hanya Bintoto ta ja wa Jamila kunne cikin tsiwa ta ce mata,

"Saura kuma idan muka koma gida ki faɗi abin da muka yi asirinmu ya tonu."

Talatu tana dariya ta ce, "Ba zan faɗi ba ai, kada na sha duka a banza wajen Habu, ko daman can neman abin da zan yi kawai yake yi don ya dake ni koyaushe."

Bintoto ta yi mata wani kallo a lalace sannan ta fara magana tana jifar ta da harara ta ce,

"To ke sai ki zauna kina kallo ƙato ya yi ta jibgar ki? Ai na rantse da Allah da ni ce ke tsaf zan sha fili da shi mu daki juna. Ke ko kin tsaya tsoro yana cin zalinki a banza..uhumm!"

Jamila ta zaro ido waje tana cewa,

"Rufa mini asiri Bintoto! Yayan nawa zan daka? Cabɗijam! Ai da kuwa a ranar sai ya somar da ni idan ya riƙa ni."

Bintoto ta murguɗa mata baki tana marmaɗi da ido tana cewa,

"Eh, shi fa! To ubanki ne da ba za ki rama ba? Ni wallahi kin ga Kulu idan ta dake ni ramawa nake yi, ke ko Kawu Manin ne ya dake ni wani zubin cizon shi nake yi ballantana ke da Habu yake yayanki, ai ba haifar ki ya yi ba."

Jamila ta riƙe baki da tagumi tana jinjina maganar Bintoton kafa j ta sake cewa,

"Cabɗijam! Ai ranar da duk na gwada ramawa na san har karya ni sai ya yi wallahi, yanzun ma fa sai Inna ta saka baki yake ƙyale ni idan ya yi zuciya..hu'ummm! Lalle! To Ni kin ga tafiyata tun kafin wani ya ji hirarmu a faɗa masa na shiga uku."

Kai-tsaye ta saki hanyar da suke bi ta yi ratsen wata hanyar da za ta kai ta gidansu. Tafiya take yi amma a cikin zuciyarta tana ta jinjina irin dukan kawo wuƙar da za a yi mata a duk ranar d ta yi kuskuren rama dukan da Habu yake yi mata. Saboda Babansu ya ba shi damar hukunta duk wanda ya yi laifi a cikin gidan, har Innarsu wani lokaci yana hana ta abu kuma ya sa ta yi, saboda ko kaɗan ba ta tsayuwa inda Allah Ya ajiye ta, ba ta da aiki sai yawon gidaje da an yi an ce. Shi ya

sa wani lokaci har gida ake zuwa turkar ta, don ma Habun yana namijin ƙoƙarin kare mata martaba a duk lokacin da aka zo gidan da ƙudurin cin zarafinta.

Bintoto kam da harara ta bi Jamila cikin jin haushi ta ce,

"Ni ma idan ban da ƙaddara ai ke ba tsarata ba ce ballantana har na yi abota da ke, don watarana ma idan na yi kuɗi ku ne masu goge mini silifas a lokacin da na dawo daga Makka."

Haka ta yi ta mitar zancenta tana tafiya tana surutai tamkar da wani take labari, da abin ya yi mata daɗi ma ajiye tiren goron ta yi tana wata kalar tafiya cikin yauƙi har da sagale hannu irin na 'yangayu, tana yatsine fuska riƙe da ƙugu ta ce,

"Ke kawo mini abinci ki je ki ɗebo mini ruwa na sha, ke kuma zo ki yi muni fifita zafi nake ji. Yawwa ke kuma zo lunda mini hancin..."

Haka ta yi ta hauka ita kaɗai sai da ta hango wani dattijo tafe a kan hanyar sannan ta ɗauki tiren ta ɗora a kai tana tafiya tana cewa,

"Ai na rantse duk na yi kuɗi sai nasa an yi mini wanka, don babu abin da zan sake yi sai dai na yi zaunena a yi ta mini komai. Haka kawai zan bari na yi wasa da dama ta! Bayan a garin nan namu kaf babu wanda ya fi ni son na zama Hajiya matar Alhaji."

Tana gaf da shigewa gidansu ta hango wata yarinya ɗauke da kwano a kanta, murya ta ɗaga tana kiran sunanta tare da bai wa yarinyar umarnin ta zo. Cikin haɗe fuska ta waiga saboda ta gama gane muryarta tana gunguni ta ce,

"Aike na a ka yi fa!"

Bintoto ta galla mata harara tare da riƙe ƙugu ta sake cewa,

"To wani abu na ce zan yi miki? Cewa fa kawai na yi ki zo."

Yarinyar ta kafe a kan ba za ta je ba sauri take yi, Bintoto ta tako cikin fushi da taƙama har inda yarinyar take tsaye tana ta gunguni. Fuskarta a haɗe ta cewa yarinyar,

"Ni dai buɗa mu gani mene ne a cikin kwanon? "

Yarinyar ta yi mata wani kallon uku kwabo tare da ja baya tana cewa,

"To dambu ne, kuma aike na aka yi na kai wa Inna tsohuwa."

Bintoto ta ɗaga kai kasancewar ta fi yarinyar tsawo ta buɗa murfin kwanon duk da yunƙurin hana ta gani da ta yi, ƙamshin manƙuli da dambun ya sha ya sa ta yi saurin haɗiye yawu muƙut riƙe da murfin ta leƙa fuskar yarinyar cikin sassauta murya ta ce,

"Don Allah Dije kin bari na yi loma uku?"

Yarinyar ta girgiza kai alamun a'a, Bintoto ta ɓata fuskata cike da jin haushi ta ce,

"To biyu fa?"

A nan ma yarinyar ta turo baki ta ce,

"Aike na fa aka yi ba nawa ba ne."

Bintoto ta marairece fuska ta ce,

"To loma ɗaya kacal! Na san dai ita ba za ki hana ni ba ko?"

Yarinyar cikin ƙosawa ta yi saurin cewa,

"To ni dai kada ki yi babbar loma kada a gane an taɓa."

Bintoto ta washe baki cike da jin daɗi ta jefa hannunta a cikin kwanon da ke saman kan yarinyar, tsabar mugunta ta kwaso dambu cike fam da hannunta har da tozo, cikin sauri ta kai bakinta tana runtse ido. Da ƙyar ta samu ta haɗiye shi, idanuwanta har da ja suka yi garin haɗiyar yawun da zai wuce mata da shi a wuya, maimakon ta mayar da murfin ta rufe salun-alun; sai ta koma ɗebo wata arniyar lomar da ta kwashe fiye da rabin dambun tana faɗin,

"Sai dai ki yi haƙuri don wallahi ni kam ba zan tsaya iya loma ɗaya ba."

Ganin ta'asar da ta aikata yarinyar ta fara mita a kan don Allah ta rage kada a ce ita ce ta cinye shi a hanya. Amma hakan bai hana Bintoto auna dambun a bakinta ba, sannan ta rufe mata murfin ta yi ƙoƙarin yin magana tana cewa,

"Ni dai yi sauri ki tafi kada wani ya gani a ce na cuce k...."

Tsautsayi ya sa dambun ya sarƙe ta, nan take ta fara tari babu ƙaƙƙautawa saboda ya shaƙe mata wuya sosai, yayin da wani ya shige ta hancinta.

Ihu ta fasa tana zarar ido tare da jefar da tiren tallar goro ta faɗi ƙasa tana murƙususu cikin ƙasa, sannan tana ci gaba da tari riƙe da wuyanta cikin fitar hayyaci, yarinyar tana kallon ta tana murguɗa baki da gunguni ta ce,

"Allah ya ƙara miki baƙar muguwa."

Ta bar ta a nan tana ta mulmula a cikin ƙasa, tari kawai take yi tare da neman agajin ruwan da za ta sha amma babu kowa a wurin. Sai da ta gama jigatuwa tana gaf da shiɗewa sannan maƙociyarsu Duduwa ta fito daga gidansu, kamar almara ta hango ta kwance a ƙasa tana wani irin tari da nishi tamkar numfashinta zai fita, da sauri ta ƙaraso wurinta tana salati, cikin firgici da mugun tsoron da ya shige ta, ta tallabo ta suka yi wurin Kandala tana ƙwala mata kira cikin gigicewa.

Saboda ta tsorata da yanayin da ta gan ta, cikin sauri ta ajiye ta tsakiyar gidan ta ɗebo ruwa da gudu tamkar ta kifa ta kai wa bakinta, da sauri Bintoton ta fara zuƙar ruwan iya ƙarfinta, yayin da ruwan da sauran dambun da bai wuce ba suka haɗu suka sake sarƙe ta har zuwa cikin ƙwaƙwalwar kanta da hancinta. Babu shiri ta faɗi kwance riƙe da hanci da kai tana kwarara ihu da ɗan sauran ƙarfin da ya rage a jikinta.

"Wayyo zan mutu! Hancina! Kandala hancina!"

Kandala ta ƙara ruɗewa ta ja ta a jikinta ta fara hura mata maɗiga, sannan ta koma bubbuga mata baya a haukace, Bintoto kam sai ihu take yi tare da rirriƙe wuyan Kandalar saboda azaba. Sai da ƙyar ta ji abin ya lafa mata, sannan ta daina kururuwa bayan ta tara wa kanta mutane. Waɗanda ba ta san da su a kanta ba sai da ta fara dawowa cikin hayyacinta, a nan aka shiga jajanta wa Kandala tare da addu'ar Allah Ya tsare gaba.

Amma tsabar shaƙiyanci irin nata, bayan kowa ya watse ta dawo dariyar Kandala saboda ganin yadda ta nemi haukacewa don kawai ta sarƙe. Cike da jin haushin firgicin da ta saka ta a banza, ta dungure mata kai tare da tashi daga zaman 'yan borin da ta yi, bayan ta kakkaɓe ƙasar da Bintoton ta yi mata wanka da ita a lokacin da take turmuje-turmuje a cikin ƙasa.

"Wai Allah! Yau na ciyo wa kaina wahala, amman fa wallahi dambun da daɗi Kandala."

.

Ta yi maganar tana kallon bayanta, babu shiri ta waigo cikin faɗa ta yi magana cike da ƙunar rai ta ce,

"Dambun mutane kika ci ashe? To Wallahi duk kika jawo mini rigima yau sai kin ci duka a cikin gidan nan."

Bintoto tana dariya ta sake cewa,

"Raina ne ya biya da shi Kandala, shi ya sa na ɗan ci kaɗan, amma fa cikina ya cika kamar na ƙoshi da na sha ruwan nan yanzu."

Kandala ta buɗa baki za ta yi magana kenan suka ji muryar Inna tsohuwa kakar Dije, surfa bala'i take yi tun a soron gidan har ta shigo cikin gidan, Bintoto ta miƙe jikinta yana rawa ta yi bayinsu da gudu, Inna tsohuwar kuma kasancewarta 'yar bala'i tana ƙarasowa gaban Kandala ta dangwarar da kwanon dambun, a masifance ta fara magana tana haɗa numfashi ta ce,

"Ga dambun nan na kawo mata ta ƙarasa cinyewa! Amma ku sani sai ta san ta ci shi yau! Don daga nan idan na fita wurin Malam Mainasara zan je a ja mata yasin mai wuta, gobe ko an ce ta sake tare Dije ta taɓa abincina wallahi ba za ta iya ba. Domin kuwa gabaɗaya sai na sa an shafe mata maƙogwaro ta yadda ko ruwa ba za ta iya haɗiyewa ba ballantana ta ci abinci."

Tana gama faɗar hakan ta wuce fuuuuu ta bar gidan, Kandala ta bi kwanon dambun da kallo ko motsi ta kasa yi, saboda takaici ya daskare ta wuri ɗaya tamkar icen da aka gama dasawa.

1K ne kuɗin littafin. 1230094555 Access Bank Hadiza D. Auta Ibrahim. Shaidar biya ta wannan lambar; 08022014771.

D. AUTA✍

SHAGALALLIYA

HADIZA D. AUTA

LAMBA GOMA.

Ranta a ɓace ta waigo ta kalle ta fuska a haɗe ta ce,

"To ai sai ki zo ga dambun nan an kawo miki ki ƙasara cinyewa, tun da kin zama mayya! Ke har kullum nasiha nake yi miki amma Allah bai sa kika koyi kawar da kai da danganar Musulunci ba? Ke kenan ba za ki ga abu ki bar shi yadda kika gan shi ba sai kin yi shigar sharu ba shan...ki zo na ce!"

Ta ƙarasa maganar a ƙufule cikin fusata, Bintoto ta baro jikin katangar bayin da take laɓe cikin ɗar ɗar ta isa gaban Kandala cikin marairece fuska fiki-fiki da ido ta ce,

"Wallahi Allah Kandala ita ta ce na zo na ci ina tafiyata ni ban ma san da ita ba, amma ta kira ni. Kuma sai da na ce mata ba zan ci ba, ba zan ci b...ta yi ta roƙo na da Allah na ci ko kaɗan ne, shi ne kuma don ba ta da imani ta yi mini sharri. Bayan ita ma ai na gan ta tana cin dambun a kan hanya tun kafin ni na ci."

Kandalar ta ƙura mata kallo tana nazarin maganar sannan ta wurga mata wata jar harara ta ce,

"Kin san Allah Bintoto ki kiyaye ni kada ki janyo na lakaɗa miki mugun dukan da zan karya ƙafarki da shegen hannun da kika ci dambun da shi. Don wannan guntun bakin naki mai kama da bakin kajin Kulu; ya tabbatar mini da cewa ƙwace dambun kika yi ta ƙarfi kika ci ba roƙon ki ta yi ba."

Bintoto ta zaro ido waje a ruɗe tana cewa,

"La'ilaha illallahu kai Kandala! To idan har da gaske ƙwace na yi mata a ce kwarankwatsa dubu ta faɗo mini a ka. Amma wallahi Allah ita ce ta ce da ni na zo na ci, idan kuma kin zaci ƙarya nake yi a kira Dijen yanzu a gabanki ki tambaye ta ki ji idan ba ta faɗi gaskiya ba."

Kandala ta yi kanta a zafafafe ba tare da Bintoton ta tantance ba ta ji ta fisgo ta da ƙarfi. Ihu ta saka tana tirjiya amma sai da ta kai ta gaban kwanon ta dangwarar da ita, tare da kai mata wata muguwar faka a ƙeyar kai. Ta faɗi ƙasa daɓas tana ci gaba da rantse-rantsen Dijen ce ta ce ta ci ita ba ƙwace ta yi mata ba, Kandala ta ɗauko kwanon ta ajiye saman cinyarta cikin ƙunar zuciya ta ɗaga wata fanteka da ke kusa da ita sama tana cewa,

"Kafin na lissafa uku ki cinye shi tas ko kuma wallahi ki janyo na ƙara ɓalle miki gotaccen hannunki yanzun nan ba tare da na tantance b...baƙar kwaɗayayyiya!"

Bintoto ta zumɓuro baki tana muimui alamun ba ta son cin dambun, kafin Kandala ta shammace ta ta kai wa bakin faka, babu shiri ta fasa ƙara dafe da bakin tana faɗin,

"Wayyo bakina!"

Kandala ta ƙara kai mata wani dundu a tsakiyar baya ranta a ɓace tana cewa,

"Za ki cinye dambun ko sai na yi miki ɗure? Don billahillazi ba zan yi kunya biyu ba, dole ne ki cinye shi tas, ni kuma na ji daɗin kai Hajo ƙara wurin Dagaci. Don da raina da lafiyata ba zan taɓa bari ki rasa maƙogwaro b...za ki ci ko sai na dinga kwakkwaɗa miki fantekar nan..?"

Bintoton ta janyo kwanon tana kwarantun faɗin,

"Innalilahi Kandala! Ni kam ko haƙora ɗaya babu a bakina duk kin zubar da su garin dukan bakin. Don Allah ni dai ki yi haƙuri wallahi na ƙoshi dubi cikin..."

Ta ƙare maganar tana turo cikin yayin da Kandala ta kai mata wani mugun mangari da fantekar a kai kafin ta sake cewa,

"Ƙundun ubanki Bintoto! Na ce da ke ƙundun ubanki malfar Amadun Jaririya! Za ki cinye ki ba ni kwanon ko kuwa sai kin jawo maƙogwaron naki ya toshe a banza?"

Bintoto ta fara kai loma tana matsar ƙwallah cike da jin zafin zagin da ta yi wa Babanta ta haɗa har da kakarta Jaririya, waton mahaifiyar Amadun. Kandala ta samo dogon kare ta tsaya kanta har sai da ta cinye dambun ta sha ruwa, sannan ta lafta mata karen a baya cikin masifa da ɗaga murya ta sakw cewa,

"To Hajo an ci dambun ki ki sa a toshe mata numfashi ma ba iya maƙogwaro ba. Sannan ke kuma wallahi kika kuskura na ji ko kallon jikanyarta kin sake yi sai na canza miki fuska, kuma ki sani kwanan nan zan mayar da ke wurin Amadu tun da kin fara lalacewa ki je can Jaririya ta ɗora daga inda na tsaya, ke kullum ba za ki bar mutum ya huta ba sai kin janyo abin da zai dame shi. Idan ban da Allah ya yi ni mai taurin ƙashi da na zuciya da tuni kin sa hawan jini ya kama ni."

Bintoto ta bi ta da wani kallo hawaye yana zuba a kan fuskarta tana zunɓuro baki tana gunguni. Kandala ta kwaɗa mata wata uwar tsawa ta ce,

"Za ki tashi daga nan ko sai na taushe ki?"

Bintoto ta miƙe tana gunguni ta yi cikin ɗakinsu, Kandala kuwa juyawar da za ta yi caraf suka haɗa ido da Kulu, wadda ke tsaye ta sha jinin jikinta tana kallon su cike da jin daɗi tana ƙumshe dariya, babu shiri ta yi saurin haɗiye dariyar da take yi ta bar wajen da sassarfa ta faɗa ɗakinta. A harzuƙe Kandala ta ɗaga murya tana cewa,

"To mazuga maƙwangama masu zuwa lahira da allon makaɗi! Kin ji daɗi ko? Sai ki zuba ruwa ƙasa ki sha baƙar munafuka, don zalunci ba za ki ce a yi haƙuri ba sai dai ki laɓe kina ta dariya! To ki sani tun da har kika ƙi ba ni haƙuri na yi ta dukan ta kina kallo; wallahi sai Allah ya isar mata a kanki, don da a ce kin zo kin ba ni haƙuri da yanzu ban yi mata abin da na yi mata ba. Ke kam Kulu zama da ke ma bai da wata rana ko kaɗan. Mani ya kwaso jangwam ya ajiye mana a cikin gida..."

Haka ta dinga sauke haushin ta a kan Kulu tana zabga faɗa kamar ta ci babu, Kulu kam ta lafe a cikin ɗakinta tana ƙyalƙyala dariya, saboda faɗan rashin dalilin

da Kandala take yi a banza a wofi ya sa ko kaɗan ba ta ji zafin maganganun da take wurga mata ba.

Wunin ranar zir haka suka cinye shi daga Kandalar har Bintoto babu wata walwala, da dare ya yi ma ko kwanciyar da suke yi a gado ɗaya Bintoto ƙin hawa gadon ta yi, ta yi kwanciyarta ƙasa ita ma Kandalar ta ƙyale ta.

Sai da tsakiyar dare da Bintoton ta ga barcin Kandala ya yi ƙarfi tana ta minshari sannan ta lallaɓa ta kwanta bayanta, saboda sabo da kwanciya bayanta ya sa ta kasa yin barcin kirki tun da ta farka, ta yi ta juye-juyenta tana gunguni saboda har lokacin ba ta daina jin haushin ta ba. Amma tana kwanciya bayanta kafin ka ce me har barci ya yi awon gaba da ita, sai da Kandalar ta tashi fitsari ta gan ta a bayanta ƙafarta saman jikinta ɗaram. A ranta ta ce, 'Ba kin ce ba kya ji ba! Gobe ma ki sake 'yar malfar uba.'

Da dabara ta sauke ƙafar a hankali sannan ta miƙe ta fice ɗakin. Da safe ma Bintoto da fushi ta tashi don da ta ci alwashin sai ta rama dukan da ta yi mata a kan Dije, a cewarta tun da ta jawo aka buge ta a banza ita ma sai ta ji a jikinta, haushin hakan ya sa ko karin safe ba ta ci ba.

Tana zaune cikin rana tana shan hantsi da gunguni a bakinta suka jiyo sallamar Hari, cikin sauri ta miƙe ta nufi wurinta tana ihun murnar ganin ta, ita ma Harin cike da jin daɗi ta rungume ta a jikinta tana faɗin,

"Oyoyo ɗiyata."

Bintoto ta ruƙunƙume ta har zuwa wurin Kandala da ke ta faman wasar baki tana ce wa Hari marhaban lale da zuwa.

Jikinta yana rawa ta shinfiɗa mata tabarma ta zauna, Bintoto maƙale a jikinta suka fara gaisawa da Kandala a tsanake, sannan ta kalli Bintoto da ke wasa da gefen gyalenta tana cewa,

"Yʼata kwana biyu ya jikin naki? Ina can ina tunanin halin da na bar ki. Hannun ya warke ko?"

Bintoto ta turo baki cikin muryar shagwaɓa ta ce, "Bayan jiya Kandala ta yi ta duka na saura kaɗan ta ƙara karya mini hannu..."

Hari ta rufe baki tana ƙumshe dariya ta ce mata,

"To me kika yi aka dake ki?"

Bintoto ta share hawayenta da ya jiƙa mata fuska ta ce,

"Wai cewa ta yi na ci dambu bayan ni ko cin shi ma ban yi ba, ga shi yau ko abin karin safe ma ƙin ba ni ta yi cikina sai kuka yake yi."

Hari ta kalli Kandala tana 'yar dariya ta ce,

"Inna me 'yata ta yi aka dake ta kuma ba aka hana mata abincin safe?"

Kandala cike da jin haushi ta miƙe ta buɗa wani kwano ta ce,

"Kin ga ɗumamen tuwonta da aka ba ta ta ƙi ci tun da safe. Har hura na ce ta je ta sha idan ba ta son tuwon amma ta yi banza da ni. To don bindin jakin Amadu ki je duk inda za ki faɗa na hana abincin tun da Amadun Jaririya ya ba ni ki ce kada ya sake ba ni gobe."

A masifance ta zauna tana hararar Bintoton ta sake cewa,

"Ai wannan 'yar taki da kike gani wallahi baƙin halinta ya fara saka ni tunanin kai ta gidan ubanta, don na gaji da jawo mini maganar da take yi. Ni kenan kullum raba faɗa da bayar da haƙuri bayan ni kaina ba ta bar ni na huta ba."

Hari ta yi shiru tana nazari na ɗan lokaci sannan ta kalli Kandalar ta ce,

"Ki yi haƙuri Inna, kin san kowane yaro da kalar ƙurciyarsa, saboda haka idan har kin amince ni zan je da Bintu birni ta zauna a hannuna, idan kuma Allah ya kawo wurin aiki nagari sai na kai ta ta zauna ko babu komai tana rage miki waɗannan abubuwan da take aikatawa, amma dai ke ya kika gani?"

To fa! Anya Kandala za ta iya rabuwa da Bintoto kuwa?😄

Akafta😊

PRINCESS DIJA✍.

SHAGALALLIYA!

HADIZA D/AUTA

1k kacal kuɗin littafin, 1230094555 Access Bank Hadiza D. Auta Ibrahim. Shaidar biya 08022014771.

LAMBA SHAƊAYA.

Ido Kandala ta zaro tare da dafe ƙirji tana cewa,

"Aika..me...?"

Cikin sanyi jiki Hari ta ce,

"Aikatau Inna, amma kuma idan kin ga da matsala sai ta yi zamanta a hannuna kawai."

Kandala cikin rashin kuzari ta ce,

"Ke ma kin san ba zan iya rabuwa da Bintoto ba, amma idan har za a haɗa da ni a wurin aikatau ɗin sai mu je ni da ita, kin ga shikenan ba za mu daina ganin juna ba idan muna tare."

Hari ta ƙumshe dariyarta sannan ta ce, "To ai ke Inna duk in da za a kaita a can za ta zauna tare da su, kuma idan aka ce da ke za ta iya yiyuwa ma su ce sun fasa, don haka idan har kin gamsu da ba zan cutar da Bintoto ba; to ki amince ta zauna a hannuna, da sharaɗin idan ta samu aikin za ta je ta wuni wurin aikin ta dawo wurina ta kwanta. Amma ke ya kika gani yanzu?"

Nan take cikin Kandala ya shiga murɗawa saboda tashin hankali da faɗuwar da gabanta yake yi. Jikinta yana rawa ta miƙe ta ja buta aguje ta yi bayi, Bintoto ta bi ta da kallo toshe da baki tana dariya har sai da ta shige, sannan ta tashi daga kwancen da take a kan cinyar Hari ta zo daidai kunnenta ta yi mata raɗar cewa,

"Don Allah ki sace ni kawai mu yi tafiyarmu, don wallahi Kandala ba za ta amince ta bari na yi tafiyar nan cikin daɗin rai ba."

Inna Hari ta janyo hannunta ta riƙe gam sannan ta ce,

"Waton ke har murna kike yi za ki tafi ki bar ta ko?"

Bintoton ta turo baki tana cewa,

"Ni fa mai kuɗi nake son na aura a can birnin ya kai ni Makka."

Hari ta rufe baki tana dariya ta ce,

"Ashe Bintu har yanzu ba ki daina wannan shirmen naki ba?"

Bintoto ta lafe a jikinta tana cewa,

"Haƙorin Kandala ma ina so na sa a cire shi idan na yi kuɗi a saka mata na ƙarfe."

Hari tana dariyar shirmen Bintoton Kandala ta fito daga bayin riƙe da ƙugu tana haki kamar wadda ta sha gudu ta dawo mazauninta ta zauna, sannan ta kalli Hari ƙwalla cike da idonta ta ce,

"Ni dai Hari da an bar zancen nan Allah ya gani da na fi farin ciki, saboda ina hangen kamar Babanta ma ba zai amince da wannan tafiyar b..."

Bintoton ta yi saurin faɗin,

"Ke dai Kandala sai idan ke ce kawai ba ki so na je, amma ina ruwan Babana da wannan tafiyar shi da ko damuwa ba ya yi da gani na? Sai dai idan baƙinciki kike so ki yi mini kada na samu wanda zai kai ni Makka don kin ga ina son zuwa."

Kandala ta bi ta da kallo riƙe da haɓa ranta a ɓace ta ce,

"Da ina baƙinciki da ke tun a ranar da kika yi sanadin mutuwar Habi zan murƙushe ki sai kin daina numfashi, don haka tun da ma kika yi wannan maganar babu inda za ki je! Makkah kuma ki hau buzu ki tashi sama rauhanai su kai ki ki tabbata a can idan kina so ba damuwata ba ce."

Ta miƙe cike da jin haushi ta shige ɗakinta, Hari ta kalli Bintoton cikin sanyin jiki ta ce,

"Me ya sa kika ce mata haka? To bari ki ji ni na ma fasa tafiyar da ke, kuma daga yau ban sake zuwa ganin ki tun da ba ki jin magana."

Hari ta miƙe da niyyar tafiya, Bintoto ta yi saurin riƙe mata hannu cikin hawaye ta ce,

"Don Allah ki yi haƙuri Inna, daga yau na daina ba zan sake ba kin ji? Ai kin haƙura ko?"

Hari ta janye hannunta tana cewa,

"To sake ni na je na bai wa Inna haƙuri."

Bintoto ta sake ta tana share ƙwalla, Hari ta yi cikin ɗakin da sallamarta a baki, da murya ƙasa Kandala ta amsa mata saboda kukan da take yi, jikin Hari ya yi sanyi ƙalau ta zauna bakin gado zuciyarta cike da tunanin janye ƙudurinta a huta, saboda hango idanuwan Kandala da suka rine nan take zuwa ja, tsabar takaicin Bintoto da baƙin cikin da take ciki na rabuwa da ita. Hari ta fara magana cikin tattausan lafazi ta ce mata,

"Don Allah Inna ki yi haƙuri, kin san shirmen Bintoton ta iya yiyuwa ma ita ba ta san ma'anar abin da ta faɗa miki ba, don haka don Allah ki yafe mata, sannan kuma idan hankalinki bai kwanta da tafiyar ba sai a fasa kawai. Amma Inna inda kin daure kin amince da tafiyar za ki ga amfaninta a gaba, ko babu komai za ta nutsu ta rage wannan rashin jin da take yi koyaushe."

Kandala ta saka gefen zaninta ta share hawaye sannan ta ce,

"Ni dai gaskiya da a za a samo mana wurin aikatau ɗin ni da ita da na fi jin daɗin wannan tafiyar, amma wallahi ko kaɗan ba zan iya barin ta ta je birni ta zauna babu ni ba."

Hari ta ce, "To idan muka je tare Inna shi Mani da matarsa fa? Barin su za ki yi su kaɗai anan ki bi Bintoto?"

Kandala ta yi wani mere sannan ta ce, '"Tun da ba ni nake auren ta ba ai dole na bar ta na tafi Hari, idan ya ji yana iyawa ya kula da matarsa don na gaji da zaman ciyar da ita yana gindin bishiya yana shan iska koyaushe, saboda bai da wani aiki sai na zaman kashe wando suna gulmar mutane."

Hari ta yi shiru na ɗan lokaci sannan ta ce, "To tun da haka ne in sha Allahu zan je na bincika na ji ko za a samu inda za ki rakuɓa ke ma ki yi aikin, amma ita yana da kyau yanzu idan na tashi tafiya na je da ita, idan aka yi katari daga zuwa aka samu

gidan kirki sai na haɗa ta da su, ke kuma ko daga baya ne sai na zo mu tafi idan an samu naki wurin aikin."

Kandala ta marairece fuska tana cewa, "Da dai za ki taimaka da kin bari ni ma mun tafi tare a yanzun, kin ga sai na zauna a wurinki har a samu wurin aikin . Idan ma abin kashewa ne babu to ni ina da kuɗin da zan ba ki a haɗa mu ci abinci kafin a samu nawa aikin."

Hari kanta ya yi nauyi girim, domin ta rasa ta wace hanya za ta bi ta zille mata, ganin ba dama ya sa ta amince mata dole don babu yadda za ta yi, kai-tsaye ta ce su shirya dukansu, idan ta yi kwana biyu za ta dawo su tafi tare.

Da haka aka katse maganar sannan hankalin Kandala ya kwanta, amma Bintoto hannu ta ɗora a ka tana ihu da kururuwar wayyo Allah sai ta bi Hari, duk da an sanar da ita cewa za ta dawo su tafi amma ba ta yarda ba, ita dole da ita za ta tafi ƙafa-da-ƙafa.

Da ƙyar ta samu ta shawo kanta ta fice gidan, ta ɗauki lokaci tana cin kukanta, tare da iƙirarin sai ta je birni ta auri mai kuɗin da zai kai ta Makka.

Bayan kwana biyu labari ya watsu a cikin gari Kandala da Bintoto za su je birni aikatau, wasu da yawa sun zo har gida suna nuna wa Kandala ta yi zamanta ta bar Bintoto kawai ta je, amma ta kafe kai-da-fata a kan sam ba za ta zauna ba ƙafarta ƙafar Bintotonta.

Kulu kam murna cikin ranta kamar ta zuba ruwa a ƙasa ta sha don daɗi, Mani ne kawai mai baƙincikin tafiyar da takaicin rashin da zai yi, don da ma ita ce gatansa, idan ta tafi bai san yadda zai yi da hidimar gida da sauran matsalolin yau da gobe na rayuwa ba, shi ya sa ya yi ta magiya a kan kada ta je ta bar Bintoto kawai su tafi, amma ganin babu fuska ya daina kushe tafiyar ya koma neman abin da zai samu a wurinta kafin ta tafi.

Bintoto kam bankwana ta dinga yi da ƙawayenta, tana sanar da su mai kuɗi za ta aura idan ta je birni wanda zai kai ta Makka. Jamila kuwa alƙawari ta yi mata a kan cewa duk ranar da ta yi kuɗi ita za ta dinga yi mata aikatau a gidanta. Jamila tana dariyar haukar ta da sambatun da take yi na shirme ta ce da Bintoton,

"Ke a tunaninki don kin je birni aikatau sai ki yi kuɗi har ki je Makka? Lalle ma, to ai ko su Karime da Habbobo da suka tafi babu abin da suka samo. Kuma har suka

gama aikatau suka dawo gida ba su samu miji a birni a nan garin aka yi musu aure. Don haka ke ma...."

"Yi mini shiru da baƙin bakinki!"

Bintoto ta kai wa Jamila wani kalar naushi a saman bakinta, wanda ya saka ta dakatar da maganar ba tare da ta shirya ba. Tare da yi mata wani mugun kallo kafin ta ce,

"Sannu mai baƙin baki! To ta Allah ba taki ba ce ai, na san baƙin cikin tafiyar kike ji shi ya sa kike yi mini muguwar fata. To ko kina so ko ba kya so sai na auri miji ɗan birni kuma a gaban idonki zai kai ni Makka. Kuma na rantse da Allah kina kallo zan yi rabon kayan Makka, sai na bai wa kowa a garin nan amma ke na hana mik...kuma daga yau ko gani na kika yi kika yi mini magana sai na darje miki baƙin bakinki mai shegen wari."

Tana gama faɗar hakan ta bar wurin bayan ta buga mata tsaki har da zuba mata yawu a jiki, tare da toshe hanci alamun warinta take ji. Jamila kam dafe bakin nata ta yi, wanda take jin zogin naushin da Bintoton ta yi mata har lokacin, sai ƙoƙarin shafa shi take yi saboda jinin da ke fita tana gogewa da gefen ɗankwalinta, yayin da take ta tofar da yawunta jinin yana fita. Saboda Bintoto ta fasa mata leɓe, sannan haƙorinta ma jini suke yi.

"Allah Ya isana wallahi. Baƙar muguwa kuma ba za ki taɓa auren ɗan birnin b..."

Jamila ta faɗa tana kallon bayan Bintoton, ganin ta juyo a fusace ta bar wurin da gudu, Bintoto ta rufa mata baya tana faɗin,

"Wallahi ki ma tsaya don ko gaban Innarki kika je sai na ci malfar ubank..."

Tsoro ya hana Jamila tsayawa, ta nufi gidansu da gudu tana kiran sunan Innarta. Bintoto ma ta afka babu shayi ta nemi jawo Jamila a bayan Innarta da tana ƙoƙarin kai mata duka. Innar Jamila ta samu riƙe hannuwan Bintoto gam tana faɗa, hakan

ya bai wa Jamila damar faɗawa ɗakinsu ta datse ƙofa. Haushi ya sa Bintoto yin cikin Innar Jamila da nufin su yi kokawa tana haki tana faɗin,

"Ai sai mu yi faɗan da ke tun da kin saye mata faɗan...." Tana maganar ta zura ƙafa ta shure garin da ta gani a cikin ƙwarya, daidai lokacin da Habu ya shigo gidan cike da mamaki, saboda ganin abin da ke faruwa kamar almara, Bintoto da kokawa da Innarsu. Ita ma kamar mai tsoron ta hannuwanta kawai ta dinga riƙewa amma ko duka ɗaya ba ta yi mata ba.

Jikinsa yana rawa ya katso bulalar dalbejiyar da ke tsakiyar gidan, idanuwansa a rufe ya dinga zabga wa Bintoto tana tsalle da ihun kiran sunan Kandala. Innarsu tana hana shi dukan ta amma bai ji ba, sai da ya zane ta raɗam sannan ya jefar da bulalar. Cikin masifa ya dinga faɗin,

"Idan ke ba za ki iya da ita ni zan iya, a kan me za ta zo har cikin gidanmu ta yi masa iskanc...?"

"Halin Kandala na sani Habu, a kan Bintoto komai tana iya yi a garin nan, ga shi ka yi mata irin wannan dukan ban san da wane idon zan kalle ta ba."

Ta yi maganar tana kama hannun Bintoto tare da ƙoƙarin miƙar da ita tsaye tana komawa, saboda ta daku sosai ko tsayuwa ba ta iya yi, amma hakan bai sa ta yi kuka ba.

"Duk abin da zai faru ya faru! Kokawa fa na ga tana yi da ke, wallahi ko gobe ta sake zuwa cikin gidan nan ta yi mana rashin mutunci sai na ci ubanta. Kandala ta daɗe ba ta tsire ni ba."

Yana gama faɗar maganar ya fice gidan, Jamila da Innar su suka yi cirko-cirko suna kallon Bintoto da ke kwance cikin ƙasa tana tofar da yawu. Saboda ganin yadda jikinta ya yi ruɗu-ruɗu da shatin bulala. Da ƙyar Innar Jamila ta miƙar da ita tsaye tare da yafa mayafinta ta riƙe ta zuwa gida. Da niyyar ta ba Kangala haƙuri saboda sanin Habu ya taro musu faɗan da ba su iyawa. Hakan ya sa ta ga gara kawai ta saduda tun da wuri kafin abin ya rincaɓe.

A yo agaji da tuwon ƙasa.😁

Princess Dija ✍

SHAGALALLIYA!

HADIZA D/AUTA

₦500, 1230094555 Access Bank Hadiza D. Auta Ibrahim. Shaidar biya 08022014771.

LAMBA SHA BIYU.

Tun a soron gidan Kandala Bintoto ta ƙwace daga riƙon da Innar Jamila ta yi mata, tare da duƙawa ƙasa ta damƙo ƙasa ta watsa musu a ido daga ita har Jamila. Ganin ta fasa ƙara Innarta kuma ta buga salati tana laluben bango, ita ma ta faɗi ƙasa tare da yage baki ta fasa wata uwar ƙara tana faɗin.

"Wayyo ni Allah wayyo ni kaina! Kandala! Kandala kina ina za a kashe ni?"

Sai ga Kandala ta faɗo soron kamar an jefo ta, zane yana kwancewa tana ƙoƙarin ɗaura shi, ɗankwali a hannunta ta isa inda Bintoton take ta kwatsa ihu iya ƙarfinta, jikinta yana rawa ta rungumo ta tana faɗin,

" Innahu min Sulaiman...ke..ke tsaya ki faɗa mini ke da wa?"

Kafin Bintoton ta rage kukan ta yi magana kamar yadda Kandalar ta buƙata; Innar Jamila da ta gama mutsuttsukar idanuwanta har sun yi ja, ta matso kusa da Kandala cikin marairaita tana faɗin,

"Haƙuri kawai za ki yi Kandala. Saboda duk abin da ya faru ita ce ta jawo. Amma dai don Allah da girman Manzon Raham....!

"Dakata Asabe! Daina zagaye-zagaye ki faɗa mini gaskiya me kika yi mata take irin wannan kukan tamkar wadda aka ɗora wa wuƙa a wuya?"

Cike da fargaba Innar Jamila ta karkace kai tana faɗin, "Wallahi billahillazi babu abin da na yi mata kin ji rantse irin rantsuwar ɗan Musulm...."

"Wallahi karya take yi Kandala! Ita da Jamila da Habu suka taru a kaina suna ta duka da buloli...dubi jikina ma ki ga shaida."

Ta ƙare maganar ta cire rigarta ta jefar tana nuna mata kalolin shatin da Habu ya yi mata, Kandala ta shiga salati tana tafa hannuwa idonta a kan Innar Jamila don ta kasa furta komai tsabar mamaki. Don ita kanta Asaben mamakin Bontoto ya sa ta shiga rabon ido tare da faɗin,

"Na rantse da Allah ƙarya kike yi Bintoto ni ko sau ɗaya ban sake ki ba, Jamila ma haka."

"Idan ƙarya nake yi ai ga shaida a jikin....Kandala wallahi idan kika ƙyale su ban yafe miki ba, saboda har da Baban Jamila aka dake ni. Ita ma Innarsu ta dake ni, Habu ma ya dake ni har da zagi na yana cewa ko ɗanbuzu ya dawo duniya sai ya dake shi ballantana ni ɗiyar Amadun Jaririy...."

"La'ilaha illallahu yau na ga bala'i ganin idona! Yanzu abin na Habu ya wuce dukan ki har ya kai kan ubana ɗanbuzu? To billahillazi yau ni ko su a garin nan! Sai na ga wanda ya ɗaure musu ƙugun haɗuwa su dake ki sannan har a zagar mini mafari."

Kandala tana ƙoƙarin miƙewa tsaye Innar Jamila ta yi wuff ta fice soron gidan tana jan hannun Jamila da ke bakin ƙofar gidan tana hawaye, don ƙasar da Bintoto ta watsa musu ta ƙi fita cikin idonta. Kandala kam tana miƙewa cikin gida ta nufa tana zazzaga masifa da zagin tushen Asabe da mijinta da 'ya'yanta tare da tsine musu albarka kala-kala. Hannun Bontoto ta ja bayan ta ba ta zane ta rufe jikinta suka fice gidan tamkar ta tashi sama.

Kulu ta bi su har bakin soron gidan cikin jimami, duk da wani gefen zuciyarta cike yake da jin daɗin an hora Bintoto. Bayan ta tabbatar sun tafi ta koma dariyar ƙeta ita kaɗai cikin gida tana yi tana buga ƙafa har da 'yar rawa alamun duniyar ta yi mata daɗi. Da ma can ta matsu su tafi birni su bar mata gidan ta sarara.

Kandala kam ba ta zame ko'ina ba sai 'yansandan garinsu suke zama. Don a cewarta ko wurin hakima ba za ta tsaya gudun a ce za a sasanta su ji bulus. Tiryan-tiryan Kandala ta yi wa 'yansandan bayanin cin zarafin da aka yi wa Bintoto. Ita ma da aka zo tambayar ta babu ko ɗar ta ce da 'yansandan Habu ya taɓa neman ya lalata ta, don ta ƙi amincewa ne ya ce duk ya kama ta sai halaka ta. Shi ne tana zuwa gidansu suka rufe ta da duka.

Sannan Kandala ta saka ta ɗage zanin da ta rufa mata tana nuna musu shatin bulolin da ke jikinta. Cikin ko-in-kula Bintoto ta zare zanen duka ta ajiye duk da 'yan ƙidan dangin da suka fara tsiro a jikinta. Ganin wani ɗansanda yana kallon ta ne ta yi hanzarin ɗaukar zanen ta rufa tana aika masa harara. Kafin ta zura kai daidai saiti da kunnen Kandala ta ce,

"Kin ga wani ɗansanda can yana kallon ƙirjina."

"To mene ne abin kallo a ƙirjin naki? Duk matan duniya ba su ishe su kallo ba sai k...?"

Bintoto ta yi hanzarin rufe mata baki don ba ta so ta buɗe zancen a fili ba. Jami'an ma ba su bi ta kan faɗan nata ba, sai haƙuri suka dinga ba ta cikin sigar wasa har ta sauko aka haɗa ta da wani ɗansandan da zai je ya zo da Habu, Jamila da iyayensu.

Zungui-zungui ɗansanda ya saka su Kandala a gaba har ƙofar gidan su Jamila, mutane suka dinga mamakin me gaminsu da 'yansanda. Cikin sa'a Habu zai shiga gidan, Bintoto ta yi tsalle tana nuna shi tana faɗin,

"Ga shi nan mugu, shi ne ya dake ni."

Caraf ɗansanda ya damƙe shi yana faɗin, "Ina sauran mutanen gidan?"

Sai da Habu ya yi masa wani kallo sannan ya ce, "Suna ciki."

"Inna, shiga ciki ki ce su fito."

Ɗansandan ya faɗa yana aika wa Habu wata muguwar harara. Habu ya shiga gyara zaman wuyan rigarsa yana cewa, "Ai ni na dake ta, mu tafi kawai ba sai an kira kowa b...."

"Wallahi ƙarya yake yi! Har da Babansu ya dake ni."

Bontoto ta yi hanzarin faɗa tana nuna shi da hannu tare da murguɗa masa baki da gungunin faɗin, "Allah Ya isa mugun banza."

Kandala kuwa tuni ta faɗa gidan tana kiran, "Asaben tana ina? Fito mu je, yau sai an fitar mana haƙƙinmu ni da Bontoto. Gobe ko wani kika ga ya buɗe baki zai furta sunan Ɗanbuzu za ki hana ballantana a zage shi gabanki. Idan ban da cin zalin irin naku Bontoto guda nawa ce da har za ku yi mata taron dangi ku dake ta. Don tsabar

abin kunya wai har da Alin kanwa. To, yau duk sai kun gane ba kanwar lasa nake ba."

Haka ta dinga maganganu har suka fice ƙofar daga ita har Asaben da Jamila. Inda suka tarar da ƙofar gidan ya cika ana ta tambayar abin da ya faru. Babu kunya Bontoto ta dinga faɗa wa mutane Habu ne ya so lalata ta.

Haka suka rankaya zuwa wurin da 'yansandan suke tsayuwa a bakin titin garinsu. Tare da mutanen da suka rako su duk da korar da ake yi musu sai da wasu suka rufa musu baya. Sai da suka sake jin ba'asin Kandala da na Bintoto sannan suka ji na Habu da na Innar Jamila da Jamila. A nan suka fahimci Bontoto ba ta da gaskiya, kuma maganganun da ta faɗa duka sun saɓa abin da su Habu suka faɗa.

Shugaban 'yansandan da ke wurin ya yi musu sulhu, tare da yi wa Habu faɗa sosai bayan ya sa an yi masa buloli kamar yadda ya saki ƙwanji ya yi wa Bintoto. Saboda ya tabbatar musu da lalle shi ne ya dake ta, kuma shi kaɗai ba tare da kowa ba. Bugu da ƙari mahaifinsu ma ba ya garin, ya tafi birni kai kanwa kamar yadda ta zamo sana'arsa.

Amma hakan bai hana su caji naira dubu huɗu daga hannun Habu ba, don ita ma Kandala sai da ta miƙa musu dubu ɗaya tun a farkon zuwanta don su ji daɗin yi mata abin da take so. A haka suka dawo gida bayan an saka Habu ya bai wa Kandala da Bintoto haƙuri, tare da kashedin duk ya sake shiga sabgarta sai sun rufe shi gidan yarin birni.

Sai dai ko kaɗan hukuncin da suka yi bai yi wa Kangala daɗi ba, don a son ranta a rufe su duka har Alin kanwa idan ya dawo garin. Innar Jamila kan tun a kan hanya ta yi wa Jamila kashedin ta raba abotarta da Bintoto. Kuma idan ta sake jin an gan su tare sai na lahira ya fi ta jin daɗi.

Habu kam komai bai ce da kowa ba, har ya shige gida ya faɗa ɗakinsa ya datse ƙofa. Saboda takaicin mari da tsinka jakar da aka yi masa bayan da gaskiyarsa. Sannan ya ci alwashin muddin Bontoto ta sake shiga gonarsa sai ya kusan kashe ta. Sai dai ya bar garin, amma ba zai lamunci iskancin kowa ba.

Kandala ma suna zuwa gidan ta ɗora ruwan zafi ta dinga gasa wa Bintoto jikinta tana ihun zafi ta yi a hankali. Haka mutane suka dinga zuwa yi wa Kandala jaje a kan abin da ya faru, don labari ya karaɗe ko'ina ana ta yamaɗiɗin Habu ya nemi Bintoto da lalata. Don ta ƙi amincewa ya lakaɗa mata mugun duka, shi ne dalilin da ya sa Kandala ta kira musu 'yansanda. Ana yi musu jajen a rai Bintoto tana faɗin,

'Baƙin mugu, ga shi nan ya ja wa kansa na ɓata masa suna a gari. Don ni ba Jamila ba ce ballantana na bari ya dake ni a banza.'

****

Bayan kwana biyar da faruwar rigimar Hari ta diro garin, cikin nasara ta sanar da Kandala ita ma an samu wurin aikinta, Kandala murna har tsakiyar kai. Nan take ta bar wa Kulu kula da akuyoyi da tumakin da take kiyo, tare da abin da kuɗin abin da za su ci kafin ta yi maramarin gida ta waiwayo wa garin. Sannan ta ɗauki ƙullin kayanta a kai na Bintoto a hannu suka rankaya bayan sun yi sallama da mutanen gari ana ta Allah Ya kiyaye.

Tafe suke a cikin motar da za ta kai su cikin babban birni, Bintoto da Kandala sai sharar barci suke yi har da minshari, irin minsharin da ya hana sauran mutanen da ke cikin motar sakewa, yayin da wasu ke tsaki masu earpiece kuma suka dinga maƙalawa a kunnuwansu. Saboda ƙarar minsharin da Kandala ke yi har da wani ƙugi, kuma tana dire shi za a ji ta sake jan wani numfashin sosai sannan ta sauke shi tare da wata haniniya mai kama da kukan doki, inda ƙarar sautinsa yake ta faɗin,

"Hiiiiiiii! Huhhhuhh!"

Kafin ta canza style ɗin minsharin ya koma faɗin, "Taaashii! Taaaashiii!"

Dole kallo da hankalin mutanen da ke cikin motar ya dawo kanta, domin wasu har da miƙewa tsaye suna leƙen fuskarta yadda yawun barcin ke biyo dogon haƙorinta mai tsini yana sauka saman zanin da ta yafa, har zuwa fuskar Bintoto da ta yi matashi da cinyarta.

Ganin hakan ya sa Hari ta kasa haƙuri ta fara tayar da ita daga barcin saboda ita ma kanta minsharin ya dame ta. Firgigit Kandala ta yi tare da yin miɗa da salati mai ƙarfi a bakinta, salatin da ya janyo Bintoto ta yi zumbur daga saman cinyarta, a bisa tsautsayi kanta ya daki bakin Kandalar, inda kai tsaye tsinin dogon haƙorin nata ya kai wa Bintoto sukar ba zata a cikin tsakiyar kai, babu shiri ta ƙwalla ihu tare da faɗin,

"Wayyo Allahna! An soka mini mashi a cikin kain..."

Kandala ta yi saurin lalabo kan nata cikin tausayawa tana faɗin,

"Yi haƙuri to! Ai duk ke ce kika jawo haƙorin nawa ya soke ki, amma tun da har Allah ya tsare wurin bai fashe ba ai sai ki gode wa Allah."

Bintoto ta yi saurin kallon bakin Kandalar tana cewa,

"Kandala yanzu kina nufin haƙorin giwarki ne ya cake ni haka tamkar an soka mini mashi!?"

Kandala ta kai wa Bintoto wani mangari a kai cike da jin haushin maganar ta ce,

"Kibiya ce ba mashi ba! Ƙaramar mara kunya waton a nan ɗin ma ba za ki bar ni ba sai kin sa na yi hargowa da ke ko? Toki gode wa Allah na taimake ki kin shigo motar nan da yanzu kina can an baro ki kina fama da kajin Kulu, idan kina bacci su yi maki kashi a baki."

Bintoto ta turo baki waje tana cewa,

"To ai ke ma ina ga har faɗuwa kika yi garin shiga motar aka tallabo ki kamar 'yar yarinya."

Wasu daga cikin mutanen motar suka fara dariya, saboda tun da suka fara musayar bakin suka shiga ƙumshe dariyar amma zancen Bintoto ya saka su dariyar dole.

Musamman waɗanda Kandala ta faɗi warwas a gabansu a lokacin da za ta shiga motar, wasu shaƙiyai har da riɓe ciki yayin dariyar tasu saboda tuno irin yakicewar da zaninta ya yi har sai da aka yi mata rumfa ta saya jikinta.

Yawan dariyar da suke yi Kandala ta fara tsarguwa ta shiga sababin faɗa tana cewa,

"Duk wanda ya yi mini dariyar na faɗi Allah ya sa shi ma wajen fita motar bakinsa ya karci ƙasa."

Wata sabuwar dariya matasan cikin motar suka sake kwashewa da ita, masu hankalin cikinsu kuwa suka fara nuna musu rashin dacewar abin da suke yi, amma duk da sun rage dariyar hakan bai hana ta ci gaba da faɗan ba, faɗan da fiye da rabinsa na saka mutum wata dariyar ne, da haka har suka fara jan ta da wasa tun tana ɗaure fuska har ta fara sakewa da su ana ta hira.

Hari dai alla-alla kawai take yi su sauka lafiya tun kafin Kandala ta yi wani sabon barci, hakan ya sa da ta ga ta fara gyangiɗi take kiran sunanta tana cewa,

"Inna! Inna! Kada ki yi barci mun kusa isa cikin garin fa, ki bari ki ga yanayin birnin da kyau ta yadda za ki bayar da labari."

Kandala ta yi saurin goge fuskarta tana kallon gefen titin tare da goge baki, amma duk da hakan minti biyu tsakani ta ƙara komawa wani sabon gingiɗin, haka Hari ta sha fama da ita har suka shiga cikin cikin garin. Bintoto da Kandala sai kalle-kalle suke yi yayin da motar ta shiga babbar tasha.

Mutane suka fara fitowa Hari ma ta fito aka bar Bintoto da Kandala suna tunanin yadda za su fito daga motar, Hari ta koma ta riƙo hannun Bintoto ta fito da ita, Kandala ta koma zarar idanuwa saboda a rayuwarta kaf ba ta taɓa shiga irin motar ba sai a wannan karon.

To fa! A samu wata jaruma ta fito mana da Kandala kada ta sake faɗuwa ta yi walle a shiga uku😂

Princess Dija ce✍

SHAGALALLIYA!

HADIZA D. AUTA

1k kacal, 1230094555 Access Bank Hadiza D. Auta Ibrahim. Shaidar biya 08022014771.

LAMBA SHA UKU.

Da dabara aka samu Kandala ta fito daga motar tana ɓarin jiki da sambatu kafin ta koma yi wa Allah godiya har da shafa addu'ar a fuskarta. Hari ta nemo musu ɗan baron da zai fitar da kayansu zuwa bakin tashar, bayan ya gama loda kayan suna ƙoƙarin bin bayansa; suka hankalta da Bintoto ba ta tare da su.

Kandala ta fara kuka tana kururuwar sai an nemo mata jikanyarta idan ta ɓata kuma sai masu tashar sun biya ta Bintototonta. Cikin tashin hankali Hari da wasu masu tausayi suka fara neman inda take lungu da saƙon cikin tashar ana bayanin siffarta da kalar kayan da ke jikinta.

Babu zato Hari ta hango ta a bakin shagon wata Hajiya mai abinci da ke cikin tashar. Hankalinta a kwance tana zaune saman dogon bencin Hajiyar tana ta guma lomomin shinkafa, jikin Hari yana rawa ta isa wurin tana faɗin,

"Haba 'yata, ashe kina nan kika sa hankalinmu duk ya tashi? Sai neman ki ake ta yi lungu da saƙo, to yi sauri ki gama ga Inna can tana kururuwar sai an nemo mata ke."

Bintoto tana dariya tana guma lomo ta ce mata,

"Share ta kawai Inna, don ba ta san daɗin da na zo sha ba ne shi yasa take kuka."

Hari tana tsaye kusa da ita tana dariyar yadda take guma loma sai ta ciko hannu, har ta cinye abincin da zuƙa-zuƙan naman da ke saman shinkafar tsoka ta kusa goma, tana gamawa ta je gaban mai abincin ta ajiye mata robarta tana cewa,

"Na gode miki da yawa wallahi, ni zan tafi Allah ya yi albark..."

Tana maganar ta juya da nufin tafiyarta, mai abincin ta zabura jikinta yana rawa ta miƙe, babu zato Bintoto ta ji an cafko rigarta ta ta baya, waigowar da za ta yi ta yi ido huɗu da Hajiya mai abincin tana aika mata muguwar harara, domin yanayinta ya nuna ƙiris ya rage ta kifa mata hamshaƙin mari. Bintoto ta yi saurin kai kallonta ga bayan Hari da ta ɗan yi misu nisa kaɗan, sannan ta yi saurin ƙwala mata kira tana cewa,

"Inna! Don Allah ki zo wannan ƙatuwar matar tana so ta kashe ni!"

Haushi ya sa mai abincin tsumar jidali ta ɗaga hannu ta kai mata bahagon mari tas, Bintoto ta yage baki ta fara zuba ihu iya ƙarfinta hannu biyu a ka, Hari ta yi saurin waigowa tana salati cike da mamaki ta ƙaraso wurin tana tambayar matar abin da ya faru. Sai dai kafin mai abincin ta haɗiye fushinta ta yi magana; Bintoto ta riga ta faɗin,

"Abinci take rabawa kyauta, kuma a gabana duk wanda ya ci ko godiya ba ya yi mata yake tafiyarsa, amman ni kina gani sai da na gode mata amma shi ne don ta gan ni baƙuwa za ta ce duka na za ta yi, to ai don ban san ba ta son godiyar ba ne yasin da ina gama ci zan yi gaba kamar yadda na ga wasu suna yi mata."

Ta ƙare maganar tana kallon ƙatuwar matar tana turo baki, nan take Hari ta fahimci inda zancen ya dosa tana haɗe dariyarta ta ce da mai abincin,

"Na nawa ne kika saka mata?"

Mai Abincin ta ƙara tsuke fuska tamau sannan ta gyara tsayuwarta ta ce,

"Abincin dubu ɗaya ne naman dubu biyu."

Hari ta yi saurin kai kallon ta ga fuskar Bintoto saboda mamakin wautar da ta tafka, ba tare da ta ce komai ba ta ciro kuɗin a jakarta ta miƙa mata, amman tsabar haushin da Bintoton ta ƙumsa mata; garin sakin ta sai da ta cillar da ita ta faɗi ƙasa, sannan ta fara ƙirga kuɗin tana haɗe rai daidai lokacin da Kandala ta iso wurin idonta a kan matar tana faɗin,

"Wannan ai rashin daraja ne! Kina ɗirkekiyar ƙatuwa da ke haka don lalacewa ki koma faɗa da wannan 'yar tsakon yariya? Wallahi kin ji kunya da yawa kuma ki gode wa Allah da ba garinmu kike ba da sai na la'ance ki gaba da bayanki bak'ar almura mai fuskar maza da mazaunai kamar ƙaton masak...."

Haka ta dinga cin zarafin mai abincin Hari tana jan ta tare da roƙon ta yi haƙuri saboda ganin cikin ɗan lokaci ta tara musu jama'a, amma Kandala sai da ta kai ayar

zancenta. Mai abinci kam ƙanzil ba ta ce mata ba saboda ganin ta tsohuwa, bakin aikinta kawai ta koma ba tare da ta kula da duk abin da take faɗa ba.

Hari da wasu mutanen da cikin tashar suka taru a kan Kandala ana ta ba ta haƙuri, sannan ta riƙe hannun Bintoto suka bar wurin. Amma ba ta daina tsine wa mai abincin albarka ba. Mai baro a gaba suna bin shi a baya har zuwa bakin tashar, inda Hari ta tsayar da napep suka shiga duka da kayansu suka nufi unguwar da Harin ta sanar da shi. Amma har lokacin Kandala ba ta daina sababin faɗan da take yi ba kamar ta ci babu, Hari tana dariya ta ce da ita,

"Inna fa abincin siyarwa ne Bintoto ta je ta ci, saboda ta zaci kyauta take bayarwa, shi ne fa da ta ga za ta tafi ta riƙe ta ta ce sai ta biya ta kuɗin abincinta."

Kandala ta yi saurin kai wa Bintoto ƙoso a kai sannan ta ce,

"Kaɗan daga aikinta, ke kam idan ba ki daina kwaɗayi ba sai kin ciyo wa kanki wutar lahira watarana."

Bintoto ta turo baki tana cewa,

"To ita ma tun da ta san ba na sadaka ba ne ai sai ta faɗa mini gaskiya tun kafin na ci. Amman don mugunta har da tambaya ta tsoka nawa za ta saka mini, ni ko na ce ta saka dozin kafin na cinye idan ban ƙoshi ba sai ta ƙara mini."

Hari da mai Napep suka fashe da dariya, yayin da Kandala ta yi gefe da kanta tana kallon bakin titin fuskarta a haɗe tana cewa,

"Ai da na san haka ne wallahi da na bar ta ta yi wa bakinki darzar man ƙuliƙuli, baƙar fitinanniyar yarinya! Sai gobe mu ga da wane bakin za ki je wurin kwaɗayin jarabar da kika saba."

Haka suka ci gaba da rikicin da suka saba yi a tsakaninsu, don bakin Bintoto ba ya mutuwa wajen ƙara tunzura ta, hakan ya sa ta sha kalolin faka da mangare kai

har suka isa gidan da Hari take haya ba su daina musayar yawun ba, bayan an sauke su Bintoto ta fara waige-waige fuskarta a yatsine take kallon gidajen cikin unguwar tana cewa,

"Amma dai wannan unguwar taku ta talakawan birni ce ko Inna?"

Hari ta yi murmushi kawai ba ta ce mata komai ba, kai-tsaye ta buɗe gidan da makulli sannan ta ce su fara shiga za ta sa a shigo da kayansu. Wasu yaran unguwar da ke murnar ganin ta suka riƙa mata kayan har cikin gidan suna yi mata sannu da zuwa. Cikin sakin fuska ta fito da jakar ƙolon daɗin da ta riƙo musu ta dinga raba musu, suna ta murna suka fice suna godiya. Bintoto ma sai kallon ledar take yi tana tunanin ita jakar ya dace ta ba ta, kafin ta ciro guda uku ta miƙa mata tana cewa,

"Karɓi ke ma ki sha, kafin wasu su shigo su karɓi nasu, don na san muddin yaran unguwar nan suka ji na dawo gidan nan ba zai sake zama shiru ba."

Bintoto ta karɓa tana gunguni Hari ta mayar da sauran a jakarta sannan ta buɗe ɗakinta ta fito musu da tabarma ta shimfiɗa, sai da ta shigar musu da kayansu ciki sannan ta fito da nufin fita, Kandala tana jefa goro a bakinta ta ce,

"Wai ke kam ba ki da ɗan farau-farau na ɗan kora? Wallahi maƙoshina har ciwo yake yi mini saboda jarababbiyar 'yar nan taki."

Bintoto ta yi karaf tana cewa,

"Ko saboda faɗanki da kika saba ba! Ai na so kin ci abincin ƙatuwar matar nan ki ji yadda yake da mugun daɗi, alƙur'an da haƙorin giwarki sai ya koma inda ya fito ba tare da kin sani ba, saboda kiran sallar da za ki yi ta jin ana yi miki a cikin kunnuwa tsabar daɗin miyar da tsokokin naman."

Hari ta girgiza kai kawai tana 'yar dariya sannan ta ce da Kandala,

"Ai Inna furar ce zan aikawa a siyo miki yanzu nan, don na san kin fi son ta da komai."

Bintoto ta sake karɓe zancen tana kallon Kandala ta ce,

"Ba fa komai ba Inna! Don wallahi tana cin nama da irin abincin matar can sai ta rasa inda kanta yake."

Hari ta fita tana dariya ta ce,

"To ni dai bari na bayar a siyo mata furar yanzun nan, tun da ke kin gama ƙoshi tun a tash... "

Princess Dija✍

SHAGALALLIYA!

NA HADIZA D. AUTA

Wannan shi ne fejin ƙarshe. Domin ci gaba da bibiyar littafin a biya 1k kacal ta wannan account; 9032685442 Opay Hadiza Ibrahim Ɗan Auta. Shaidar biya ta wannan lambar 08022014771.

LAMBA SHA HUƊU.

Haka Hari ta dawo da abinci mai rai da lafiya da furar Kandala, suka baje a kan tabarma suka ci suka ƙoshi, Kandala sai lasar leɓo take yi da dogon haƙorinta mai tsini saboda jin daɗin jar miya. Bintoto kuma tsabar lasar hannu har zuwa gwiwa tana rawa da kai don ita ma ba ƙaramin daɗin abincin ta ji ba, saboda takanas Hari ta saka maƙociyarta ta dafa musu abincin tun kafin su iso garin, gudun su zo suna jin yunwa a koma a neman abinci.

Da dare ma a nan suka baje tsakar gidan dukansu suka yi barci, saboda yanayin zafin da ake ciki a lokacin, bayan sun gama shan hira da matan da ke zuwa yi wa Hari barka da dawowa. Sai da sawunsu ya ɗauke hira ta koma tsakanin Hari da Kandala, a nan Hari ke sanar da ita washegari idan Allah ya kai su za ta je ta kai Bintoto gidan aikin da ta samo mata. Sannan ita ma za ta haɗa ta da matar da za ta yi wa aikatau a goben duka. Shiru kawai Kandala ta yi tana nazari kafin ta ce,

"Wai ni kam me zai hana mu yi aiki a gida ɗaya ni da Bintoton? Ni fa Hari ba na fatar duk abin da zai sa a ce na yi nisa da Bintotona gaskiya, don haka a duba dai idan akwai inda za a karɓe mu mu biyu a ɗan rakuɓa mu mu yi maneji."

Hari ta yi murmushi sannan ta ce,

"Ai Inna da ke za mu je ki ga gidan, duk lokacin da kika buƙaci ganin ta sai ki je ki dubo abarki babu wanda zai hana ki zuwa inda take."

Kandala ta taɓe baki cike da rashin jin daɗin maganar Harin sannan ta ce,

"Yanzu ba za su ɗauke mu mu yi musu aikin tare ba?"

Hari ta yi shiru sannan ta sauke ajiyar zuciya ta ce,

"A yadda na ji wata ma'aikaciyar asibiti ce Bintoto za ta dinga yi wa rainon 'yarta mai wata bakwai da haihuwa, saboda tana fita aiki kullum shi ya sa take buƙatar mai kula mata da yarinyar, don ita kaɗai ce a gidan mijinta ma ɗan kasuwa ne ba zama yake yi gidan koyaushe ba. Sannan uwar yarinyar za ta a samu nutsuwa da yin aikin gidanta cikin lokaci."

Kandala ta yi murmushi mai sauti sannan ta ce,

"Allah ya sa 'yar taki za ta yi abin da ake buƙata to, saboda ina tsoron ta je ta yi musu rashin jin da ta saba a koro ta ko'ina ba a je ba."

Hari ta yi dariya sannan ta kai kallon ta ga Bintoton ta ce,

"In sha Allahu ma za ta yi duk abin da ake so."

"Allah ya sa!"

Shi ne abinda Kandala ta iya faɗa saboda gabaɗaya jikinta ya gama mutuwa da rabuwar da za ta yi da Bintoto, Hari tana 'yar dariya ta ce,

"Amin Inna."

Da haka suka kulle hirar kowa ya yi shiru yana tunanin abin da ke ransa, Bintoto kam tun ƙarfe takwas na dare ta baje tana shaƙar barci baki buɗe, tsabar gajiya minsharinta kawai ke tashi tare da sauke numfashi kala-kala tana canza giya.

Tun da sassafe suka shirya sannan Bintoton ta ɗauki kayanta da ke ƙulle a ɗankwali suka fito. Kandala jiki babu kuzari take bin bayan Harin har suka hau adaidaitasahu zuwa unguwar da za a kai Bintoton, sai murna take yi tana ta kalle-kalle saboda mamakin manyan gidajen da ke cikin unguwar da suka zo, har suka shiga gidan idonta ba su daina waige-waige ba a zuciyarta tana murnar ita ma ta kusa zama mai kuɗi.

Kandala ma sai mamakin ganin ƙaton gidan take yi tana jinjina mulki da iko na Ubangiji tana ji kamar a mafarki ne ta hango suna shiga aljanna, musamman da ta tuna irin ginin gidajen garinsu, a take ta saka wa ranta masu gidan sun gama samun arziƙinsu tun a nan duniya sun cinye komai.

Ba ta ƙara shiga mamakin da ya tashi kashe ta ba sai da suka shiga falon gidan, a nan ne Kandala ta fara zarar ido yayin da Bintoto ke washe baki saboda farincikin ta tako arziƙi, suka zauna a ƙasan carpet d'in dake shimfiɗe tsakiyar kujerun. Kandala sai faman shafa carpet ɗin take yi tana taɓa jajayen leda seat ɗin da suka ƙara ƙawata falon, waɗanda raɓar ac ta sa suka ɗauki ni'imtaccen sanyi mai ratsa jiki. Sannan suka koma kallon Tv plasma da ke jingine jikin bangon falon tana aiki.

Kandala baki a buɗe take kallon Tv'n tana mamakin irin damben da ake ci a cikin tv kuma wai ba za a raba faɗan ba, hakan ya sa duk aka zo kai duka sai ta zabura tana faɗin,

"Mugun abu!"

Kafin ta koma faɗin,

"Wannan ƙarfi haka! Da alama dai ƙashi ɗaya ne da wannan mutumin, don Allah Hari duba mini ki gani wai mutum fiye da goma duk ya bai wa ƙasa ajiyar su. Ke kin san wannan daga ganin shi horon tuwon dawa ne."

Hari tana murmushi ta ce da ita,

"Ai shiri ne Inna, duk abin da kika gani ba gaskiya ba ne, shi ya sa ma..."

Babu shiri Kandala ta yi saurin faɗin,

"Wane shiri bayan kina ganin yadda yake fitar wa da mutane jini? duba..duba ki gani Har... Innalilahi wa inna ilaihirraji'un har da haƙori ya zubar don yana la'ananne.. kaiiiii! Subhanallah ya gama aiki wannan ai rashin imanin n...."

Sallamar wata dattijuwar mata ne ya sa suka kai kallonsu gare ta dukansu, bayan sun amsa mata ta zauna fuskarta ɗauke da murmushi ta dinga amsa gaisuwar da Harin ta fara yi mata, Kandala ma ta washe baki d dogon haƙorinta ya ƙara fitowa tana cewa,

"Hajiya sannu da fitowa, tun ɗazu muna nan muna kallon tanbaɗaɗɗen yaron can mai yi wa mutane dukan tsiya, kuma abin haushi kowa yana kallo babu mai iya rabawa."

Hajiyar sai da ta yi murmushi mai sauti sannan ta ɗauki remote ta rage muryar tv tana cey,

"Shiri ne kawai inna, amma ba da gaske dukan ake yi ba."

Kandala idonta a kan Tv ta ce,

"To kam wannan ai rashin daraja ne, wane shiri za a yi da dukan da za a fitar wa da mutane jini?"

Hari tana murmushi ta gyara zamanta sannan ta daƙile hirar cikin dabarar dafa kafaɗar Bintoto wadda ta yi nutsuwar dole tana kallo, idonta ƙurin ko ƙiftawa ba ta yi, ta ce da ita,

"'Yata ba ki gaishe da Hajiya ba."

Sai da ta a ɓata fuska cike da jin haushin Hari ta katse mata kallon, ganin sun haɗa ido da Hajiyar ta koma washe baki tana cewa,

"Sannu Hajiya!"

Hajiya ta faɗaɗa fuskarta da murmushi ta ce,

"Yawwa Umma Binta."

Bintoto ba ta ce komai ba ta mayar da kanta tana ci gaba da kallon, har da matsawa gaban tv gudun su Hari su dame ta. Hari tana 'yar dariya ta ce da Hajiyar,

"Ashe sunan tsohuwa ne da ita?"

Hajiyar tana murmushi ta amsa mata da cewa,

"Sunan ƙanwar mahaifiyata ne, kuma a hannunta na tashi har na yi aure shi ya sa duk inda na ji sunan ba na wasa ina girmama shi sosai gaskiya."

Cike da jin dadi Kandala ta washe baki ta ce,

"Ai suna ne mai daraja tun asali, saboda ɗiyar Ma'aikin Allah guda ce babu tamkar ta a duniya."

Hajiya tana murmushi ta ce,

"Haka ne tabbas Allah ya ba mu albarkacin masu daraja!"

Dukansu suka ce amin, kafin Hari ta ɗan muskuta sannan ta ce,

"To Hajiya ga Inna Kandala nan ita ce kakarta, mai sunan tsohuwar kuma ita ce wadda kika ce na samo miki."

Hajiyar ta kai kallon ta ga Bintoto sannan ta yi 'yar dariya ta ce,

"Ta yi sosai, duk da cewa ina ganin kamar za ta yi ƙanƙanta da raino, don na fahimci da wuya idan za ta mayar da hankali a kan abin da ake so ta y...."

Kandala ta yi caraf da zancen tana cewa,

"Za ta iya kuwa! Don tana son yara sosai ko a garinmu tana ɗaukar 'ya'yan maƙota, kuma da ƙyar ake karɓar su hannunta idan ta goya su har barci suke yi a bayanta."

Hajiyar ta yi murmushi sannan ta ce,

"To ya yi babu damuwa, bari direba ya zo ya kai ta gidan da za ta yi aikin, an yi sa'a ma yau matar gidan tana gida ba ta fita wurin aikin ba."

Kandala ta yi saurin haɗiye wasu yawu muƙut sannan ta ce,

"Amma da ni za a je na ga gidan duk lokacin da na tashi ganin ta sai na je, duk da na so a ce ni ma akwai aikin da zan yi a can sai mu zauna tare da ita, ko kuma a bar mu nan gidan ni da ita mu yi wani aikin kamar sai ya fi da a kai ta wani gida daban."

Hajiyar ta yi 'yar dariyar manya saboda ta gano ba ta son rabuwa da ita ne kawai, cikin murmushi ta ce da ita,

"Ki yi haƙuri Inna, ai can ɗin ma gida ne za ta je saboda matar yaron gidan nan ne za ta yi wa aikin."

Kandala ta yi shiru kawai ba don ta so ba, haka aka tsadance kuɗin aikin kowa ya amince. Hajiyar ta miƙe tana kiran wata 'yar aikinta, jikinta yana rawa ta rusuna ta gaishe da su Hari kafin ta mayar da hankali a kan Hajiyar. Kai-tsaye ta ce ta je da su wurin direban gidan ya kai su gidan Hamida.

Sannan ta wuce ciki bayan ta ce su jira ta, mintuna a tsakani ta dawo da wata leda da kuɗi a hannunta ta miƙa wa Hari suka yi sallama. Hari ta ɗaga Bintoto sama tare da jan hannunta gudun ta tsaya magana ta kunyata su a gaban Hajiya. Don ƙaramin aikinta ne ta ce ba za ta je ba sai ta gama kallo. Har suka fita falon Bintoto ba ta daina waigen Tv ba, duk da jan da Hari take yi wa hannunta, don ta san muddin aka biye ta ba fitar za ta yi ba.

Da sauran kallo. Yanzu ma aka fara.

Domin ci gaba da karanta littafin Shagalalliya ku biya kuɗinku ku more karatunku mai cike da zallar nishaɗi.

Princess Dija✍

* SHAGALALLIYA!*

NA HADIZA D AUTA

1 kacal, 1230094555 Access Bank Hadiza D. Auta Ibrahim. Shaidar biya ta wannan lambar 08022014771.

LAMBA SHA BIYAR.

A wannan karon sun shiga motar lafiya ba tare da ƙauyanci ba, amman wajen rufe ƙofar sai da aka rufe wa Kandala tana rufe ido tare da janye fuskarta gudun tsautsayi ya sa garin rufewa a buge mata fuska.

Tun da suka shiga unguwar su Hamidar kallon su ya koma sama, saboda ganin dogayen gidaje masu benaye hawa-hawa gwanin burgewa. Domin kafatanin unguwar ta masu kuɗi ce sai tsilla-tsilla da za a kira masu dama-dama, amma unguwar ta yi fice da sunan manyan masu kuɗi waɗanda suka ci suka ƙoshi. Domin ko a tsarin gidajen za a fahimci sai wane da wane ne a cikin ta.

Har bakin ƙofar gidan aka ajiye su suka fito Kandala da Bintoton suna ƙara ware idanuwa suna ta kallo, don ko Hari da ta goge da zama cikin 'yan birni ba ta ɗauke idanuwanta daga kallon gidan ba. 'Yar aikin Hajiya ta yi musu jagora har cikin gidan zuwa wani ƙaton falo irin na alfarma, ƙamshin da ya mamaye hancinsu ya sa dukansu suka ja numfashi. Saboda falon ya tsaru ta ko'ina ƙalƙal tamkar ba a rayuwa a cikin sa, bayan sun zazzauna ƙasa 'yar aikin Hajiya ta yi ciki ta bar su, mintuna a tsakani suka fara jin kukan ƙaramar yarinya yana doso falon.

Sai ga wata matashiyar mace mai kimanin shekara ashirin da biyar ta fito saɓe da 'yarta a kafaɗa tana girgiza ta saboda azabbaen kukan da take yi, tare da 'yar aikin suka ƙaraso falon fuskarta a washe ta zauna tana gaishe su, Bintoto ta bi ta da kallo cike da burgewa saboda ganin ta fes da ita waton 'yar gayun gaske, sannan ga ta ma sha Allah babu makusa, duk da cewa ba ta cika manyan kyau ba amma babu muni a fuskarta. Bugu da ƙari gayunta ya sa ta zama wata kalar tauraruwa a idanuwan su Bintoto.

Hamida tana ci gaba da girgizar 'yarta ta ce da su,

"Yanzu Hajiya take sanar da ni za ku zo!"

Hari ta gyara zamanta ta ce,

"E, Haka ne."

Sannan ta kalli Bintoto ta sake cewa,

"Ga wadda za ta taimaka miki da rainon yarinyar, duk da cewa kin sani amma yana da kyau a ƙara yi miki bayani...yawwa Bintoto je ki karɓi 'yar taku ki gani don na san za ta daina kukan idan ta gano ke ce kika ɗauke ta."

Ta ƙare maganar tare da kallon Bintoton tana dariya cike da umarni a kallonta, Bintoto ta miƙe cikin zumuɗi ta karɓe yarinyar ta ɗora ta a bayanta da nufin goya ta, sai ga yarinya tana shirin faɗowa saboda zilliyar da take yi. Hakan ya jawo hantar Hari da Kandala kaɗawa, saboda tsoron ta kayar da ɗiyar mutane su shiga uku, amma cikin sa'a ta goya ta sannan ta kalli Hamidar ta ce,

"Ɗauko zani na saka sai goyon ya fi daɗi."

Hamida tana dariya ta miƙe cike da jin daɗi ta yi ciki mintuna a tsakani ta fito da zanin ta miƙa wa Bintoto. Bakinta a washe ta karɓa ta goye yarinyar tsantsan sannan ta fara bubbuga duwawunta tana yawo, kamar almara yarinya ta yi shiru saboda ta ji daɗin goyon,kuma daman shi take buƙata ba ta samu ba. Don Hamida ba ta son goya ta, sai kullum tana saɓe a kafaɗa shi ya sa wani lokaci take damun ta da rigima, musamman idan tana jin barci.

Mintuna a tsakani yarinya ta shiga sauke numfashi da ajiyar zuciya tsabar jin daɗin goyon da kukan da tasha, hakan ya faranta wa kowa rai saboda ganin Bintoton ta fara sanin kan aikinta. Hari ta bai wa Hamida haƙuri a kan zaman da za ta yi da Bintoton, sannan ta ƙara nuna mata cewa yarinya ce sai ana yi ana nuna mata hanya idan ta yi laifi. Hamida ta ɗauki amanar Bintoto da kyau saboda jin daɗin kulawar da ta fara yi wa 'yarta cike da burin faranta mata ita ma. Da haka ta yi musu alheri suka yi sallama da ita ta rako su har bakin gate, Kandala tana share

ƙwalla ganin Bintoto tana yi mata bye-bye, cike da farincikin za ta zauna gidan 'yan gayu ita ma ta zama mai kuɗi.

Hari da 'yar aikin duka suka shiga mota amman Kandala tsaye take jikin motar tana kuka, ganin hakan ya sa Bintoto ta zo wurinta tare da yi mata raɗa a kunne tana cewa,

"Kin ga gidan masu kuɗi ne ni ma kuɗin zan yi na kai ki makka Kandala, don haka ki yi haƙuri ki tafi don ALLAH tun kafin ki jawo matar ta ce ta fasa son aikin na shiga uku."

Kandala ta dungure mata kai cike da takaici ta juya tana ƙoƙarin shiga motar tana kuka, Bintoto ta turo baki cike da jin haushi ta sake cewa,

"Ni dai don Allah ki daina kukan nan Kandala sai ka ce an ce da mun rabu mutuwa zan yi? "

Takaici ya ƙara rufe Kandala ta yi banza da ita tana ci gaba da goge ruwan hawayenta, Bintoto ta rufe mata ƙofar bayan ta shige cikin gidan tana wasar baki ta ce,

"Sai watarana Kandalata! Inna sai kun ƙara zuwa gani na..."

Hari tana ɗaga mata hannu direban ya ja motar suka tafi, hakan ya janyo Kandala ta fashe da wani sabon kuka mai sauti iya ƙarfinta tana faɗin,

"Wayyo kaina shikenan an raba ni da Bintoto!"

Hari tana ba ta haƙuri suka kama titi, Bintoto kam hankalinta a kasance ta bi Hamida suka koma cikin gidan goye da yarinyar, wadda har lokacin ba ta daina ajiyar zuciya a cikin barcin ba, bayan sun koma falon ta kalli Hamidar tana cewa,

"Wannan abin naki shi baya magana ne? Na ga a can gidan da muka fito nasu har dambacewa ake yi muna ta shan kallo."

Bayaninta ya sa Hamida ta fahimci abin take nufi da zancen, tana 'yar dariya ta nufi Tv ta kunna mata tashar Arewa 24, sannan ta juyo tana cewa da ita,

"Zo mu je ki ga masaukin ki sannan ki dawo ki ci gaba da kallon."

Idon Bintoto a kan Tv ta ce,

"Laaa! Ashe har da Hausa abun yana yi na ji kamar ita ce ake yi fa! Don Allah bar ni na gani kar kafin mu dawo su ɗauke maganarsu."

Hamida ta ɗauki remote ta ƙara volume kawai sannan ta zauna tana dariyar shirmenta don ta fahimci tana da abubuwan ban dariya da yawa, saboda muryar kaɗan take fita, amma don ta ji daɗin kallon kawai ta ƙara mata. Kamar haɗin baki aka fara waƙar makullin zuciya, daɗin waƙar ya sa Bintoto ta fara cashewa a gaban Tv tana kwaikwayon yadda ta ga masu rawar suna yi. Hamida sai faman cin dariya take yi saboda yadda take ta wata malƙwasar jiki tana karya wuya. Da shauƙin waƙar ya ɗebe ta ta murɗe ƙafafuwa garin koyon rawar Zee pretty inda take harba ƙafa ɗaya baya, kawai sai ga Bintoto ta yi bayan duka ta faɗi babu shiri ta taushe yarinya, kafin kace me yarinya ta tsala ihun kuka na tashin hankali. A zabure Hamida ta yi kansu ta karɓe yarinyar ranta a ɓace ta fara duba jikinta tana shafa kanta, don gefen teburin tsakiyar falon da suka faɗa kansa ya buge mata kai. Wanda cikin ɗan lokaci wurin ya haye ya yi ƙaton ƙololo, ga jikin yaro ba taushi da kuma tsautsayi ya afka tun a tashin farko.

Har an fara wasar ashe😳😂

Princess Dija ce✍

SHAGALLIYA

16.

Ganin ƙololon da ke kan yarinyar ya sa Bintoto tsurewa ta shiga zarar ido bayan ta ɗora hannu aka tana cizon yatsa. Hamida ta shiga murza wurin daidai lokacin da suka jiyo gunjin mota alamun maigidan ne ya dawo. A zabure ta miƙe jikinta yana rawa ta yi ɗakinta da sasssarfa, ganin wurin har ya fashe jini ya fito. A nan ta bar Bintoto tsaye tamkar an dasa ta tsabar sanyin da jikinta ya yi, amma hakan bai hana ta sake bin wata waƙar da aka saki ba, har da gwada yadda ake yin rawar tamkar ba ta aikata komai ba.

Yana shigowa falon ya yi ido biyu da Bintoto a tsaye tana wara hannuwa har da juyi bakinta yana muimui saboda bin waƙar da take yi. Cike da mamaki ya zagaya ta bayan kujeru ya shigo cikin falon, bayan ya gama kallon ta tsawon mintuna riƙe da ƙugu ko ƙiftawa ba ya yi. Ganin ta gan shi har sun haɗa ido amma ba ta daina rawar ba, ballantana ya samu arziƙin gaisuwa ko ta nutsu. A harzuƙe ya bi gefenta tamkar ya kai mata duka ya kashe socket ɗin sannan ya ciire wayoyin yana kumbura ya nufi wurin Hamida, saboda jiyo sautin kukan yarinyar yana tashi babu ƙaƙƙautawa.

Ransa a ɓace ya faɗa ɗakin idonsa a kan yarinyar da Hamida ke ƙoƙarin goge mata jinin da tissue, takaicin jin kukan da yarinyar take ta tsalawa ya ƙara ƙona masa rai. Hakan ya sa ya rufe ta da faɗan da ya saba ta inda yake shiga ba a nan yake fita ba. Domin tun kafin ya ji dalilin kukan ya fisge yarinyar daga hannunta yana nanacin ya gaji da sakacin da take yi wa rainon yarinyar. Cike da fargaba ta fara magana cikin sanyin muryarta da tunanin za ta fita idan ta sanar da shi gaskiya.

"Don Allah ka yi haƙur...wallahi tsautsayi ne kawai ya jawo ta ƙwale da table ɗin falo, amma dukanmu ba mu san hakan za ta faruwa b.."

"Dukanku ke da wa?"

Sai da ta haɗiye yawun firgicin da take ciki sannan ta ce, "Ni da wadda ta ƙwale ta ba da gangan b.."

Wani mugun kallon da ya wurga mata fuskarsa a cure ya sa ta haɗiye sauran maganar da ke cikin bakinta. Fuskarsa a cure ya saɓa yarinyar a kafaɗa sannan ya nuna ta da ɗan yatsa cike da gargaɗi ya yi magana cikin kaushinn murya ya ce,

"Ta bar gidan nan kafin na dawo! idan kuma na tarar da ita hatta ke sai na nuna miki asalin wane ne ni!"

Yana gama maganar ya fice daga ɗakin, ransa a ɓace ya fice gidan ko kallon inda Bintoton take bai yi ba ballantana ya bi ta kan kumburin da take yi saboda jin haushin kashe kallon da ya yi, sannan da mugun kallon da take wurga masa riƙe da ƙugunta tun a lokacin da ya fito har zuwa fitarsa cikin falon.

Shiru ya ratsa tsakani bayan fitarsa gidan, daga Hamida har Bintoto babu wanda ya yi motsin kirki. Sautin kiran da aka yi wa Hamida ya ja hankalin Bintoto zuwa inda wayar take, cikin sauri ta isa wurin cike da farin ciki ta rarumi wayar ta shiga juya ta har Hamida ta fito daga ɗaki ta karɓi wayar a lokaci ɗaya ta karɓi kiran, bayan ta gama sauraron abin da ya faɗa ta sauke ajiyar zuciya, da guntun hawaye maƙale a idonta ta kafe Bintoto da kallo tana nazarin mafita. Saboda maigidan ne ya kira yana jaddada mata Bintoto ta bar gidan kamar yadda ya faɗa tun kafin ya dawo.

"Ke kam kin fi mijinki hali mai kyau. Dubi ki gani kallon da kika kunna mini ma yana shigowa ya kashe shi."

Zancen Bintoto kenan tana kallon Hamida da ko ƙiftawa ba ta yi. Hakan ya bai wa Hamida damar yin magana cikin sanyin jiki ta jawo wayarta ta kira Hajiya. Ringing biyu ta ɗauka suka sake sabuwar gaisuwa kafin ta sanar da ita abin da faru. Saboda har cikin ranta Hamida Bintoton ta kwanta mata, don zuciyarta ta tabbatar mata tsautsayi ne kawai ya jawo ta buge yarinyar ba da gayya ba. Hajiyar ma ba ta goyi bayan barin Bintoto gidan ba, domin kai-tsaye ta ce ta bar ta da shi za ta kira shi a waya.

Bayan ta sauke wayar ta miƙa kallon ta ga Bintoto da ta gama sakin baki tana sauraron abin da suke tattaunawa, a zuciyarta tana faɗin,

'Kambu! Ai wallahi babu ta yadda za a yi na bar gidan nan ni kam. Ya dai yi haƙuri ko Kandala ta ce haƙuri take yi da ni ba don tana son halina ba.'

Amma a fili ta ɓata fuska bayan ta cire tagumi ta isa gaban Hamida ta kai gwiwa ƙasa tamkar mai neman gafara tana cewa,

"Ni dai don Allah ki ƙyale mijinki ki sake kunna mini kallon kada su ɗauke waƙoƙinsu."

Wani kallo Hamida ta yi mata babu shiri ta saki 'yar dariya sannan ta ce, "Waton ke ta kallo ma kike yi ba ki damu da an ce ki bar gidan ba?"

"Ai ke ba za ki raba ni da gidan nan ba, don Allah ma ya sani ban so yarinyar ta ƙwale kanta ba saboda Allah ma ya sani har na fi shi son ta."

Miƙewa Hamida ta yi tana faɗin, "Sai ki ba shi haƙuri idan ya dawo na san zai haƙura. Amma ki kiyaye gudun matsalar ta sake faruwa."

Tana faɗar haka ta shige kitchen, Bintoto ta taɓe baki cikin murya ƙasa ta ce,

"Ai wallahi ni ko sai dai ya mutu idan aka ce sai na ba shi haƙur...hu'um! Kuma ni wallahi ba zan bar gidan ba sai dai ya kashe n..."

Zumbur ta miƙe jikinta yana rawa ta taryi gaban Hamida. Saboda ganin ta da plate shaƙe da shinkafa da miya har da kifi a sama. Bakinta a washe ta miƙa hannu tana cewa,

"Don Allah kawo na kai miki inda kike so kada ki wahala."

Hamida tana 'yar dariya ta sakar mata plate ɗin tana faɗin, "Naki ne ai, ki je ki ci zan shiga wanka kafin ya dawo mu ga yadda za a yi."

Bintoto baki har kunne ta karɓe plate ɗin, har da 'yar rawarta ta isa tsakiyar falon ta zauna saman carpet tana waƙe-waƙenta tana zuba loma. Don cire cakalin da ke ciki ta yi ta tsoma hannunta kamar yadda ta saba. A haka maigidan ya dawo gidan ɗauke da yarinyar, yana ido biyu da Bintoto dumu-dumu da abinci ya watsa mata muguwar harara ya wuce fuu zuwa ɗakinsa.

Mintuna a tsakani Hamida ta fito daga wankan da ta shiga ta yi ɗakinsa. Inda ta tarar da yarinyar a kan gadonsa sharkaf tana barci har da sauke ajiyar zuciya wata bayan wata. Cikin sanyin jiki ta fara magana a tsorace tana cewa,

"Don Allah ka yi haƙuri yarinyar can ta zauna Baban Baby. Saboda 'yar aikin da Hajiya ta kawo mana ce domin ta kula mana da Baby. Kuma ka sani idan aka kore ta ba za ta ji daɗi b..."

"Yar aiki ko mahaukaciya kamun yunwa? To bari ki ji; zan bar ta zauna kamar yadda Hajiya take so, amma daga yau kada ta sake taɓa Baby a cikin gidan nan! Domin ko 'yar'uwarki ce idan ba ta da hankalin da zan zuba ido na bar ta ta yi rainon Baby, ko a gabanmu ballantana a bayan idanuwanmu. Saboda ita kanta rainon take nema a yi mata, ta ya ya za ta iya rainon Baby? Haka kawai ta je ta kashe mana ita a banza. Ko so kike yi mu saka kuɗinmu mu sayo abin da zai jaza mana bala'i da hannunmu?"

Ya ƙare maganar a harzuƙe tamkar ya rufe ta da duka, baya ta ja cike da tsoro, duk da ta saba da halinsa jikinta yana rawa ta ce,

"Tsautsayi ne kawai amma ba za ta sake ba Baban Bab...."

Yi mini shiru ba na buƙatar wata kariya daga bakinki! Idan ma tsautsayin ne a kanta zai ƙare ba a kan Baby ba. Idan ta kuskura ta sake kuma za ki ga abin da zai faru."

Yana gama faɗar hakan ya shige toilet ya bar ta tsaye tana jimamin abin. A hankali ta fito daga ɗakin tare da ja masa ƙofa cikin sanyin jiki. Tana juyawa ta ga Bintoto tsaye a kofar ɗakin tana lasar plate da harshenta. Cikin rawar baki Hamida ta isa wurin tana cewa,

"Me kike yi a nan?"

Bintotona ta maƙale plate ɗin a hamatanta tana murza maiƙon miyar da hannuwanta tana faɗin,

"Sauraro na tsaya yi na ji idan za ki rama faɗan da yake yi miki, ko kuma za ki bar shi ya yi zaton tsoron sa kike ji. Ai ina ganin ki ɗazu har da hawaye kika yi a kan ya yi miki faɗa. To wallahi ki saki jiki ku daku kawai, idan ya ɗibi naman dafuwa ke ma ki ɗibi na gashi sai kowa ya ji a jikinsa. Amma haka kawai kina kallo yana ta miki masifa ke ba za ki iya ramawa b"

To fa□□

Princess Dija ✍

17.

Hamida tana ƙoƙarin yin magana riƙe baki tsabar mamakin da Bintoton ta ba ta, ya buɗe ƙofar ɗakin ya fito idonsa a kan Bintoto ya ce,

"To ibilishiya! Ashe bayan haukar har da haɗin gurmin bala'i kike yi...to ba a gidana b..."

Yana maganar ya fisgo ta tana tirjiya da faɗin ya sake ta, a haka ya dinga jan ta har suka fice harabar gidan, Hamida tana bin su baya dariya fal cikinta ganin yadda Bintoton take tirjiya da ƙoƙarin ƙwace kanta amma babu dama, saboda ƙarfi ba ɗaya ba. Sai da ta ga ya buɗe gate ya wurgar da ita ƙofar gidan ya rufe ƙofa; sannan ta haɗe fuska cikin magiya tana cewa,

"Don Allah Baban Baby ka bar ta mu zauna, ni wallahi shirmenta ma dariya yake saka n..."

"Dariya ko? To wannan idan ta sha ruwan birni ta goge Allah kaɗai ya san bala'in da za ta tafka wa mutane. Amma tun da dariya take ba ki ki ɗauki shawarar da ta ba ki mu daku ni da ke ɗin, kamar yadda ta ce."

Tana rufe baki tsabar dariyar da ke taso mata ta ce, "Allah ya kiyaye wannan rana Baban Baby. Ita ma kamar shirme ne kawai da ya yi mata yawa ta yi wannan maganar, sannan da ƙarancin shekarunta ba ta fahimci mene ne aure da girman miji ba. Amma don Allah ka yi haƙuri saboda har zuciyata yarinyar ta kwanta mini, ina son mutum mai barkwanci saboda nishaɗi."

Da waɗannan maganganun ta rage girman fushin da Bintoto ta saka shi. Amma bai buɗe gidan ba ya yi cikin gida yana faɗin,

"Ki bar ta sai ta horu ko za ta dawo cikin gidan nan."

Ya shigewarsa ya bar ta tsaye tana sauraron dukan ƙofar da Bintoton take yi tare da magiyar da ta ƙara saka Hamida dariya har da hawaye.

"Don Allah Alhaji ka buɗe mini albarkacin uwata da ta rasu aka binne ta cikin ƙasa da ice, sannan aka lulluɓe ta da ganye. Ka yafe mini ba zan sake ba ko don albarkacin haƙorin Kandala mai kama da na giwa. Wallahi na yarda idan na sake ka saka wuƙa ka yanka wuyana ka sha jinina idan ya fit....amma gidan nan idan aka raba ni da shi an cuce ni wallahi, saboda matar gidan ta iya miyar shinkafa da soya kifi. Wayyo don Allah ka buɗe mini ga kare can yana kallo na..wayyo Allahna!"

Ta ƙwalla ƙara sanadin hango wani baƙin karen maƙotansu ya nufo inda take gadan-gadan yana zaro harshe. Hamida da ke leƙenta ta ramin ƙofar gate dariya take yi har da riƙe ciki. Musamman da Bintoto ta haye saman gate ɗin nasu ta maƙale, karen kuma yana ta haushi da tsallen son kamo ƙafarta tana kai masa harbi a kai yana kaucewa. Ga idonta a zare cikin matsanancin tsoro take ta kwarara ihun faɗin,

"Wayyo uwata wayyo ubana! Kandala! Kandala ki zo kare zai kashe ni!"

Da gudu Hamida ta koma cikin gidan tana sanar da shi ya zo ga black can zai haukata ɗiyar mutane. Duk da haushin ta da ke ransa cikin sauri ya fito ya buɗe gidan saboda karen har cizo yana yi. Sai da ya kora shi ya bar ƙofar gidan sannan ya koma tunanin yadda aka yi Bintoto ta haye gate ɗalam har da maƙalewa. Ƙugu ya riƙe fuskarsa a haɗe ya ce mata,

"Sauko Hajiya kada ki ɓalla mini gate. Kuma daga yau idan kika sake saka guntun bakinki a cikin harkar gidana da shi zan haɗa ki ya yagalgala namanki ki mutu kowa ya huta. Don na gano ba Allah kika sani ba ballantana ki ji tsoron saɓa masa."

Bintoto ta shiga rantsuwa har da ɗaga yatsan hannu sama bayan ta lasa yawu alamun ta yi ƙarshen rantsuwa tana cewa,

"Allah yana gani na yarda idan na sake ka kashe ni."

Kumshe da dariya ya yi, sannan ya yi yunkurin komawa cikin gidan alamun bai yafen ba, kasancewar kafafuwan Bintoton sun yi sanyi kuma ba za ta iya dira ba akwai tazara. Bakinta yana rawa ta ce,

"Don Allah don Muhammadul Aminu ku saukar da ni!"

Kansa ya daga yana kallon ta ya ce,

"Sauko da kanki, ai lokacin da kika hau babu wanda ya dora ki."

Idonta ya raina fata ta shiga rantsuwar ita ma ba ta san ta hau ba, wataƙila aljanun Kandala ne suka taimaka mata amma ba ita ce ta hau da kanta ba. Da maganar ido Hamida ta roƙe shi a kan ya bari ta sauko da ita saboda ta fara kuka, hakan ya sa ya yi cikin gidan ya bar su cikin dabara ta taimaka mata ta sauko tana dingisa kafa suka koma cikin gidan, sai matsar kwalla take yi tana shessheka.

Kai-tsaye wani karamin daki Hamida ta kai ta sannan ta tabbatar mata da shi ne dakinta, bayan ta zaunar da ita a kan katuwar katifar da ke shimfiɗe mai kamar gado.

Bintoto baki har kunne ta shiga kallon dakin tana shafa gwiwar hannunta da ta gurje yayin hawa gate. Ranta fes ta yi magana cike da jin dadi ta ce,

"Yanzu a nan zan dinga kwana?"

Hamida ta daga mata kai tana murmushi ta ce, "Ta so ma na nuna miki yadda za ki yi amfani da toilet."

Bakin Bintoto a sake ta ce, "Mene ne tulit?"

Sai a lokacin Hamida ta tuna wace ce Bintoto ta ce, "Bayi nake nufi ai kin gane ko?"

Ta yi hanzarin ɗaga mata kai sannan ta bi bayanta har zuwa toilet ɗin, cike da mamaki take ta kallon Hamida da ke bayanin yadda za ta yi wanka da kashi, idan ta gama kuma da abin da za ta aikata. Tagumi Bintoto ta yi tana kallon kwalbar kashi ta ce,

"Yanzu shi wannan abin a kansa ake yin kashin?"

Hamida ta ɗaga mata kai, Bintoto ta sake cewa, "Daman ku a zaune kuke yin kashi a garin nan naku na 'yan birni?"

A nan ma ta sake ɗaga mata kai da murmushi a kan fuskarta ta kunna shower sai ga ruwa shaa yana sauka. Bintoto ta zabura tana ƙoƙarin ficewa cike da tsoro saboda ganin ruwan kamar almara. Idonta a kan shower ta yi hanzarin faɗin,

"Laa'ilaa! Ku kam dai kun ji daɗinku, har da ruwan sama kuna da kuɗin saya mala'ikun ruwa su yi ta zubo muku a lokacin da kuke so?"

Babu shiri wata ƙaƙƙarfar dariya ta suɓuce wa Hamida kafin ta ce, "Ba ruwan sama ba ne Fatima, daga ƙasa ake jawowa, shi ya sa ake yin amfani da shi a duk lokacin da ake so. Ai ke ma kuna da Bohol a garinku ko?"

Bintoto ta ɗaga kai, Hamida ta ce,

"To kamar haka ne ake zuƙo ruwan daga ƙasa ta hanyoyi da dama domin amfanin al'umma. Haka ma rijiya ai kin san ita ma daga ƙasa ruwan yake fitowa ko?"

Bintoto ta ɗaga kai, tana 'yar dariya ta ce, "Don Allah ɗan sake kunna mini na ga kalar ruwan."

Hamida tana kunnawa ta zura hannunta ta taɓo ruwan da sauri ta jaye hannun tana lasa ruwan tana 'yar dariya ta ce,

"Ashe ruwan ma bai da maiƙo."

Ta sake kai hannunta ta ɗebo ruwan ta kai bakinta tana sha ta ce, "Aradun Allah ruwan nan sun fi na garinmu daɗi."

A haka ta tara hannuwanta biyu a ruwan yana sauka tana zuƙa sai da ta ƙoshi sannan ta shafa ciki ta ce,

"Gaskiya ni ma idan na yi kuɗi sai na saka wa Kandala wannan ƙarfen a cikin ɗakinta. Da ta tashi son ruwa ta buɗa kawai ta ɗiba Kawu Mani ya daina yi mata jan rai idan ta ce ya ɗebo mata ruwa."

Hamida tana dariya ta ce, "Ai da ruwan famfo kawai ake yin amfani wannan a bayi yake na wanka ne kawai...zo mu je ki ga sauran abubuwan da ya dace ki sani kada ki tafka wauta ki ce don ba a nuna miki ba."

"Cabɗijam! Ku kam kun samu duniyarku ni ma Allah ya ba ni na rama wulaƙancin da Kulu take yi mini don ta ga ban tafi Makka ba. Amma na san dole idan ta gan ni da haƙorin Makka a bakina ta ce mini Hajiya"

Haka ta yi ta zuba wa Hamida surutu tana nuna mata tsarin gidan da jera mata abubuwan da ba a so ta yi gudun ta sake jawo fushin maigidan. Har ta gama nuna mata Bintoto ba ta daina hangen ayaba da lemun da ta hango a cikin wani ƙaramin firij ba. Tana ganin Hamida ta shige ɗaki bayan ta ce ita ma ta je ta yi wanka ta yi sallah. Zumbur Bintoto ta miƙe saɗaf-saɗaf ta koma inda ta ga firij ɗin ta jawo a hankali ya buɗe, nan take sanyi ya daki fuskarta ta fara lumshe ido tana zuƙo numfashi tana faɗin,

"Wayyo daɗi gidan 'yangayu."

Ta zura hannu ta ciro ayaba ƙwara guda ta fara ci tana lumshe ido har da bubbuga kai sanyi yana ratsa bakinta, motsin buɗe ƙofar da ta ji alamun za a fito ya sa ta yi hanzarin cinye sauran ayabar ta wurgar da ɓawo. A bisa tsautsayi maigidan yana taka ƙafarsa saman ayabar cikin rashin sani santsin ayabar ya ja shi, babu zato sai ga shi tim a ƙasan tayis.

Princess Dija✍.

18.

Waige-waige ya shiga yi cike da jin kunyar faɗuwar, bayan ya tabbatar da babu kowa a wurin ya miƙe cike da jarumta yana riƙe ƙugu, fuskarsa a cure ya dinga wara ido don zuciyarsa ta ba shi aikin Bintoto ne, saboda ba halin Hamida ba ne kuma a tarihin zaman da yake yi da ita tun tana amarya har lokacin ba ta ajiye abu inda ba muhallinsa ba. Don mace ce mai tsananin tsafta da ƙoƙarin kauce wa abin da ta san ba ya so. Amma hakan bai hana shi ƙwala mata kira har sau uku a jere ba.

Kafin ya koma ƙare wa falon kallo a tsanake, caraf idanuwansa suka hango firij ɗin da Bintoto ta buɗe a wangale har lokacin, wanda ke ajiye a wata kusurwar da ke kai mutum kitchen ko hanyar ficewa ta bayan ɗakunan gidan.

Domin ita tana ganin aika-aikar da ta tafka kafin hankalinsa ya kai kanta ta yi bayan firij ɗin ta lafe tare da shan jinin jikinta ƙirjinta yana bugawa fat-fat.

A take zuciyarsa ta ba shi tana wurin, cike da tabbatacin ita ce mai aikin, amma hakan bai sa ya nufi wurin ba saboda bai san wane kalar duka zai yi mata idan ya damƙo ta.

Hankalin Hamida a tashe ta fito idonta a kansa fuskarta cike da tambayar abin da ya faru, tun kafin ta isa inda yake ta tsaya. Babu zato ita ma ta jefa ƙafarta saman sauran ayabar santsinta ya ja ta ta tafi luu, sai dai kafin ta faɗi ya tallafo ta tana salati ya miƙar da ita gefe ransa a ɓace, tana ƙoƙarin yin magana ya riga ta da cewa,

"Mahaukaciyar yarinyar can nake so ki fito mini da ita a inda ta ɓoye!"

Hamida ta waiga hanyar ƙofar ɗakin Bintoton tana cewa, "Tana ɗakinta bari na kira t..."

Ƙarar wayarsa ta katse masa maganar da ya yi niyyar yi, cikin sauri ta bar wurin yana magana. Babu jimawa ya yi sallama da mai kiran nasa wanda ya yi daidai da fitowar Hamida daga ɗakin Bintoton. Sai dai tun kafin ta ƙaraso ya bar wurin cikin sauri yana cewa,

"Ki haɗa mini jakata kafin na dawo wata tafiyar gaggawa ce ta kama n.."

Yana maganar yana tafiya har ya fice da sassarfa bai bi ta kan Bintoto ba, ballantana ya zaƙulo ta daga maɓoyar ya yi mata kalar hukuncin da zuciyarsa ta gama yankewa a kanta. Cikin sanyin jiki Hamida ta ɗauke ɓawon ta jefa kwandon shara, sannan ta nemo mopper ta goge wurin jikinta yana rawa ta rufe firij ɗin ta faɗa ɗakinsa da ɗan gudunta, cike da fargaban kada ya dawo ba ta gama aikin da ya saka ta ba.

Bintoto da ke bayan firij ɗin zafinsa ya gama ɗumama jikinta har ta yi gumi tsabar dunƙular da ta yi. Ganin babu kowa ta fito cikin sauri ta ƙara buɗe firij ɗin ta zura kanta ta zuƙo numfashi. Kukan Baby da ta ji ya sa ta yi hanzarin katse ayaba biyu, ta ɗauki lemu ɗaya da apple ta rungume a jikinta, kafin ta rufe firij ɗin da ƙafa ta bar wurin jikinta yana rawa ta koma ɗakinta. Zaman dirsham ta yi tana 'yan waƙe-waƙenta ta fara cire fatar lemu tana faɗin,

"Su dai har da lemunsu na 'yangayu ne. Ji fatarsa babu ƙarfi har jira take yi na jawo ta biyo ni."

Da santi kala-kala ta cinye ayabar har apple sannan ta koma lasar baki a ranta tana faɗin,

'Ko dai na koma na ƙaro wai!'

Zumbur ta miƙe cikin sauri ta fice ɗakin ta leƙo kanta tare da yin ƙasake domin ta tabbatar daga ina take jin sautin kukan Baby. Kamar haɗin baki ta jiyo muryar Maigidan da sautin Hamida suna magana a cikin falo. Baki ta turo tare da aika wa cikin falon harara sannan ta ja guntun tsaki ta koma ɗakint tana dube-dube, a ranta tana faɗin,

"Wannan gida kamar a aljanna wallahi. Ni da ma an bar ni gidan nan har sai na mutu a jingine gawata jikin wancan abin mai sanyi, ina so ya yi ta hura mini iska mai daɗi."

Da ire-iren waɗannan tunane-tunanen nata na shirme ta faɗa toilet. Cike da karambani ta kunna shower kamar yadda ta ga Hamida ta yi. Sai ta fara yin tsalle sannan ta shige tsakiyar ruwan suka yi ta sauka a kanta tana rawa da waƙa kala-kala tana juyi. Ta kwashi tsawon minti talatin a cikin ruwan har sai da muryarta ta fara shaƙewa ta shiga tari babu ƙaƙƙautawa. Sannan ta kashe shower cikin sauri ta fito da kayanta a jiƙe ta haye katifa ta dunƙule wuri ɗaya tana rawar sanyi.

Kafin ka ce me zazzafan zazzaɓi ya rufe ta ruf ta shiga kakkarwa, ita kaɗai a saman katifar tana juyi dafe da kanta da ke masifar ciwo tana kiran sunan Kandala a kan don Allah ta zo kanta cirewa zai yi.

Hamida kuwa, kukan da Baby take yi ya hana ta saurin shirya wa maigidan nata jakar tafiya, dokarsa ta Bintoto ba za ta sake ɗaukar ta ba ta katange mata son kai ta wurinta. Da dabara ta ba ta kayan wasa bayan ta haɗa mata madarar NAN da ake ba ta tana wasa da fidar. Cikin sa'a ko da ya dawo ta gama komai, tare suka fito da shi a falo yana ja mata kunne a kan sai ta saka ido sosai ga Bintoto. Gudun ta jawo musu wata musibar da za ta dame su tun da ta ji ta ga gani za ta iya zama da ita a yadda take. Dalilin da ya sa Bintoton ta ji tashin muryarsu a falo kenan kafin ya bar gidan.

Daga rakiyarsa ta nufo ɗakin Bintoto a lokacin ta ji motsin saukar ruwa toilet zuciyarta ta saƙa mata wanka take yi. Hakan ya sa ta koma hidimar baby bayan ta kwashe ɓawon ayaba da lemun da ta sha ta watsar a tsakar ɗakin, sannan ta faɗa kitchen tana yi musu girkin dare.

Misalin ƙarfe bakwai da rabi na dare Hamida ta shigo ɗakin ɗauke da plate ɗin abincinta, kuma da niyyar ta ji idan ta yi sallah. Saboda shirun da ta ji ba ta fito ba

har lokacin, tunaninta ya ba ta barci ta yi bayan ta fito daga wankan. Sai dai halin da ta gan ta a ciki hankalinta ya tashi sosai, jikinta yana rawa ta ajiye plate ɗin ta yi kanta.

"Fatima, Fatima!"

Sunanta ta shiga kira ganin fuskarta har ta sauya idanuwanta sun yi ja bayan tarin da take yi har da atishaya. Ɗago ta ta yi cikin rawar jiki hucin zafin jikinta ya dake ta bakinta yana rawa ta ce,

"Ya salam! Daman ba ki da lafiya kuma shi ne ba ki sanar da ni ba?"

Bintoto ta ƙara langaɓe mata tare da fashewa da kuka tana kiran,

"Kandala, wayyo don Allah ki..kira mini Kandalat...wayyo kaina Kandala ki zo...zan..zan mu..t...."

Ta ƙare maganar jikinta yana ciccira. Hamida ta fice ɗakin cikin sauri ta haɗa mata allurori da dabara ta tsikara mata ɗaya tana ihu da kururuwa ta yi mata sauran ɗayar da ƙyar.

Sannan ta taimaka mata ta cire kayan jikinta ta sauya wasu, ta kai ta falo ta kwanta a kan doguwar kujera ganin ta jiƙe katifar gadon, ta yi mata rufa da bargo ruf. Kafin ta koma ɗakin ta saki fanka saboda katifar ta yi saurin bushewa. Kayanta kuma ta jefa cikin injinin wanki zuciyarta cike da tausayin Bintoton da halin da take ciki.

Princess Dija ✍

19.

Tsakiyar dare Bintoto ta farka da wata mahaukaciyar yunwa, jikinta yana rawa ta nufi firij saboda mafarkin tana cin ayaba ta gama yi. Kanta tsaye ta fiddo ƙundun ayabar ta fara yago ta ɗaya bayan ɗaya tana ci, don a take ta ci fiye da ƙwara goma. Sannan ta koma kan apple da lemun kwali idan ta gutsura ta zuƙi ruwan lemun. Sai da ta ji cikinta zai fashe sannan ta tsaya tana nishi tare da shafa cikin tana faɗin,

"Wai Allahna! Ni kam har daɗi ya yi mini yawa!"

Ta miƙe dafe da ƙugu ta rufe firij ɗin ta bar kwalayen da ta shanye da ɓawon ayabar duka a wurin, sannan ta koma kan kujerar ta kwanta zuciyarta cike da tunanin kwaɗon garin kwakin Kandala da take ci a garinsu, sannan da irin daɗin da ta sha zuwanta gidan a cikin 'yan kwanaki. A ranta ta ce,

'Kandala sai dai ki yi haƙuri ki bar musu ni kawai, don wallahi ko za a kashe ni ba zan koma wurinki ba. Haka kawai ki yi mini asarar daɗin da nake sh....'

'Kululuuu..'

Cikinta ya yi wani ƙugi a lokaci ɗaya ya shiga murɗawa, aguje ta watsar da bargon a nan falon ta ruga da gudu zuwa ɗakinta, a haka ta faɗa toilet jikinta yana rawa ta haye saman masan gabaɗaya da ƙafafuwanta ta yi tsugunno a inda ake zama da ɗuwawu. Ta shiga kwararo zawo 'ziiiiii' tana rintse ido tare da nishi tana runtse ido, har ta samu juye rabin cikinta sannan ta sauko da dabara tana toshe hanci ganin aika-aikar da ta tafka. Domin gabaɗaya ta ɓata kwalbar har inda ake jingina baya.

Jikinta yana rawa ta kunna shower ta tara ɗuwawunta ta wanke kashin sannan ya miƙe ta yi wa ruwan hanya da hannunta suka koma kallon masan suna sauka samansa da niyyar wanke kashin ya wuce.

Caraf ta hango inda Hamida ta taɓa ruwa suka zo ta yi wurin ta danna makunnin ruwan sai ga ruwa yana ta fitowa har da tozo ya wuce da kashin gabaɗaya. Amma ta ƙi saki ta koma wasa da makunnin ruwan cike da nishaɗi idan ta kunna ta kashe, haka ta dinga yi sai da ta gaji don kanta ta fice ta haye katifa, tare da buɗe ƙafa ɗaya-ɗaya ta baje tana sauke numfashi har barci ya sake yib awon gaba da ita.

Da asuba da ƙyar Hamida ta tayar da ita barci tana gama harigidon sallar da ba ta san komai a kanta ba ta koma ta baje tana ta barci. Ko da Hamida ta gama shirin zuwa aiki ta shigo ɗakin tana sauri ta ce mata ta je kitchen abincinta yana can ta ci. Kuma kada ta je ko'ina babu jimawa za ta dawo, cike da jin daɗi Bintoto ta sauko gadon tana cewa,

"Ki bar mini yarinyar to sai mu zauna kafin ki dawo."

Hamida ta so hakan amma babu yadda ta iya dole ta zaɓi zuwa da ita a kan ta bar ta wani abu ya faru maigidan ya ga laifinta. Duk da tana sauri sai da ta nuna mata yadda za ta wanke bakinta da brush da makilin. Sannan ta fice gidan zuriyarta cike da fargaban kada ta yi mata muguwar ɓarnar da abin zai dame ta. Saboda ta ga aika-aikar da ta yi wa ayaba bayan ta sake yi wa wuri kaca-kaca sai da ta gyara. Amma ta ci burin idan ta dawo za su yi zama na musamman domin hana ta yin abin da zai jiƙa mata aiki ta bar ta da gyara.

Garin wanke baki sai da Bintoto ta yi wa makilin rabi, gabaɗaya ta gurje dasashinta ya fashe yana ta jini tsabar darza da bakin ya sha. Ba ta fahimci ta yi wauta ba sai da ta zo cin dafaffiyar indomie ta sha tarugu, tana kai wa bakinta loma ɗaya ta yi hanzarin dafe kai tare da zaro ido ta kwarma kuwa, a zabure ta miƙe cikin tashin hankali ta shiga zagayen falon dafe da kanta tana faɗin,

"Wayyo! Wayyo na boni bakina!"

Ta ɗauki lokaci yajin bai saki bakin ba, duk kwaɗayinta ruwan gora ta koma sha masu sanyi tana kurkure baki tana zubar da ruwan a inda duk ranta ya yi mata daɗi a cikin falon. Babu zato ta taka ƙafarta saman ruwan, santsin tayis ya ja ta ta faɗi ƙasa har kanta ya ƙwale, bakinta a yage ta fasa wata uwar ƙara dafe da kan ta fice falon da gudu tana waige, saboda ta gama tsorata don zuciyarta ta ba ta aljanu ne suka fisge mata ƙafa ta sha ƙasa.

Harabar gidan ta shiga shawagi tana leƙe-leƙe kasancewar babu maigadi a gidan saboda tsattsauran hali irin na maigidan. Domin kusan kowa a gidansu tsoron shi ake ji, Hajiyarsa kaɗai take taka masa birki ya bi ko da ba ya so. Amma ƙannensa ko gidan ba sa zuwa saboda masifar faɗansa da ba ya jiran sai an taɓa shi.

Bintoto kam garin leƙe-leƙenta ta hango wani filin shaƙatawa da ƙarfen lilo mai mazauni guda biyu. Cike da tsantsar farinciki ta isa wurin da gudu ta haye abin zaman bakinta a washe ta shiga wulwula kanta bayan ta riƙe igiyar lilon tana rufe ido idan ta yi gaba ta dawo baya.

Da abin ya yi mata daɗi ta yi dabarar hawa ta miƙe tsaye, a bisa gangancin da ta yi ƙafarta ɗaya ta zame, babu zato ta faɗo bakinta ya daki abin zaman ta fasa uwar ƙara saboda ta datse harshenta da haƙori jini ya ɓalle nan take.

Dafe da bakinta tana kuka da matsar ƙwalla ta shiga zubar da yawun jinin tana kai wa abin lilon harbi da ƙafa tare yi masa daƙuwa tana zagin sa. Sai da ta gaji don kanta ta bar wurin tana haɗiye yawu da ƙyar saboda gefen harshen nata da ya buge har ya kumbure.

Falo ta koma tana ƙoƙarin haɗa kallo amma ta kasa, duk da ta jona komai daidai amma ba ta iya kunna Tv ba. Haka ta yi ta wasa da remote idan ta latsa ta koma wayar ƙarya tana yatsina fuska da wata tafiya a tsakiyar falon. A ranta tana ji ina ma a ce gidanta ne kuma komai na gidan nata ne.

Haka ta kwashe tsawon awanni tana shiririta har zuwa lokacin da Hamida ta dawo ta tarar da ita tana sharar barci a ƙasan carpet bakinta a hangame yawu yana bin gefen bakin. Saboda ta yi maganin yunwar da ta addabe ta da kwalin hollandia mai sanyi. Kuma ta koma ma'ajiyar kayan shayi ta ci biredi ta kwaɓa madara da milo ta lashe. Bakinta dagaje da danƙon madara da milo, tana ta nishi saboda zogin da harshen yake yi mata har lokacin.

Hamida tsaye ta yi a kanta, zuciyarta a cunkushe saboda ganin yadda ta yi wa falon ɗaiɗaya kamar ba a taɓa gyara shi ba. Komai a watse bayan dauɗar da tayis ɗin ya yi wurare da dama sanadin ruwan da ta yi ta zubarwa, kuma ta dinga bi ta kai da ƙafafuwanta. Saboda ko yawon da ta yi cikin gidan duka babu takalmi a ƙafarta. Nan take ran Hamida ya ɓaci babu zato ta kai wa Bintoto harbi da ƙafa cikin fushi tare da faɗin,

"Tashi ƙazamar banza!"

A zabure ta tashi tana waige-waige da murza idanuwa tana kallon Hamida fuskarta a kumbure ta ce,

"Me na yi miki kuma da za ki dake ni? Ko ba ki ga kwana nake yi ba?"

Hamida ta sunkuya ta ajiye Baby da ke ƙoƙarin kuka fuskarta a cure ta ce,

"Fice mini daga nan baƙar ƙazama kin wani hargitsa mini falo tamkar kafin na fita ban gyara shi ba. Ji..ji..yadda har ruwa kika zubar mini a cikin falo! To wallahi idan kika sake da kaina zan kore ki cikin gidan nan domin ba za ki saka mini ciwon zuciya ba."

Tana masifar faɗan tana gyaran falon Bintoto tana zaune idonta a kanta amma ko motsin kirki ba ta yi ba. Maimakon ta ba ta haƙuri ta koma aika mata harara idan ta juya baya. Sai da ta ga Baby tana ƙoƙarin sauka daga kan kujerar ta miƙe cikin sauri ta ɗauke ta. Kallon ta kawai Hamida ta yi tare da jan tsaki, saboda ta gama ɓata mata rai don ta tsani ƙazanta da ƙazamai. Sannan ga ta da ƙyanƙyami a komai nata sai ta nutsu da tsaftarsa take amfani da shi.

Sai dai dariyar da Baby take ƙyalƙyalawa a kan wasar da Bintoto take yi mata sosai ta rage mata zafin da ta cusa mata. Saboda hatta plate ɗin da ta zuba mata abin kari yana saman kujera ajiye ta ci kaɗan ta bar saura saboda bakin ya ƙi ba ta haɗin kai, ga kuma harshen da ta datse. Cike da jin daɗin ganin Baby ta saki jiki da ita ta ce,

"Ki bi a hankali kada ki sake yi mata rauni ki jawo mini shiga uku."

Bintoto ta ƙara riƙe ta gam tana yi mata wasa, a bisa gwaji ta fara saka mata hannu a baki tana janyewa da sauri tare da ɓoye hannun a jikinta Baby tana ɓangalar dariya. Da gangan ta sake saka mata yatsanta daidai lokacin da Hamida ta ja jakarta da ke kan kujera ta yi ɗaki. Saboda gajiyar da ta kwaso da aikin da ta yi

daga dawowa ko zama ba ta yi ba, sosai take jin ƙyamar jikinta tana da buƙatar wankan gaggawa.

Baby tana dariya ta gatsa wa Bintoto cizo da ƙarfi har da runtse ido, Bintoto ta yi hanzarin faɗin,

"Wash Allah!"

Kafin ta koma yarfa hannun tare da wurga mata daƙuwa tana aika mata harara. Sai da ta ɗaga kanta ta hango Hamida ta shige ɗaki sannan ta jawo hannun Baby ta gatsa mata cizon da ya sa ta zabura tare da ƙwalla ƙara a lokaci ɗaya.

'Ni ma na rama ki ji inda da daɗi.'

Abin da ta faɗa kenan tana ƙwafa, ganin Hamida ta fito a firgice ya sa ta yi hanzarin ɗaukar ta tana jijjiga ta kamar gaske.

Da sauri ta karɓe ta tana tambayar abin da ta yi mata. Bintoto ta shiga rantsuwar ba ta yi mata komai ba idan kuma ta zaci ƙarya take yi ta tambayi Babyn ta ji. Ido kawai ta shiga zare mata tare da cure fuska saboda ganin shatin cizo a hannun Babyn. Don haƙorin Bintoton sun fito raɗau a kan fatarta wanda ko ba a faɗa ta tabbatar da cizon ta ne ta yi.

Cike da jin haushi ta dungure mata kai da kalolin ƙoso, a cikin fushi ta fara balbala mata ruwan faɗa a ranta tana jin kamar ta rufe ta da duka ko za ta rage jin haushin ta . Bintoto kam barin wurin ta yi tana zagin ta a zuciya da gungunin tare da cin alwashin sai ta rama ƙoson da ta yi mata a kan Baby.

Princess Dija ✍

20.

Kwana ta yi tana kumbura fuska, don ko abincin dare da Hamida ta dafa ta kawo mata har cikin ɗaki ƙin ci ta yi. A nan ta bar shi ko wanka sai da ta tsayu a kanta ta yi shi, tana gunguni ta yi barci rabi da rabi da juye-juye saboda kewar kwanciya a bayan Kandala. Sai tsakar dare da yunwa ta tayar da ita dole ta ci abincin tana zagin Hamida da mijinta, a cewarta;

"A farko na zaci ita matar tana da kirki, amma ashe duk halinsu ɗaya, to ni kuma duk sai kun san ɗiya ce ni ba shegiya ba, don ba zan zura ido na bar ku ku cuce ni a banza ba."

Da ire-iren waɗannan zantukan a bakinta ta sake komawa barci. Da safe ma ta ƙi fita daga ɗakin, ko sallar da Hamida ta tayar da ita ce mata ta yi ta yi. Bayan da man can ba ta damu da yin sallar ba. Tsakaninta da sallah asuba ko magriba, idi, ko sallar Juma'a idan sun tafi masallaci da Kandala. Amma sauran duka shan ruwan tsuntsaye take yi musu.

Lokacin da Hamida ta shirya zuwa wurin aiki ta ƙwala mata kira, saboda ba ta son zuwa ɗakin nata gudun ta ga abin da zai ɓata mata rai, shi ya sa ta tsaya daga inda take tsaye a cikin falon rungume da Baby tana bubbuga bayanta don ta samu ta yi barci. Amma sarai tana jin ta ta yi shiru kamar ba ta san tana yi ba. Sai da ta gaji da kiran nata ganin za ta ɓata mata lokaci ta yi latti, ta leƙo ɗakin tana cewa,

"Wai ke Fatima ba kya ji ina kiran ki ne?"

Bintoto ta turo baki sannan ta ce, "To ai ni Bintoto nake ba Fatima sunana ba."

Sakato Hamida ta yi tana kallon ta babu shiri dariya ta suɓuce mata ganin yadda take kallon sama da tagumi ko ƙiftawa ba ta yi.

"To Fatima ni dai a haka nake son kiran ki ba wani Bintoto ba, yau Juma'a ba zan jima ba zan dawo gida. Saboda haka na so bar miki Baby amma halinki ba zai bari na bar ta ba, tun da ina nan ma kika yi mata cizo ballantana kin ga ba na cikin gida.."

"Ai ko jiya wasa muke yi ni da ita shi ne ta yi kuka. Kuma ni ma ta cije ni amma na yi haƙuri na yafe mata."

Bintoto ta faɗa tana rungume hannuwanta a ƙirji tana kumbura fuska. Hamida ta yi 'yar dariya tana cewa, "Wasa ake yi da cizo har shatin haƙori ya fito? Umm.. ni dai kada ki ɓata mini lokaci tashi mu je yau ba zan bar ki cikin gidan nan ba. Abin karinki ma yana can saman baranda a harabar gidan na ajiye miki. A can za ki zauna sai na dawo, kuma kika fita cikin gidan kare yana cikin unguwar nan zai iya cije ki kuma babu ruwan kowa."

Bintoto ta fito daga ɗakin tana hararar Hamida da gefen ido, saboda gaba ta saka ta har suka fice cikin gidan. Tana matsar ƙwalla a ranta tana cewa,

'Ai ni ko wallahi duk bala'i ba zan bar gidan nan ba.'

Wurin da ta nuna mata ta zauna tare da dunƙule fuskarta cikin cibiyoyinta har Hamida ta buɗe gate ta fice da motarta, sannan ta sake rufe gate ɗin tare da leƙo kanta ta ƙaramar ƙofa tana jaddada mata kada ta fita gidan, saboda kare yana yawo cikin unguwar zai iya cije ta.

Ko kallon ƙofar da take tsaye ba ta yi ba har ta ja motarta ta wuce asibiti. A hakan ma ta ja lokaci a ƙame wuri ɗaya ba tare da ta motsa ba. Tsabar takaici da haushin wulaƙancin da take ganin Hamida ta yi mata a kan 'yarta.

Sai da ta gaji da kallon wuri guda sannan ta yi ƙwafa tare da kai kallon ta ga kofin shayin da Hamida ta ajiye mata, sannan da baƙar ledar da ta ƙulle mata biredi da masar ƙwai. Cikin rawar jiki ta yi wurin tare da jawo ledar yawunta yana katsewa ta buɗe ta fara kai wa bakinta tana hararar kofin shayin tana faɗin,

"Mara mutunci sai na shanye ka duka ba zan rage komai ba, tun da ba ni na ce a ba ni ba."

Sai da ta cinye biredin da ƙwan, ta zuƙe shayin har da lashe kofin tas da zura harshenta cikin kofin tana lasar inda duk ta samu harshen nata ya kai, kafin ta kalli ƙofar shiga gidan ta ja tsaki tsabar haushin Hamida ta hana ta yin abin da ta ci burin yi a ranar. A fusace ta wurgar da kofin a tsakiyar gidan tare da bin shi da gudu ta shiga kai masa harbi da ƙafa tana buga shi kamar ƙwallo. Haka ta mayar da shi abin wasa ta yi ta buga kofin da ƙafa tana bin shi da gudu tana ihun yeeee ta cinye.

Ita kaɗai a cikin gidan tana ta hauka har ta gaji don kanta ta buɗe gidan, ta fita tana leƙen inda ta hango karen ya fito a ranar da ta fara ganin shi. Kamar an jefo wani mai rake a layin gidan ta hango shi tafe da baron rakensa mai kyau kuma mai tsafta, ta shiga tsallen jin daɗi tare da shan gabansa cikin sauri tun kafin ya isa inda take, bakinta yana rawa ta fara faɗin,

"Gara da Allah Ya kawo ka, yanzu nake so na tuƙa mota na tafi wurin sayen ta, ashe da na yi gajen haƙuri tun ga shi ka zo har ƙofar gidanmu."

Shi ma yana murmushin jin daɗin maganarta, ya fara tattaɓa raken yana faɗin, "Allah Sarki, ai haka abin yake."

Sai da ta gyara tsayuwarta tana kallon raken, a ranta tana jin kamar ta zari ɗaya ta ruga da gudu, amma ta yi dauriya tana haɗiyar yawu ta ce,

"Raken ɗari biyar za ka ba ni."

Tana gama maganar ta haɗe fuska kamar gaske ita mai kuɗin ce, har da riƙe ƙugu bayan ya zaɓo mata wata ƙatuwa ta ce,

"Ƙare fere mini ita da kyau don ba na son ƙazanta."

Ya ja wuƙa har da 'yar waƙarsa yana gyaran raken ya miƙa mata tare da yayyafa wa rakensa ruwa ya buɗe murya yana faɗin,

"Gaaaa rakeeees!"

Bintoto ta kafa wa raken haƙora ta datso ruwan yana bin gefen bakinta tana wani lumshe ido ta ce,

"Umm Ummm! Wai Allah wagga rake da daƒi take...ƙaro mini wata irin ta guda biyu mu gani nawa kuƒin suka kama."

Cike da jin daƒin yabon raken da ta yi ya ƙara zaɓo mata biyu masu kyau yana faƒin,

"Ai wannan raken tawa ba a wurin kowa za a samu irin ta ba. Shi ya sa duk wanda ya saya sai ya nemi ya ƙara..."

Haka ya yi ta zuba yana sake gyaran raken kamar yadda ya yi mata a farko. Bakinta cike da tokar raken tana tauna ruwan yana ratsa tsakiyar kwanyarta ta ce,

"Ai ni ma a rayuwata ban taɓa shan raken da ta yi daƒin wannan ba....amma wai don Allah a ina ake dafa ta ne a cikin garin nan?"

Dariya mai raken ya yi har da ƙyaƙyatawa, tsabar farincikin ta fara santi a kan rakensa, kafin ya sake cewa,

"Sha ki ƙara kenan...ba ni kuƒin na wuce don yau da alama ko ɗaya ba zan koma da ita gida ba."

Bintoto ta karɓi raken guda biyu bayan wadda ke hannunta tana sha ta juya kamar ba za ta ce da shi koma iba. Shi ma ya biyo ta yana faƒin,

"Ko dai wata za a ƙara miki ne?"

Ta waigo idonta a kan fuskarsa ta nuna masa gidan su Hamida da raken hannunta tana cewa,

"Ka ga wancan gidan?"

Mai raken ya jinjina kai alamar ya gani, cike da gadara ta datsi raken tana taunawa ta ce,

"Gidanmu ne, mu je can na ɗauko maka kuɗinka idan ban ƙoshi da waɗannan ba sai ka ƙara mini."

Bakinsa a washe ya ce, "Ranki ya daɗe ko dai bahon za ki juye mini gabaɗaya na huta da yawo? Don ire-iren ku manya na san wannan ƙaramin aiki ne a wurin k...."

"Ai da jiya ka zo bayan wannan ma idan na juye sai ka koma gida ka ƙaro mini wata. Saboda akwai kuɗi masu yawa da Babana ya ba ni kafin ya yi tafiya, kuma a jiyan duka na rabar da su. Masu aikina ma ba su samu ba sai yau zan sake raba musu kuɗin....mu je ƙofar gidan ka jira ni na ɗauko maka kuɗinka ka san masu kuɗi komai suke so saya suke yi yadda suka ga dama."

Mai rake ya ƙura mata kallo zuciyarsa cike da wasi-wasi a kan zancenta, saboda ganin yanayin ta ko kaɗan ba ta yi masa kama da ɗiyan masu kuɗi ba. Duba da kayan jikinta da takalmin ƙafarta tsohon sani gare shi tun a ƙauyensu. Saboda har sun yi mata kaɗan tsabar ajiyar da Kandala ke yi wa takalmin gudun ta lalata su da wuri. Sannan ga ɗaurin ɗankwalin da ke kanta kamar an kifa kwando, da ɗan kunnen da ke kunnenta na tsofaffi waɗanda ake rabo a yayin bikin aure masu suna tsiyarku dangi. Waɗannan abubuwan sun saka shi tunanin kamar abin da ta faɗa babu gaskiya. Amma saboda ya ga iya gudun ruwanta ya bi ta yana faɗin,

"Ki ce kawai na dawo gobe ko za a dace na shiga cikin 'yan aikin naki a raba da ni?"

"E fa, ka dawo kawai idan za ka iya, ai mu masu kuɗi komai muka yi daidai ne...ƙaro raken ɗaya ka haɗa mini kan kuɗin."

Sai da ya tsaya kallon ta, saboda zancenta ya gama fallasa masa ba ɗiyar kowa ba ce duk su ne shi da ita mutanen ƙauye. Sannan ya zaro raken ɗaya ya miƙa mata tare da haɗe fuska ya ce,

"Kuɗinki sun kama dubu biyu. Je ki ɗauko mini na wuce kada ki ɓata mini lokaci."

Bintoto ta karɓa tana wurga masa harara tare da turo baki ta ce,

"Ni dai ba ni, idan kuma ganin kake yi kamar ba zan iya biya ba ka riƙe kayanka. Daman ku talakawa ba ku iya cin arziƙi ba. Ana so a yi maka taimako amma kana ƙoƙarin yi wa kanka asara....mitssss!"

Ta ƙare maganar tare da jan tsaki ta yi cikin gidan a fusace kamar za ta tashi sama. Tana shiga ta rufe ƙofar tare da kiciniyar danna sakata jikinta yana rawa tsabar tsoron kada ya biyo ta cikin gidan ya ga inda ta ɓoye, ga shi babu kowa ballantana a tare mata rigimar.

Uban tsalle ta daka bayan ta datse ƙofar gidan da sakata ta leƙa gefen kusufar gate ɗin tana kallon shi cikin haɗe fuska ta ce,

"Malam ka yi haƙuri ka tafi sai gobe zan biya ka kuɗin yau babu ko ficika a hannuna."

Princess Dija ✍

21.

Baki a sake ya bi gefen fuskarta da kallo, kafin ya ƙaraso jikin gate ɗin gidan ya nuna ta da hannu ya ce,

"Nan da kika gan ni wallahi na fi ki tashanci. Ko ki fito ki ba ni kuɗina ko na diro ta katanga na ci miki uba! Don a kan rakena ban ƙi na yi miki yankan rago ba matuƙar kika ce za ki nuna mini iskancinmu na karkar..."

"Ai ba cewa na yi ba zan biya ba ko! Cewa na yi ka jira zuwa gobe, idan kuma ba za ka bari ba to ka jira matar gidan ta dawo sai ta biya mini. Ai Allah ma ya sa ni ba matsiyaciya nake ba, ballantana ka nuna mini warin talauci a kan raken da ma ba ta da wani daɗi don an taimaka maka an saya."

Imanin da ya gama kama shi a kan batutuwanta masu kashe jiki da zallar tsagwaron takaici, tsaye kawai ya yi yana kallon ƙwayar idonta da ke leƙensa ɗauke da hararar bayan murguɗar bakin da take yi masa har da guntayen tsakinta mai sautin,

'tsutt tsutt.'

"A tunaninki iri na za ki yi wa wayo?"

Ya ƙare maganar da nuna kansa saboda ta gama ba shi mamakin duniya gabaɗaya. Ba ta yi aune na, kafin ta ba shi amsa ta ji dutsin da ya wurgo mata a kussuwar da take leƙensa cikin ƙunar zuciyap, aka dace ya daki gate ɗin bayan ta ja baya, a ƙufuke ta zuro hannunta tana yi masa daƙuwa tana faɗin,

"Wallahi ban yafe maka b..."

Cafkar da ya so kawo wa hannun nata ya sa ta yi wani ihu tare da janye hannun tana faɗin,

"Kuma ba za a biya raken ba ka yi duk abin da kake so, talakan banza mai warin talauci."

Daga haka ta koma saman barandar da ta sha shayi ta yi zaman dirsham tana ta gatsar rake tana waƙoƙi tare da aika wa ƙofar harara. Daga inda take tana jiyo sautinsa yana ta zage-zage da kai wa gate ɗin duka haɗi da shuri da ƙafa, tsabar haushin da ta tura masa.

Bintoto kam raken ta shanye tas tana ci gaba da waƙe-waƙenta, ta tara tokar raken a gabanta tana lasar baki. A nan ta baje tana hamma saboda barcin da ya cika mata ido tana sambatun daɗin raken ina, a ranta tana faɗin ina ma zai ɗan ƙara mata idan ta samu kuɗi ta biya shi.

Mai rake kam saboda ta kai shi bango, cikin ɗan lokaci ya tara mata tsirarun mutanen da ke wucewa ta ƙofar gidan. Har wani ya so biyan kuɗin amma mai rake ya kafe a kan ko an biya shi sai ya yi mata dukan kawo wuƙa, tun da ta yi masa rainin wayon da bai taɓa cin karo da shi ba tun da ya fara sana'arsa .

Ana cikin rigimar Hamida ta dawo daga aiki. Tun da ta shiga layin nasu ta ji gabanta yana faɗuwa dam-dam. Saboda hango mutane a ƙofar gidan ya tuna mata da Bintoto da ta bari ita kaɗai babu kowa. Hankalinta a tashe ta isa ƙofar gidan ta yi parking, jikinta yana rawa ta fito tana tambayar abin da ya faru.

Wani maigadin maƙocinsu ne ya yi mata bayanin abin da mai raken ya sanar da shi. Hannunta a ƙirji ta sauke ajiyar zuciya saboda tunaninta ya faɗa a kan wani mugun abu ne ya samu Bintoton. Babu jinkiri ta fito da kuɗi a jaka ta miƙa wa mai raken, zuciyarta a cunkushe ta isa ƙofar gidan ta bubbuga kafin ta leƙa ta hango ta kwance ta juya wa gate ɗin baya. Ranta a ɓace ta shiga ƙwala mata kira amma har ta gaji Bintoto ba ta san tana yi ba, saboda wani mugun nannauyan barci ne ya kafce ta mai haɗe da mafarkai.

Tsabar haushin da ta bai wa Hamida ya sa ta kalli maigadin maƙocinsu ta ce,

"Baba ina Black?"

Kai-tsaye ya sanar da ita barci yake yi, fuskarta a haɗe ta ce ya kawo mata shi don shi ne kaɗai zai yi maganin rashin mutuncin Bintoto. Daga jin haka kowa ya yi sakato yana kallon ta, mai raken ma gyara tsayuwarsa ya yi don ya ƙi tafiya duk da ta biya shi kuɗin rakensa. Cikin ɗan lokaci Maigadin ya jawo shi yana ƙugi suka tsaya a ƙofar gidan. Da dabara ya saka shi wartsakewa har ya koma zuba haushi babu ƙaƙkautawa.

Haushin karen ya yi nasarar tayar da Bintoto daga kafurin barcin da take yi. Zumbur ta miƙe da ihu ta shiga wara ido tana neman inda yake. Domin a tsammaninta ya shigo gidan yana so ya kamo ta ya cije ta.

A daidai lokacin ne ta ji muryar Hamida da ke bakin gate tana kiran sunanta. Cikin sauri ta isa bakin gate ɗin da nufin buɗe mata amma haushin karen ya sa ta tsaya hannunta a ka tana faɗin,

"Don Allah ki kori karen kada na buɗe ya cije ni."

Ran Hamida a ɓace ta ce, "Malama ki buɗe babu abin da zai yi miki!"

Da ƙyar ta buɗe gate ɗin tare da zubawa da gudu, Hamida kuma tun kafin ta shiga ta tura karen ya bi ta aguje tana kururuwa da ihun wayyo a taimake ta suka shiga zagayen gidan ita da shi. Saboda kawai ta ladaftu da kyau Hamida ta rufe ƙofar gate, sai da ta ga Bintoton ta galabaita bayan ta gama firgita da karen sannan aka kama mata shi yana ta haushi da ƙoƙarin cafko ta.

Ƙasa ta faɗi tana birgima Hamida tana yi mata faɗa a kan rashin mutuncin da ta aikata wa mai rake, tana ƙara sautin gunjin kukanta da rantsuwar ba za ta sake ba, tsabar tashin hankalin da karen ya saka ta gabaɗaya ta zauce da ban haƙurin da sai da ya dinga saka mutanen da ke bakin ƙofar gidan dariyar dole.

Sannan ta ja ta suka fita har gaban mai raken ta ce ta ba shi haƙuri. Jikinta yana rawa ta duƙa har ƙasa idonta yana tsiyayar ruwan hawaye ta shiga haɗa hannu tana roƙon don Allah ya yi haƙuri ya yafe mata ba za ta sake ba.

Maigadin da gayya ya sake sakin karen ya yi kanta afujajan, a firgice ta zubura tana ihun wayyo uwarta kamar walƙiya ta faɗa gidan a sukwane tana kururuwa, cikin kiɗimewa ta ci tuntuɓe ta faɗi karen ya yi kanta yana ƙoƙarin cizon ta. Yanayin yadda take sambatun tsoro ta bai wa mutane tausayi, aka riƙe karen ta miƙe da jan jiki ta samu maɓoya.

Hamida ta sake bai wa mai raken haƙuri, sannan ta yi wa maigadin godiya ta ja motarta zuwa cikin gidan. Zuciyarta a sake ta buɗe ƙofar ta shige, tare da cin alwashin duk ta sake jawo mata rigima ta gama zaman gidan kenan don ta gaji da tsarabobin rashin jin ta da kullum sababbi suke zama.

Wunin ranar Bintoto sukuku ta yi shi, don bayan firgicin kare yanayin fuskar Hamida ma ya saka ta shiga taitayinta, saboda ruwan faɗan da ta juye a kanta kamar za ta rufe ta da duka. Sannan ta tsorata sosai da kalamanta a kan duk ta sake yin abin ya ɓata mata rai sai ta kawo karen har cikin gidan a cikin ɗakinta ta rufe ta da shi, sai ya gama cinye naman jikinta tass za ta buɗe ta.

Wannan barazanar ta yi matuƙar tasirin ladaftar da ita, don har takatsantsa ta shiga yi a komai na gidan gudun kada ta kuskure a sa karen ya kashe ta a banza. Amma ta ci alwashin duk ta sake ganin mai raken sai ta rama abin da ya jawo aka yi mata a sanadinsa.

Wasa-wasa Bintoto sai da ta kwashe kwana uku a nutse ba tare da ta yi laifi ba har zuwa ranar da maigidan zai dawo daga tafiya. Kuma a ranar Kandala ta yi wa gidan tsinke zuwa ganin ta a kan haƙurinta ya ƙare, kuma ta gama kawaicin da take yi wa Hajiya. Saboda tun daga ranar da suka rabu take uzzura wa Hari da zancen son zuwa ganin Bintoto, duk da an kai ta wurin aikin ta ga gidan babu wata matsala, amma hankalinta gabaɗaya yana kan Bintoto, a duk wani motsinta sai tuna ta tare da zancen zucin ko me take yi a daidai lokacin?

Aikinta ma da Hari ta samo mata, hidimarsa bai sa ta manta da Bintoto ba. Saboda wanke-wanke take yi wa wata Hajiya mai waina, sannan da miƙa abinci da kwashe kwanonin da aka ci abincin idan an kammala. A can take wuni sai dare ya yi ta dawo gidan Hari ta kwanta, ba ta rasa ci da sha ba, amma hankalinta ya ƙi kwanciya saboda rashin ganin Bintoto.

Ranar da aka kwana uku ba su tare; ta saka Jaeri gaba a kan sai ta kai ta gidan aikin ta ga halin da take ciki. Domin a cewarta ko barci rabi da rabi take yi saboda mafarkin da take yi da ita kowane dare. Hajiya da kanta ta ba ta haƙuri a wayar Hari, tare da yi mata alƙawarin idan ta cika sati har gida za ta turo direbansu ya ɗauke ta ya kai ta gidan su Hamida ta gano Bintoton. Hakan ta kasance kuwa, domin ranar tana zuwa tun da asuba ta shirya, ko wurin aikin nata uzuri ta bayar kamar wadda idan ta je a can za ta kwana.

Ƙorafinta ya sa Hari shiri tun kafin motar da za ta kai su ta zo. Kasancewar sun yi shawarar saya wa Hamida kuka, daddawa da kayan yaji, kuma an saya har Kandala ta ƙulle tamau tare da kayan zaƙin da take saya tana ajiye wa Bintoton. Da dabara Hari ta ja tafiyar zuwa ƙarfe goma da rabi na safiya, saboda ƙagarar da Kandala ta yi waje ta koma tana jiran zuwan motar da Hajiya ta ce za ta kai su gidan aikin Bintoton.

Ƙarfe sha ɗaya a kan hanya ta buga musu, duk da gudun da direban yake yi amma Kandala ganin take yi ko kaɗan motar ba ta sauri. Kasancewar Hamida ta san da zuwan nasu hannu kawai ta saka a asibitinsu ta dawo gida. Kuma ta yi hakan musamman saboda dawowar Baban Baby da zuwan su Kandalar.

Amma ko da wasa ba ta sanar da Bintioto ba, don ta daina hira da ita a gidan gudun ta sake sakar mata fuska ta jawo mata wata fitinar da ta fi wadda take aikatawa. Sai dai ta saka ta yin wanka da shiri a cikin kayanta da fitar mata, waɗanda suka yi mata kaɗan kuma take da niyyar kyautarwa. Don sanadin haihuwar Baby wasu kayan nata da yawa sun matse ta, tsabar gayunta tun tana budurwa ɗinki ma daidai jikinta ake ɗinkawa, kuma ba su jimawa a hannunta matuƙar ta yi sababbi sai ta rage yawan kayanta. Wannan dalilin ya sa ta haɗa wa Bintoto kala biyar a cikin kayanta ta miƙa mata, tare da umarnin ta saka ɗaya daga cikin kayan a ranar, sannan kuma ta fito falo ta zauna za su yi baƙi.

Bintoto a gaban madubin ɗakinta bayan ta gama wankan ta shirya tsaf da ita har da goga madarar turaren da Hamida ta saya mata, ta shiga juyi a gaban madubin bakinta a washe tana ta kallon kanta tana zuba shirmen surutan da ta saba koyaushe. Kiran da ta ji Hamida ta yi mata ne ya sa ta ɓata fuska, tana gunguni da bubbuga ƙafa ƙasa tsabar jin haushin ta katse mata abin da take yi, don kalolin tafiyar take yi a gaban madubin tana yauƙi tare da sambatunta na dogon burin da take yi koyaushe.

Princess Dija ✍

22.

Ta fito ɗakin tana haɗa fuskada gunguni, amma tun da ta ƙyalla ido ta hango su Kandala a cikin falon bakinta bai sake rufuwa ba, tsabar jin daɗi da mamakin ba zatar da suka yi mata. Don wani uban tsalle ta daka tare ihun kiran sunayensu ta yi wurin Kandala aguje ta faɗa jikinta. Ita ma Kandala tsabar daɗi da farincikin ganin ta ba ta san lokacin da ta fashe da wani kalar kuka ba. Saboda a take murnar ganin ta ta koma kukan daɗi, sai da su Hari suka yi ta ba ta baki sannan ta share hawayenta idonta a kan fuskar Bintoto ta shiga shafa kanta tana cewa,

"Bintoto me kike ci kika zama 'yar gayu haka a lokaci ɗaya ni kika bar ni da kewarki?"

Ta ƙare maganar tana share sabon hawayen da ke bin fuskarta, saboda kukan da take ƙoƙarin dannewa amma hawayen ya kasa tsayawa a cikin idonta. Bintoto ta turo baki ranta a jagule ganin kukan da Kandalar ke yi, amma hakan bai hana ta magana cikin tsiwa ba.

"Ni dai Kandala ki daina kukan nan kada ki jawo Anti ta ji tausayin ki ta ce ki tafi da ni gida sun fasa riƙo na...bayan kuma aikin da aka kawo ni don shi ma maigidan ya ce ba ya s..."

Kallon da Hamida ta yi saurin wurga mata ya sa ta kawar da kai tana kumbura fuska tare da sake cewa,

"Ai gaskiya ce dole a faɗa, don kin san da yana gidan nan ba zai bari na zauna da ku ba sai ya ce a mayar da ni...."

Murmushi kawai Hamida ta yi kafin ta ce,

"Ai babu ruwansa Fatima, don ko jiya da muka yi waya sai da ya ce ina kike kin daina rashin ji? Saboda da ma can rashin jin naki ne ba ya so, ba wai zamanki a gidan ne damuwarsa ba. Amma yanzu tun da kin rage jawo mana rigima lafiya lau za ki zauna da shi a cikin gidan nan..."

'Babu wani kare shi da za ki yi Anti, don kawai kin ga idon su Kandala. Bayan ke ma kin koyi muguntarsa kina yi mini.. yawwa Kandala, Wallahi ki yi mata magana kare take sakar mini ya yi ta cin naman jikina...dubi hannuna ki gani saura kaɗan ya sake fama mini gociyar da Kulu ta yi mini."

Ta ƙare maganar tare da wurga wa Hamida wata kalar harara bayan ta ƙara shigewa jikin Kandalar ta lafe tamkar wata ƙaramar yarinya 'yar goye. Cike da jin kunya Hamida ta yi hanzarin faɗin,

"Idan ba kya rashin ji me zai sa a haɗa ki da karen t..."

"Amma kuma fisabilillahi idan maganar Allah ake yi me zai sa a haɗa ɗan mutum da kare? To a gaskiya idan har irin wannan horon kuke yi mata don kun ga ba ta jin magana gara kawai a bar aikin tun da ba dole ba ne..ashe ba banza ba nake ta mafarki da ita tana kiran sunana!."

Zancen Kandala kenan, ranta a matuƙar ɓace saboda jin kalamin Bintoto da amsar da Hamida ta bayar. Saboda kai-tsaye ta ji aikin ya fita ranta don zuciyarta ta ba ta zalunci kawai suke yi wa Bintoton ganin an kawo musu baiwa tana yi musu aikatau. Amma fahimtar da Hari ta yi wa Bintoton za ta samu tarbiyya idan zamanta ya yi tsawo a gidan, hakan ya sa ta katse Kandala daga boren da ta fara yi gudun ta ɓata lamarin aiki ya koma mata baya, idan har aka rashin sa'a zaman ya rushe za a wargaza 'yar nutsuwar da ta fara nuna kanta a cikin rikitattun halayen Bintoton.

"Haba Inna, ke ma fa kin san halin 'yar tawa ba ta barin bakin mutum zama kurum matuƙar tana ga wuri. Kuma shi karen ba wai an yi ne don ya cije ta ba, tsoratarwa ce kawai don a samu ta rage abubuwan da take y.."

"Daina yi wa zancen nan kwaskwarima Hari, ko ba ki ji abin da ita uwar ɗakin tata ta faɗa ba? To ba don ba a son Bintoto aka kawo ta aikatau birni kare ya ci naman jikinta ba. Tun da ba baiwa ba ce gara kawai a haƙura da aikin a samo mata wani gidan da ba za a dinga firgita ta da cizon kare ba. Don irin wannan tsaf za a saka mata ciwon hauka garin ladaftarwa ta zauce a saka ni cikin masifa... don haka baiwar Allah don Allah idan kin san ba za ki riƙe mini Bintoto amanar Allah ba ki biya ta kuɗin ranakun da ta yi a gidanki kina tsoratar da ita mu tafi mu bar miki gidanki, tun da aikin ba na dole ba n..."

Zancen Kandala ya katse saboda jin furucin da ke fita daga bakin Bintoton. Domin kuwa zumbur ta tashi daga jikinta ta tsaya ƙyam a gabanta riƙe da ƙugu tana faɗin,

"Ai na rantse da Allah babu inda zan je sai dai ki yi haƙuri ki bar musu ni! Hu'umm lalle ma Kandala, to irin abincin da take ba ni ko Inna Hari ga ta nan ba za ta iya saya da kuɗinta ta ci shi ba, ko na yi ƙarya Inna?"

Ta ƙare maganar tare da nuna Hari da ɗan yatsa, kafin ta sake magana bayan ta murguɗa baki, ganin Harin ba ta ce komai ba ta ce,

"Don haka babu inda zan je ni kam. A bar ni a nan, rashin jin ma da ba ta so ina yi mata na daina...Anti ki faɗa musu don Allah kwana nawa rabon da na yi miki laifi a gidan nan? Ko raken da na sha kika biya kuɗin ai ban sake yi miki irin haka ba ko?"

Hamida ido da baki a sake take kallon ta tsabar dariya da mamakin halin Bintoton na rashin shayin duk abin da ya zo bakinta, bayan ta gama jin haushin furutan Kandalar da suka sa ta gano ita ce tushen matsalar Bintoto, don zuciyarta ta gama tabbatar mata ita ce tsanin duk wata taɓarar da Bintoton take yi, saboda babu tsawatarwa a cikin riƙon da take yi mata kuma ba ta so kowa ya taya ta gyaran tarbiyyarta, sannan ta fahimci tunanin Kandala ya tafi a kan rashin so ne ke sa a yi wa Bintoto horo, saboda ita kaɗai ce mai ƙaunar ta a duniya, kuma ba ta son abin da zai ɓata mata rai.

Shirun da Hamida ta yi ya bai wa Hari damar kallon Kandala da ta kafe Bintoto da ido baki a sake tsabar mamakin da ta ba ta.

"Kin dai ji da kunnenki Inna, har raken mutane ta sha ta bar baiwar Allah da biyan kuɗi! To da a ce baiwar Allahr nan tana cutar da Bintoto babu abin da zai sa ta ce ba za ta bar gidanta ba. Amma saboda jin daɗin zaman da take yi da su; ki dube ta da kyau ki ga yadda ta fara sauyawa a cikin sati ɗaya kacal! Don Allah kalli ko kayan jikinta ki gani Inna ai ba da su ta zo gidan nan ba, don ko ba a faɗa ba kyautatawa ce ta jawo ta yi mata wannan alherin. Don haka ki bar zancen barin aikin a nan inda kika yi shi tun kafin zancen ya yi tsawo, saboda jikina yana ba ni zamanta a gidan nan alheri ne kuma ta sanadinsa za ta samu nutsuwar da muke fata, kuma duk abin da kika san tana yi wanda ba kya so za ta daina shi babu jimawa. Amma idan kin zaɓi ta bar aikin shikenan sai mu tafi da ita kawai, sai dai ba baki na yi mata ba, amma da wuya ta sake samun wani gidan aiki irin wannan matuƙar ta bar sh..."

"Wallahi babu inda zan je ni kam!"

Furucin Bintoto kenan tare da nufar ɗakinta da niyyar komawa ta rufe ƙofa, har sai sun tafi ta fito gudun Kandala ta raba ta da gidan jin daɗi a cewarta. Amma maganar da ta ji Kandalar ta yi cikin sanyin murya da sanyin jiki ya sa ta dawo bakinta a washe ta zauna kusa da ita tare da komawa jikinta ta lafe har da rufe ido tsabar jin daɗi. Domin ita ma Kandalar an yi sa'a ta hango abin da Hari take ƙoƙarin nuna mata kuma ta fahimci komai daga yanayin Bintoton.

"Ai shikenan ta ci gaba da zama Hari, da ma ni karen da ta faɗa ne ya ba ni tsoro. Kada garin horo a kuskure ya guntule mata ƙafa ko hannu, kin ga kuma ni bar mini ita za a yi babu wanda zai aure ta idan ta koma musaka."

Ba Hamida kaɗai zancen Kandala ya bai wa dariya ba har da Harin kanta, don sai da ta ƙumshe bakinta tsabar dariyar da ta zo mata babu shiri. Musamman da ta kai wa Bintoton faka a baya tana faɗin,

"Ni ɗaga ni uwar son jikin tsiya, ko kuma na haɗa ki da karen ya cinye dogon bakinki kowa ma ya huta da kalolin fitinarki."

Garin tashi zaune kanta ya daki haƙorin Kandalar ta yi hanzarin dafe wurin tana faɗin,

"Wayyo Kandala ki yi wa haƙorin giwarki magana kin ga ya cije ni a tsakiyar kai."

"Bantar ubanki! Mashi ne ya cake ki ba haƙori ba."

Hamida babu shiri ta fashe da dariya, a cikin dariyar ta ce, "Kai jama'a! Ashe a tsakaninku ma ana kaftawa."

Hari tana dariyar ita ma ta ce, "Ai in dai Inna da Bintoto suna wuri ko ba a so sai an yi dariya. Amma kuma a hakan babu mai shiga tsakaninsu, wanda ya shiga kuma kunya zai kwasa. Iyakacin mutum da su ido, don idan sun gama artabun sake ɗinkewa suke yi kamar ba su ba. Saboda haka ki yi haƙuri da duk abin ya faru, kuma mun yaba sosai da riƙonku Allah ya biya ku. Da yardar Allah ita ma watarana za ta yi hankali ta bar duk abin da take yi, ko babu komai bakin kowa zai sarara da bari-barin da ake faman yi da ita kullum ku ma za ku samu lada."

Da murmushi mai sauti a kan fuskar Hamida ta ce, "Allah ya ƙara mana haƙurin zama da juriya gabaɗaya...ammmm..sai batu na gaba a kan ita Bintoton; da ma mun yi magana da maigidan a kan ya dace a saka ta makaranta. Amma sai kun amince idan kuna da ra'ayi sannan za a yi komai.."

sabon kafceƍ

Princess Dija ✍

23.

"Ni dai ina so, ko da su ba su amince ba."

Zancen Bintoton kenan tana kallon Kandala tare da turo baki, don ta san halinta sarai, abu ne mai wahala ta bari a yi abin arziƙi da ita ba tare da ta kawo wata matsala ba. Saboda ko a can ƙauyen ita ce ke hana ta zuwa makaranta a wasu lokutan, a cewarta boko karatun 'yan wuta ne, barin sa ya fi alheri idan mutum yana so ya gama da duniya lafiya. Makarantar zauren ma ba zuwa take yi ba, ko Mani ya faki idon Kandala ya kora ta gidan da bulala ba ta zuwa, yawonta kawai take yi a cikin garin ba ta nan ba ta can. Sai ta daidaici lokacin tashi ya yi sannan ta koma gida, Kandala ta yi ta saka mata albarka da jin daɗin ta tafi Makaranta.

Hakan ya sa Bintoton gano shirun Kandala, musamman tagumin da ta rafka. Inna Hari ce ta yi hanzarin faɗin,

"Ai in dai karatu ne Inna ba za ta hana ki ba Bintoto. Rashin jin ki ne kawai ake gudu, ki je ki jawo wa mutane wata fitinar a can ana zaune lafiy..."

"Yo ai Inna na daina komai da nake yi, ki tambayi Maman Baby ga ta nan ki ji...don Allah ki faɗa musu gaskiya zan yi karatu ba zan koma yin rashin ji ba."

Ta ƙare maganar tana kallon Hamida idonta cike da ƙwalla. Hamida ta yi murmushi kawai don ita kanta ta san abu ne mawuyaci shiryuwar Bintoto a cikin ƙanƙanin lokaci. Amma tana ji a ranta kamar idan ta je makarantar, karatun ya fara kama jikinta za ta rage wani abu, ko kuma idan ta yi rashin mutuncin malamai suka horu ta a can, wataƙila za a samu ta rage halinta a huta da jarfa.

Wata gwauruwar ajiyar zuciya Kandala ta saki kafin ta kalli Hamida cikin sanyin jiki ta ce, "Ki yi haƙuri da abin da zan faɗa miki yanzu, saboda na fi kowa sanin wace ce Bintoto da ɗanyen aikinta, don ba na son garin neman gira a tsokale ido..."

"Ni dai Kandala gaskiya ki amince kawai, haka kawai ki ce za ki hana ni don kin ga Allah Ya sa zan zama 'yar gayu. To wallahi ni dai ko ba kya so tun da ina son karatun sai na yi."

Ta ƙare maganar tare da haɗe fuska cikin muryar kuka, ranta a ɓace ta miƙe tsaye tare da ɓare baki ta fasa wani uban kuka tamkar ƙaramar yarinya za ta bar wurin, Hari ta yi hanzarin riƙo hannunta cikin zafin nama ta zaunar da ita tana cewa.

"Ke fa matsalata da ke taɓara, idan kika bi a hankali ai za ta amince ne. Amma kina wannan shirmen yaushe za ta fahimci kin sauya halinki har ta bari ki yi Makarantar da kike so?"

Bintoto ta yi hanzarin share hawayen fuskarta tana kallon Kandala cikin fuskar tausayi tare da turo baki tana muimui. Kandala ta maka mata uwar harara sannan ta yi magana tana miƙewa tsaye ta ce,

"Nan da kika gan ta ko barci sai an yi da ƙyar take tashi, idan ba yanzu aka samu ta sauya halinta ba a sanadin zama gidan nan. Karatun ma ko a garinmu ba son sa take yi ba, sai Mani ya kora ta da bulala har zuwa makarantar sannan take zuwa. Don haka kada ki ɗora wa kanki wannan nauyin ki bar ta kawai ta ci gaba da aikin da ya kawo ta ana biyan ta kuɗinta duk wat..."

"Inna ki bar ta don Allah tun da tana so."

Hari ta yi maganar cikin sassauta murya, don ita ma a son ranta tana so a ce Bintoto ta samu karatun ko don ta goge ta zama 'yar birni kamar yadda take yi mata hasashen samun miji a birni, idan aka dace ta san ciwon kanta sannan ta zubar da shirmen da ke cikin ƙwaƙwalwarta.

Kandala ta nufi hanyar ficewa fuska babu yabo babu fallasa tana cewa, "Ku dai yi yadda kuke so, amma ku sani duk rigimar da ta ɗebo a tsakaninku ne babu ni a ciki ballantana ruwana."

"In sha Allahu ma babu abin da zai faru Inna, ki dai taya mu da addu'a."

Hari ta faɗa tana shafa kan Bintoto ta sake cewa,

"To 'yata, yanzu dai Inna ta amince, amma don Allah ki nutsu kada ki ba mu kunya kin ji?"

Bintoto ta ɗaga kai, tare da miƙewa cikin yin wani tsallen murna ta haye bayan Kandala, sannan ta ruƙunƙume ta tana ihun faɗin,

"Ina mugun son ki Kandalata."

Hari da Hamida suka saka dariya, ganin tana ƙoƙarin kayar da Kandalar garin farinciki, ita kuma ba ta yi ƙasa a gwiwa ba wurin sakar mata duka a saman ƙeyar kanta ba, tana faɗin ta sake ta.

A nan aka sake bin zancen karatun nata a tsanake, bayan Hamida ta nemi alfarmar su zauna su ci abinci kafin su tafi. Ta yi musu jagora har zuwa ɗakin Bintoto sannan ta kai musu abincin a can suka baje. Bintoto a jikin Kandala suna cin abincin, tare da kalolin santi iri-iri a wurin Kandala suna yi mata dariya, saboda bakinta dagaje-dagaje da maiƙon jar miyar tana faɗin,

"Uh'umh! Yanzu Bintoto haka kike cin wannan daɗi kullum safiya ta Allah?"

Bintoto ta washe bakinta tana lasar hannunta, ba tare da ta ce komai ba. "Ai dole ki mini boren ba za ki bar wannan gidan arziƙi ba...wai Hari ko za ki tambayar mini matar gidan mu ji idan akwai wurin zamana ni ma su ɗan sakaya ni cikin gidan don Allah?"

Zancen Kandala kenan tana jinjina kai bayan ta gama gwaiguyar ƙashi tana faɗin,

"Duniya da daɗi Allah mai iko."

Hari ta yi hanzarin rufe bakinta tsabar wata kalar dariya da ta so kufce mata, sai da ta haɗiye tsokar miyar da ke bakinta tana tauna sannan ta ce,

"Ai ke Inna ire-iren waɗannan gidajen babu masaukin tsofaffi a cikinsa. Amma ki yi addu'a idan 'yata ta samu miji sai a yi miki ɗaki a can gidanta ki taya ta zaman auren..."

"A'a gaskiya Inna, ni dai ta yi zamanta wurin ki kawai, kada ta je ta dinga ɓata mini gida da yawun goro."

Dundu Kandala ta sakar mata a tsakiyar baya har sai da ta gantsara, ta kifa kanta saman tsintsiyar hannunta tana gunguni bayan ta sandare tana aika wa Kandalar wani malalacin kallo. Kwafa ta yi a lokacin da Inna Hari ta ce,

"Inna wannan dundun ai zai iya huda mata baya mu shiga uku."

"Gara kawai bayan ya hude tun da ba ta san ciwona ba Hari. Ni ce kawai a wahale koyaushe ina goyon rashin mutuncinta, amma ita ko kaɗan ba ta san darajata ba ballantana na sa ran za ta jiƙaina idan ta yi hankali."

"Ki yi haƙuri Inna ƙurciya ce kawai ke damun ta, idan ta yi hanakalin ai da kanta za ta gano inda duniya ta nausa gaba ta dawo kyautata miki. Don rabon Makka ta farko ke ce da kujerar idan muna da rayuwa."

Kandala ta yi mere tana dungure wa Bintoto kai ta ce, "Uhum, wannan da kika gani idan ta ƙara wanke dauɗarta da ruwan birni cewa za ta yi ma ba ta san ni b..."

Dawowar Hamida cikin ɗakin ya sa suka yi gum tare da jefar da zancen halin Bintotob aka kama wani zance daban, amma fuskar Kandala ko kaɗan babu annuri, alamun Bintoto ta gama ɓata mata rai.

Hamida ta yi musu sha tara ta arziƙi suna ta godiya, ita ma tana godiyar tsarabar da suka kawo mata. Ta bai wa Kandala sabuwar atamfa, sannan da rakiya

har bakin ƙofar gida, saboda Hamida ta fahimci kukan da Kandala take yi duk da a fakaice take share ƙwallar tana baje fuska da murmushin yaƙe. Jikin Hari ya yi sanyi ƙalau, a kan fahimtar shirmen Bintoto ne ya ɓata mata rai har take hawayen, saboda ɗan zaman da ta yi da ita wuri ɗaya ta karanci mugun ƙulafucinta a kan jikar tata, bayan zallar tsagwaron son da ta ɗora mata tamkar ba ta da kowa sai ita kaɗai a cikin duniya.

Da dabara ta ja Hamida gefe, bayan Kandala ta yi gaba ta bar su a baya tace da ita, don Allah ta ƙara haƙuri da halin Bintoton, kuma ta lurar da ita muhimmancin Kakarta da yadda take ƙaunar cigaban rayuwarta. Saboda a tarbiyyar da Kandalar ta yi mata babu cusa tausayi a kan ɗawainiyar da take yi da ita tun tana ƙarama har girmanta. A komai ganin take yi ita dole a yi mata, babu zancen taimakon ta za a yi ko kuma alfarma ce za a yi mata. Shi ya sa ko kaɗan ba ta jin komai don ta ɓata wa wani ko ita kanta Kandalar. Saboda a rayuwarta ba ta san muhimmancin kowa ba ballantana ta san girman mutum ko ta mutumta mutane.

Hamida ta yi wa Hari alƙawarin ɗora Bintoto a hanyoyi masu kyau, sannan ta ƙudurta haƙuri da ita ko don ta tallafi rayuwarta ta samu lada.

Haka suka rabu jiki babu kuzari kowa da abin da yake saƙa wa ransa. Bintoto ma da ke cikin giyar rashin sanin ciwon kai kewar rabuwa da Kandala ya saka ta zubar da hawaye.

Bayan sun tafi ta shige ɗakinta tana ta kuka, zuciyarta cike da son zuwa gidan Inna Hari ta kwana, a gefe ɗaya kuma cike da ɗokin karatun da za a saka ta. Tana ta wassafa yadda za ta saka uniform da kurin da za ta yi a matsayinta na ɗiyar mai kuɗi idan ta je.

Hamida kuwa, takaicin rashin dawowar maigidanta ya sa ta manta shaf da zuwa ɗakin Bintoto ta ga halin da take ciki, har ta shige barci. Saboda ya kira ta a waya yana sanar da ita ba zai samu dawowa ba.

Da ma ɗabi'arta ce rufe gida ko da rana balle duhun dare ya kutso kai. Don haka Bintoto ta kwana a falo TV a kunne tana kallon Wrestling har ita ma barcin ya yi awon gaba da ita. Sai da Hamida ta ji hayaniya tsakiyar dare ta fito a tsorace. Saboda nannauyan barcin da ya ɗebe ta ba ta farka ba sai da kukan Baby ya tayar da ita.

Da hannu a ka ta isa gaban Tv ta kashe ƙirjinta yana bugawa, sannan ta zare komai da ke jone ranta a jagule ta gyara mata kwanciya tare da rufa mata bargo da ke yashe ƙasa, wanda ta yi guzurinsa daga ɗakinta zuwa falon, don kawai ta ji daɗin kallo a lokacin da ta shige cikin bargon, ranta fes ta baje ɗaiɗaya a kan doguwar kujera. Bayan ta gama ciny tsarabar da Kandala ta kawo mata, kayan fruit ɗin da ta yanka a faranti ma tana kallo tana tsinta da cokali mai yatsu tana sha tana yanga. A ranta tana jin kanta wata hamshaƙiya ganin yadda take yin abin da take so babu mai kyarar ta.

Asubar farin Hamida ta tayar da ita sallah, tana gunguni ta ja bargonta zuwa ɗaki ta datse ƙofa. Saboda ba ta son Hamida ta sake takura mata bayan ba ta gama yin barcin ba. Maimakon ta yi sallah sai ta koma kan gado ta duƙunƙune, wani sabon barci ya kwashe ta sai ƙarfe bakwai da minti ashirin ta farka. Shi ma a sanadin dukan ƙofar ɗakin da Hamida ta yi ta yi ranta a ɓace. Saboda ta yi ƙwanƙwasa ƙofar cikin arziƙi har ta gaji ta fara masifa, tare da kiran sunanta a fusace.

Zumbur ta zabura cikin tashin hankali ta faɗa bayi, saɓanin buɗe ƙofar da ya dace ta fara yi ko don ta daina kiran sunanta a sama. A gurguje ta yi wankan sannan ta fito ta buɗe ɗakin, daidai lokacin da Hamidar ta dawo cikin shirin fita aiki, fararen kayanta na asibiti a jiki don ta bar wurin ta je ta shirya ganin ta ƙi buɗewa. Ranta a ɓace ta fara balbale ta da faɗa tamkar ta rufe ta da duka, don tsabar haushi ba ta san lokacin da ta dungure mata kai ba tana faɗin,

"Wai ke ba za ki sauya halinki ba ko? Kalli yadda kika bar ɗakin tun kwanukan abincin jiya da baƙi suka ci kin kasa kwashewa. Sannan kin yi wa falo kaca-kaca da ledodin biskit da na minti, kuma kin sha fruits kin bar farantin sai da na ɗauke miki. To buɗe kunnuwanki da kyau ki ji na gaji da halinki, ko ki gyara ko ki bar gidan nan a yau ɗin nan! Ba za ki saka ni hawan jini ba tun ina yarinyata, haka kawai kafin na haifi yaran da za su saka ni ciwon kai ke ki haifar mini da wani ciwo. Wai tsabar kin raina mutane hatta Tv a buɗe kika bari ta kwana tana aiki. To idan kika bari maigidan nan ya dawo ba ki sauya ba ke ma kin sani ba zai zauna da ke a haka b...."

"Don Allah Anti ki yi haƙur..."

"Yi mini shiru shashasha! Shin kin yi sallah?"

Bintoto ta shiga rabon ido alamun rashin gaskiya tana sosa kai ta ce, "A'a, amma ni dai na..na yi wallahi tun cikin dare da kika tayar da n.."

"Ba ki yi sallah ba!"

Hamida ta yi maganar kai-tsaye ranta a jagule tare da riƙe ƙugu tana wurga mata wani mugun kallo ta sake cewa,

"To sai kin bar gidan nan! Kuma karatun ma an fasa saka ki, don babu yadda za a yi na zauna da wadda ba ta yin sallah a cikin gidana. Oya haɗo kayanki na wuce da ke inda aka kawo mana ke...ba zan iya ba gaskiy..."

A miliyan ta kai ƙasa riƙe da ƙafafuwanta tana magiyar faɗin, "Don Allah...don Manzo Sallallahu alaihi wasallama Anti ki gafarce ni.... wallahi na tuba daga yau ba zan sake b..."

Princess Dija ✍

24.

"Yi mini shiru!"

Ta katsa mata tsawa, Bintoto ta sha jinin jikinta riƙe da towel ɗin da ke kanta tana kyarmar jiki. Umarni Hamida ta ba ta a kan ta tashi ta yi sallah, kuma minti uku kacal ta ba ta ta gama komai ta same ta a falo.

Ta fice cikin sauri saboda ƙarar wayarta da ke tashi alamun ana kiran ta. Bintoto ta miƙe cikin rawar jiki ta doddosa sallah faka-faka don ba ta san me ake faɗa a cikin sallar ba, daga cikin kayan da ta ba ta ta saka kala ɗaya. A gurguje ta fice hijabi a hannunta har tana cin tuntuɓe ta isa falon ido tsakiyar ka tana haki, tamkar wadda ta sha gudu.

Tsaye take a kan Hamida har ta gama wayar sannan ta yi saurin durƙusawa ƙasa tana faɗin,

"Ina kwana Anti?"

Hamida ta yi mata wani kallo kamar ta yi dariya amma ta basar tare da ɗauke kallonta a kanta ta ce,

"Kin sa na yi latti, da na so kai ki makarantar da za ki fara zuwa a yi miki 'yantabiyu. Amma kin ja wa kanki sai gobe idan kin yi sammakon yin sallah kin shirya cikin lokaci. Don haka yanzu mu je na ajiye ki gidan su Hajiya, idan na dawo aiki zan biya na ɗauko ku don Baby ma a can zan barin ta. Kuma saura rashin jin da kika yi jiya ki gwada yi musu a can, kin ga shikenan kin hutar da ni yi musu bayanin yadda halinki yake da yadda za mu rabu da ke salun alun."

Tana maganar tana tafiya da 'yarta a kafaɗa ta fice falon zuwa farfajiyar gidan da jakarta a ɗaya kafaɗar. Jiki babu kuzari Bintoto take bin bayanta har bakin mota, sai da ta yi magana sannan ta rufe ƙaramar ƙofar shiga falon gidan ta miƙa mata makullin. Ta shige motar cike da jin daɗi a ranta, amma fuskarta babu annuri, saboda hararar Hamida da take yi ta gefen ido. Har suka kai gidan su Hajiyar idonta a kan sitiyarin motar da Hamida take juyawa cike da ƙwarewa, a ranta tana jin watarana sai ta fita yawo da motar Hamida a garin, tun da ta gano jujjuya hannu kawai ake yi da sitiyarin tuƙin babu wuya.

Baby tana ta gwarancin ta a kusa da ita amma ko kaɗan ba ta bi ta kanta ba, sai da ta jawo ta a lokacin da Hamida ta tsayar da motar ƙofar gidan sannan ta ɗauke ta tana faɗin,

"Yi shiru, zan saya miki goriba."

Hakan ya sa Hamida ta bar ta da ita, ta shige cikin gidan da sasaarfa tana faɗin, "Ki biyo ni da ita ki miƙa ta wurin Hajiya."

Ta yi gaba ta bar su a baya, Bintoto ta rage tafiya sai da ta ga ta gama gaisawa da miagadin gidan sannan ta bi bayanta, a ranta tana faɗin,

'A kan 'yarki zan rama duk cin zalin da kika sa kare ya yi mini. Kuma ma don rainin hankali sai da kika yi niyyar kai ni makaranta a yau kika fasa. To wallahi sai na fanshe komai a kanta.'

Tana tafe tana zancen zucinta har ta shiga wani ɗan soron da ke kai mutum cikin gidan, a cikin famfas ta nutsa akaifarta ta tsamuko naman ɗuwawun Baby da ƙarfi. Yarinya ta fasa ƙara tare da zabura tamkar wadda aka tsirawa allura. Cikin sauri ta rufe mata baki idonta zare tana faɗin,

"Laalaalaa! Me aka yi miki ke kuma kike kuka? Yi shiru...daina kukan to kada a ɗauka na ci zalinki n..."

Karaf ta haɗu da ƙanen mijin Hamida zai fito daga cikin gidan, cike da tsoro ta zabura tana faɗin,

"Wallahi ni ban yi mata komai ba, idan na yi ƙarya kuma ka tambaye ta ka ji gaskiya."

'Yar dariya kawai ya yi tare da karɓar Babyn ya koma cikin gidan yana jijjiga ta da buga bayanta yana faɗin, "Shiiii...yi haƙuri Baby...kurrrr.." Haka ya dinga yi mata a kunne har ta rage kukan Bintoto tana biye da shi har cikin babban falo. Inda suka ci karo da Hamida tana ƙoƙarin fitowa cikin sassarfa tana duba agogon hannunta.

Ba ta tsaya bi ta kansu ba ta fice tana faɗin, "Sai na dawo."

Hajiya ta karɓi Baby idonta a kan Bintoto tana faɗin, "Maraba da mai sunan manya, sannu da zuwa uwata."

Sai a lokacin Bintoto ta saki ranta ganin yadda Hajiyar take farincikin ganin ta tamkar wata mai babban matsayi a cikin danginsu. Har ta zauna kan kujera, ta tuna huɗubar da Hari ta yi mata a kan gaishe da mutane, hakan ya sa ta zame ƙasa tana gaishe da Hajiyar cikin ladabi. Cike da jin daɗi Hajiya ta amsa tana tambayar lafiyarta, da yanayin zamanta cikin gidan Hamida. Bintoto ta nuna mata babu matsalar komai don kada ta faɗi wani abu Hamidar ta kore ta. Amma hakan bai hana ta cewa wani abu ba.

"Gaskiya Hajiya matar gidan tana da kirki, amma tana yi mini faɗa idan na yi laifi."

Hajiya ta faɗaɗa fuskarta da murmushi tana cewa, "Faɗan ma za ta daina yi miki idan kin daina laifin uwata. Ki nutsu da kyau Hamida ba ta da matsala, shi ya sa aka kai ki wurin ta kuma za ki ji daɗin zama da ita fiye da yanzu..."

Haka ta dinga yi mata nasiha a fakaice tana jan ta wasa da barkwanci har Bintoton ta fara warewa, har da nemo tsintsiya tana share filin gidan don kawai Hajiya ta yabe ta. Da abin ya yi ma daɗi har da aikin bai wa fulawowi ruwa, da wanke wata tsohuwar motar da ke ajiye cikin rumfar gidan. Sai dariya 'yan aikin gidan maza suke yi mata ganin yadda ta dage sai darzar motar take yi da tsalle tana 'yan waƙe-waƙenta na shirme.

Jin daɗin aikin da ta sha, Hajiya ta sa aka cika mata ƙaton plate da abinci ta lamushe tana lasar hannu, ganin kamar ba ta ƙoshi ba ta ajiye mata kula ta ce ta ɗibi iya son ranta. Bintoto ta baje sai da ta ji za ta yi amai sannan ta bar abincin dolenta ba don tana so ba. Ta shiga nishi jingine da kujera tana hamma, kafin ka ce me barci ya yi awon gaba da ita tana jan minshari tamkar wata raƙuma.

Ko da Hamida ta dawo ƙarfe biyu tana ta barcin, don hannun da ta ci abincin ko wanke shi ba ta yi ba ta ɓingire. Hajiya ce ta sa mai aikinta ta wanke mata hannun aka shafe mata baki tare da gyara mata kwanciya. Sai faman yabon ta take yi da jinjinawa ga irin aikin da ta sha. Hamida dai ba ta ce komai na kushe ba, sai dariya take yi tana girgiza kai ganin yadda Hajiyar ta taƙarƙare tana ta yabon Bintoton babu ruwanta, sannan kuma ga ta da son aiki.

Ba su bar gidan ba sai yamma, sannan da abincinsu na dare da aka haɗo su da shi aka hutar da Hamida shiga kitchen. Hajiya ta yi wa Bintoto kyautar atamfofi da dogayen riguna ta ce a ɗinka mata ta samu na gayu ko za ta samo mata Baba, a matsayin da ta ba ta na uwa mai darajar da ba ta son abin da zai taɓa mata ita. Bayan ɗan kunne da kayan kwalliya har da turare ta saka mata cikin kayan. Ga lemun Shani da ta zuba mata gwangwani uku a leda, bayan ƙaramar gorar Pepsi-Cola guda biyar da fanta biyu. Amma hakan bai hana ta gane-gane a kan titin komawarsu gida ba. Don duk abin da ta gani ana sayarwa a bakin titin sai ta ce, 'Anti ga kaza can ki saya mini don Allah. Wayyo gwaba ta nuna yawuna ya tsinke Anti. Laa! Kin ga kifi can an wuce da kin saya mini shi don Allah.'

Sai da Hamida ta gaji da halinta sannan ta ci birki a bakin wani bahon mai kilishi ta saya musu, kowa da ledarsa, sannan ta daina damun ta suka isa gida lafiya ba ta sake cewa komai ba. Saboda auna kilishin kawai ta dinga yi a baki tana kurɓa Fanta har da rufe ido tare da waƙa, da rawa da kai alamun banza ta gama samuwa.

Kayanta ta ɗauka cike da jin daɗi ta nufi ɗakinta ta datse ƙofa. Gado ta faɗa tana birgimar jin daɗin kayan da Hajiya ta ba ta. Ta shiga haukar ta ita kaɗai tare da kiran Kandala da kwalbar turaren da ta mayar waya tana faɗin,

"Hilo! Hilo Kandala kina ji na? Shin ba kya ji kika ce? Yawwa to gara da kika fara jin me zan faɗa miki. Da ma cewa zan yi ki taya ni murna na zama 'yar gayu har da atamfofi Hajiyar nan ta ba ni wai a ɗinka mini na samu miji mai kuɗi....Wayyo daɗi."

Ta yi wani tsalle ta sake faɗawa gadon ta baya da kwalin turaren a kunnenta tana sake cewa,

"Ni fa wallahi sai na yi abin da duk nake so. Kin ga idan na fara zuwa makaranta zan iya Turanci, idan na je America a can zan siyo miki takalmi mai tsini. Ko ba kya so?"

Ta ƙare maganar tana ɓata fuska kamar gaske kafin ta sake cewa, "To ki ce da Kawu Mani ya kora Kulu gidansu tun yanzu kafin na zamo Hajiya. Don wallahi sai na sa an yi mata bulolin tsiya a duk ranar ta bari muka sake haɗuwa. Baƙar muguwa mai fuskar tumaturi. Ai an bar mata gidan ita kaɗai sai ta ci kanta baƙar mayya. Wai Allahna! To ni dai sai anjma Kandala tun kafin ki cika mini kunne da hawayenki."

Ta danna kwallin wayar kamar gaske wayar ce ta gama, don yadda ta ga Hamida tana yi ne take kwaikwayo saboda ta zama 'yar gayu kamar ita.

Ba ta daina shirmen da ta saba ba sai da ta ji Hamida tana ƙwala mata kira a falo, saboda sai da ta yi wanka ta yi wa Baby sannan ta fito da niyyar su ci abinci. Amma har lokacin ita Bontoto babu abin da ta yi, don bayan wayar kwalin da ta yi ta koma baje atamfofi tana ɗaurawa a gaban madubi, don tana so ta gano wadda ta fi yi mata kyau a cikin su. Hakan ya sa gabaɗaya ta yamutse atamfofi ta jibge wuri ɗaya tamkar kayan wanki. Doguwar rigar da ke ciki kuma ta saka tana juyi gaban madubi tare faɗin,

"Ai wannan duk ta fi yi mini kyau."

Tuno kiran da Hamida ta yi mata ya sa ta zabura ta nufi falon. Ganin tana cin abinci ta tuno ashe ita ma ba ta ci abincin daren ba, duk da ba ta jin yunwa, don tsiren da Hamida ta saya mata duka ta cinye har ƙulin tun kafin su ƙarasa gidan.

Next page

25.

Kallo ɗaya Hamida ta yi mata ta ɗauke kai, duk da ta so ta yi mata faɗa a kan doguwar rigar da ta gani a jikinta. Amma tsabar ba ta son surutu ta yi banza da ita, har sai da ta gaji da zaman tana satar kallon kular abincin da wanda take ci, sannan ta gyara zamanta tana cewa,

"Anti wai da gaske rigar nan ta yi mun kyau ko?"

Ba tare da ta ɗaga kai ta kalle ta ba ta ce, "Musamman idan kika bar ta a jikinki kika kwana da ita, za ta fi yi miki kyau."

Ta miƙe cike da jin daɗi tana kallon jikinta ta, saboda ko kaɗan ba ta fahimci gatse ne ta yi mata ba. Baki har kunne ta ce da Hamida,

"Gaskiya ni kaina na san ta yi mini ɗan banzan kyau. Amma kin san mene ne? Idan Kandala ta gan ni da ita zan ce mata rigar Saudiyya ce na sayo a lokacin da na je aikin Hajji."

Dariyar da ta so kufce wa Hamida ce ta sa ta ƙware, ta shiga tari tana bubbuga ƙirjinta har ta sha ruwa ta samu tarin ya lafa. Amma Bontoto ko sannu ba ta ce mata ba, sannan ba ta daina juye-juye tana kallon rigar ba.

"Ki ci abincin ni ba na son sakarci da yawan surutu."

Bintoto ta zuba abincin tana 'yan waƙoƙinta. Jin daɗin girkin ya saka ta shiga jujjuya kai tana rangaji tana ci gaba da waƙenta.

"Ke kina da matsala wallahi, wai wa ya faɗa miki ana magana idan ana cin abinci? To ki ci gaba, idan kika sarƙe wallahi ko sannu ba zan yi miki ba tun da ba ki da hankali."

Tana gama faɗar maganar ta miƙe tare da plate ɗin da ta gama cin abincin ta nufi kitchen tana sake cewa,

"Idan kin gama ki tabbatar kin kwashe komai kin wanke. Yau da wuri nake so na yi barci, ke ma ki kwanta cikin lokaci, don idan kika yi lattin tashi a goben ma ba zan kai ki makarantar ba."

Maganganun da ta yi kenan har ta wanke plate ɗin ta ajiye ta fito ta nufi ɗakinta da niyyar shigewa. Bintoto ta yi hanzarin miƙewa tsaye tare da ɗaga murya tana lasar hannu ta ce,

"Anti kallon fa! Ba ki kunna mini ba."

"Ba zan kunna ba, tun da barci kike yi ki bar shi har safe yana aiki."

Daga haka ta shige ɗakinta ta rufo ƙofa. Bintoto ta riƙe ƙugu tana aika mata harara ta ce,

"Wallahi idan ba ki bi ni a sannu ba sai na yi miki abin da maigidan nan zai ya mayar da ke gidanku. Na san a can babu tirbin kallon, sannan kuma tuwon dawa ne ake ci a shari malmala ba irin abincin gidan nan mai shegen daɗi ba. Tana wata tafiya haka....haka...tamkar za ta karye don lauɗi. Ni wallahi gabaɗaya ma haushi take ba ni yanzu."

Ta ƙare maganar bayan ta gwada yadda Hamidar take tafiya tana yatsine fuska, tare da yarfa hannu tana aika wa ƙofar ɗakinta harara.

"Ke kika sani."

Ta murguɗa baki tana kwashe kayan abincin ta yi kitchen. Har za ta juyo ta fito, ta tuno da umarnin da ta ba ta a kan ta wanke komai. Tana tsaki da gunguni ta wanke ta ajiye inda ake tsane kwanoni. Maimakon ta fito kitchen ɗin sai ta koma wasa da ruwa tana yi tana wanke fuska da ƙafa kamar mai arwala. Sai da ta jiƙe kitchen ɗin ko'ina sannan ta kashe fanfon ta fito, tana bubbuge ruwan da ya ɓata mata riga.

"Wayyo sabuwar rigata ta jiƙe, kuma ga shi masifaffiyar matar can ta ce na kwana da ita. To amma ni ko wallahi sai na cire ta babu yadda za a yi na kwana da ita a jikina ta jiƙe. Sai dai komai za ta yi ta yi ba zan yi abin da ta ce ba."

Daga haka ta sauya rigar ta jawo lemunan da Hajiya ta ba ta ta dinga kwankwaɗa, sai da ta ji babu wani sauran fili a cikinta sannan ta ajiye saura tana zuba gyatsa kala-kala. Atamfofin da ta dunƙule wuri ɗaya ta ɗora hilo a kansu ta kwanta tana zuba hamma. Daga nan sai barci.

Asubar farin Hamida ta tayar da ita, tun kafin a yi sallah. Sai da ta tabbatar ta tashi sannan ta koma tana sabgoginta a kitchen. Ganin yadda ta ɓata kitchen ɗin ta ji a ranta ina ma ba ta ce ta yi wanke-wanken ba.

Bintoton kam kamar kada Hamida ta tayar da ita, tana shiga bayi ta dinga kwarara zawo. Kafin ka ce me ta jigata, ko da ƙarfe shidan safe ta yi gabaɗaya ta zuge a lokaci ɗaya. Amma a haka ta yi ƙarfin halin shiryawa gudun ta yi laifin da za a fasa kai ta makaranta. Hamida kanta tana ganin ta ta ce,

"Ke lafiya me ya same ki haka duk kin yi laushi?"

Tana turo baki ta ce, "Ba zawo nake yi ba!"

"Da ma shegen kwaɗayinki ai dole ki yi zawo. Ke komai kika gani sai kin ci, to garin ciye-ciyenki sai kin yi zawon hanjin cikinki gabaɗaya kowa ya huta da halinki."

Ta dangware mata plate ɗin Irish da ƙwan da ta soya, sannan da kofin shayin da ke hannunta ta yi ɗakinta. Mintuna a tsakani ta fito, cike da mamaki ta dinga kallon Bintoto da abin da ta ajiye mata, don kafin ka ce me har ta cinye ta koma lasar hannu. Hamida tana isowa wurin Bintoto ta bazama da gudu ta yi ɗaki. Saboda wani arnen zawon da ya taso mata wanda tun kafin ta isa bayin ya dinga bin ƙafafuwanta.

Hamida ta biyo ta, ganin inda ta nufa da warin da ke tashi ta tabbatar da wani zawon ne za ta yi. Kafin ta ankara da wanda ya bi ƙafafuwanta duk inda taka. Cikin sauri ta fice tana duba jikinta ranta a ɓace ta yi ɗakinta.

'Allah Ya gani ni dai na gaji da zama da yarinyar nan. Tsabar ƙazanta har da kashi za ta dinga yi mana barbaɗe a cikin gida?"

Sai da ta wanke jikinta ta kunna turaren ƙamshi a gidan ta ko'ina, sannan ta ƙwala mata kira daga inda take tana cewa,

"Wallahi sai kin gyara duk inda kika ɓata. Kuma idan kika sa na yi lattin fita na rantse da Allah sai kin bar gidan nan don na gaji da zama da ke."

Bintoto ta fito bayan ta cire kayan da ta ɓata ta wanke, sannan cikin rawar jiki ta dinga gyaran duk inda ta hango zawon. A bisa umarnin Hamida da ke faɗa mata kaza za ta yi ta saka kaza ta barbaɗa kaza har ta gyara wurin tsaf. Cike da ƙyama Hamida ta miƙa mata wasu magunguna ta ce ta shanye su duka. Jikin Bintoto yana rawa ta kora su da ruwa.

Misalin ƙarfen bakwai da mintunan safiya suka bar gidan. Bayan Hamida ta tabbatar da jikin Bintoto babu inda yake wari. Don turare ta yi mata kala-kala sannan ta bar ta shiga motarta. Amma duk da hakan idan ta tuno da halin Bintoton tana jin ba za ta iya ci gaba da zama da ita ba.

Gambo Academy, sunan Makarantar da aka saka ta, saboda da ma can sun biya kuɗin komai kai ta kawai ya yi saura, ba tare da dogon turanci ba aka ba ta uniform da littafai, saboda makarantar kuɗi ce komai su suke bai wa ɗalibansu. Amma aji biyu aka ajiye ta na Firamare, saboda wasu tambayoyi da aka yi mata ba ta amsa su ba. Hamida ta tafi ta bar ta bayan an kai ta cikin aji ta zauna. Bintoton ta dinga kallon yaran da ke cikin ajin 'yan kuci-kuci duka ba su wuce shekara bakwai zuwa takwas ba, a ranta ta ce,

'Cabɗijam! An ma raina mini wayo. yanzu waɗannan yaran ne 'yan ajinmu? Ai kuwa dole a ba ni monita, idan ba haka ba wallahi duk sai na ci ubansu."

Tana zaune tana wara ido bayan ta dawo daga tunanin da ta lula, ta fahimci yaran ajin duk ita suke kallo suna dariya, ganin ta gandama a cikin su. Hakan ya ƙara ɓata mata rai, ta shiga aika musu harara kafin ta miƙe ta tsaya gaban ajin riƙe da ƙugu tana cewa,

"Da wa da wa ne suka yi mini dariya?"

Cike da mamaki 'yan ajin suka dinga kallon ta kafin wani daga cikin yaran ya ce, "Me za ki yi idan an faɗa?"

"Idan ka sani kawai ka sanar da ni, yanzu babu ɓata lokaci zan sanar da kai abin da zan yi."

Sai da ya isa gabanta da wata kalar tafiya sannan ya tsaya gabanta ya ce, "Ni ne nan! Me za ki iya y...."

Kafin ya rufe bakinsa ya ji saukar mari fau! Takaicin marin da ta yi masa ya saka shi yin cikin ta da naushi mai haɗe da harbi da ƙafa. Amma duk da haka tun da ƙarfi ba ɗaya ba, ko'ina kokawar ba ta je ba Bintoto ta kayar da shi ƙasa ta taushe tana ta duka. Yayin da wasu abokansa suka shiga faɗan su ma suka dinga kai mata harbi da ƙafa masu sakar mata duka a baya suna yi. Hakan ya sa ta sake shi ta koma kan wanɗanda suka shigar masa faɗan tana dukan su bayan ta ci kwalarsu. Amma nan take suka kai ta ƙasa saboda ƙarfinta ya gama ƙarewa, da ma can zawo ya cinye rabin ƙarfin. Kafin malamai su shigo a raba har sun jigatar da ita, don bayan mazan da suka shigar wa abokinsu faɗan har da wasu matan ajin sun afka faɗan.

Hakan ya sa ba a ba su gaskiya ba, duk da bayanin da suka yi wa malaman a kan cewa ita ce ta fara jawo faɗan. Ganin yadda suka saka ta yin laushi ko tafiya sai an riƙa ta take yi. Sunan Kandala ko ta kira shi ya fi sai hamsin. Har da hakan ya sa yaran da ke wurin sulhun suka dinga dariyar shirmen da take yi da surutan da take faɗa.

A nan aka yi wa yaran da suka yi faɗa da ita bulala goma-goma, sannan aka ce duk wanda ya sake taɓa ta ko ya yi mata rashin kunya ko dariya a cikin ajin sai an kore shi ya bar makarantar bayan an gama hora shi. Yan ajin ma da babu ruwansu sai da aka yi musu bulala biyar-biyar, a cewar malaman ita Bintoto sabuwar zuwa ce ba za a buge ta ba, sannan kuma dukan da aka yi mata ya wadatar ba sai an ƙara mata ba. Nan take zazzaɓi ya rufe ta, ko da aka tashi makarantar ko idonta ba ta iya ɗagawa. Waɗanda da suka dake ta suka dawo jin tausayin ta suna faɗin ta yi haƙuri, ganin yadda take rawar sanyi da kakkarwa alamun ita kaɗai ta san me take ji. Kasancewar Makarantar haɗe take boko da Islamic, ƙarfe biyu daidai wasu daga cikin 'yan ajin suka kai ta Clinic ɗin makarantar. A can aka yi mata allura biyu tana ta ihu da raki kala-kala yara suna yi mata dariya.

Ƙarfe biyar motar Makarantar ta ajiye ta a bakin titin gidansu Hamida. Ta fito tana jin jiri ta dinga bin bangon gidajen mutane tana tafiya, idan ta gaji ta tsaya ta huta, haka ta dinga yi har ta isa bakin ƙofar gidan. Tana ƙoƙarin bubbuga gate ɗin ta ji wata murya a bayanta tana yi mata sallama. Cike da matsanancin tsoro ta yi hanzarin juyawa tare da faɗin,

"Innalillahi!"

"Yi haƙuri don Allah, ni ma ban yi zaton ke ce ba, sai daga baya na tabbatar da ke ce sannan na biyo ki. Saboda na san za ki tuna ni idan kika gan n...."

"To ban tuna ka ba! Ka tafi kawai ba na tsayawa magana da talakawa."

Cike da mamaki ya dinga kallon ta, saboda ba ƙaramin naushi maganarta ta yi wa zuciyarsa ba. Don tun ranar da ya fara haɗuwa da ita yake fatar Allah Ya mayar da shi garinsu ya nemo gidansu. Sannan bayan barin su garin ya samu damar komawa, amma labarin da ya ji ya saka shi barin garin cikin alhini. Don an sanar da shi wani ya nemi lalata mata rayuwa shi ya sa aka kai ta birni aikatau. Amma abin haushi, yana murnar ganin ta ita kuma ta zo masa da abin da ya jijjiga tunaninsa.

"Yanzu da gaske ba ki gane ni ba Bintoto? Ni ne fa wanda na zubar miki da goro a garinsu kika ce sai na saya duk..."

"Kai ka tafi na ce! Ban gane ka ba, ni ban ma san lokacin da aka yi haka ba. Sannan ka ga ban da lafiya ma, ko magana da kai ni ba na son ma na yi. Ka tafi don Allah."

Ta ƙare maganar da bubbuga gidan tana ƙwala kiran "Anti don Allah ki zo ki buɗe mini zan faɗi."

Ta ɗauki lokaci tana bubbuga ƙofar kafin Hamida ta zo ta buɗe mata, shi kam kansa kawai ya saka cike da baƙin cikin wulaƙancin da ta yi masa. Sannan kuma da alwashin sai ya samo kanta tun da har ya fahimci inda hankalinta ya fi karkata.

Princess Dija.

26.

Kuka ta fashe da shi iya ƙarfinta tana kiran sunan Kandala tun da ta yi ido biyu da Hamida. Saboda takaici goma da ashirin da ya haɗe mata, ga zafin zazzaɓi, ga rashin kuzarin zawon da ta sha da na dukan da 'yan ajinsu suka yi mata. Don ba ta yi tsammanin za su yi mata taron dangi ba, hakan ya sa ta so nuna musu halinta don su dinga jin tsoron ta kamar yadda ake tsoron ta a ƙauyensu. Sai ga shi duk da ƙarfin da take kuri da shi an goge mata harda, da ma an ce taron yawa ya fi taron ƙarfi.

Kallo mai cike da mamaki Hamida ta dinga aika mata don ta kasa barin bakin ƙofar gate ɗin, ganin yadda Bintoton ta zube tana ta kuka da gurje-gurje a ƙasa.

"To ni dai na gaji da tsayuwa, idan ba ki tashi shiga gidan ba na rufe ƙofar, lokacin da kika gama abin da kike yi ki sake bugawa na zo na buɗe."

Bintoto ta yi banza da ita tare da ƙara volume ɗin kukanta dafe da kanta da ke mugun sarawa. "Wannan haukar taki za ta jawo Black ya tashi daga barci, kuma wallahi idan ya zo ko kin bubbuga mini ba zan buɗe ba."

Zabura ta yi cike da matsanancin tsoro ta juya tana kallon ƙofar gidan da karen yake, tana ciccika da shesshekar kuka ta faɗa gidan har tana ƙoƙarin ture Hamida. Ba ta tsaya bi ta kan abin da ta yi mata ba, ta rufe gidan tana faɗin,

"Allah dai ya dawo da maigidan nan lafiya, na gaji da halinki, Allah ma ya san na yi abin da zan iya."

Bintoton da ke ƙoƙarin shigewa cikin gidan ta waigo tana turo baki ta ce, "Don ba ki san abin da ya faru ba ne shi ya sa kike ganin laifina, to sanyi nake ji, har da allura aka yi mini a muguwar makarantar da kuka kai ni. Sannan wasu 'yan yara suka yi mini taro a cikin ajin suka yi ta duka na. Idan kuma kin ɗauka ƙarya nake yi ki je makarantar ki tambayi malamai."

Tana gama faɗar maganar cikin muryar kuka ta yi cikin gidan ta bar Hamida tsaye cikin sanyin jiki. Don yanayinta ya nuna zazzaɓi ne ya kafce ta, duk da ba ta yi mamakin dukan da ta ce an yi mata ba. Saboda ba kowa zai iya jurar halinta ba, ita kanta ba don tana kai zuciya nesa ba da tuni ta karya mata hannu ko ƙafa.

Kai-tsaye ta nufi ɗakinta, ta ɗauko wasu magunguna sannan ta je ta haɗa mata tea da ruwa ta kai mata. Inda ta hango Bontoton ta dunƙule bisa gadon jikinta yana ta ciccira haƙoranta suna kakkarwa, cikin sauri ta zauna bakin gadon tana kiran sunanta. Da ƙyar ta samu ta sha ruwan shayin da maganin, Hamida ta jawo bargon da ke gadon ta lulluɓa mata kafin ta ce,

"Ki yi barci da kin farka za ki ji kin wartsake. Tun da kin ce an yi miki allura a makaranta."

"Kan....Kandala za a kira mini, wur...wurin.... ta na...nake so na kom..."

Sosai ta bai wa Hamida wani kalar tausayi saboda tuno artabun da aka sha da ita a kan ba za ta bar gidan a ranar da su Kandalar suka zo. Har cikin ran Hamida, ta ji kamar abin da take yi mata a cikin gidan ba ta kyautawa, tun da har Bintoto ta iya furta cewa a kai ta wurin Kandala ta manta da abincinta da take maita. Jiki babu kuzari ta miƙe ta fice, tare da ja mata ƙofar ɗakin, bayan ta gyara naɗin atamfofin da Bintoton ta watse. Zuciyarta cike da burin ta ga Bintoto ta samu lafiya idan ana gama ɗinkunan ta fara gayu.

Bubbuga gate ɗin gidan da ake yi ya sa Hamida ta yi hanzarin kammala sallar da take yi ta shafa guntuwar addu'ar da ta yi a gaggauce gudun ta tashi ba ta yi kowace addu'a ba Mala'iku su jefo mata sallarta. Saboda tun tana yarinya ta wannan fatawar kafin malamai da ya tunatar da ita cewa, "Duk wanda ya yi sallah bai tsaya ya yi addu'a ba ba za a karɓi sallarsa ba. Mahaifiyarta ma cewa ta yi a fuska a jefa wa mutum kayansa yana tashi ya watsar da ita a nan, saboda babu fiffiken da za ta tashi sama ta je inda ake.

Cikin sauri ta isa bakin ƙofar ta buɗe bayan ta ce waye, ya sanar da ita shi saurayin Bintoto ne. Mamakin da zancen nasa ya sa ta buɗe ƙofar tare da ƙare masa kallon sama da ƙasa kafin ta ce,

"Kai ne saurayin Fatima?"

Yana washe baki tare da sosa kansa da makullin mashin ɗin da ya zo da shi ya ce, "I Bontoto ba, ai na san ta tun a ƙauyensu kafin ta zo gidan nan aiki. Har garinsu na yi neman ta aka ce da ni ta dawo nan birni tana aikatau."

"To ya aka yi ka san tana gidan nan?"

"Ɗazu na gan ta lokacin da motar makarantarsu ta ajiye ta, har magana ma mun yi da ita ta ce mini ba ta da lafiya."

"Ikon Allah."

Hamida ta faɗa cikin sakin fuska, saboda yanayinsa ya nuna gaskiyar abin da yake faɗa. Ledar da ke hannunsa ya miƙa yana cewa, "Don Allah a ba ta, ni zan wuce Allah Ya ƙara afuwa."

Ta zura hannu ta karɓi ledar tare da rufe ƙofar, daidai lokacin da motar Aliyu ta durfafo unguwae tare da sakin titin ta isa bakin ƙofar gidan ta tsaya. Saurayin Bintoton yana ƙoƙarin juyawa da mashin ɗin sa Aliyu ya fito daga motar a zafafe ya shaƙo wuyan rigarsa, yana ƙoƙarin kai masa naushi saurayin ya yi hanzarin cewa,

"Wurin Bintoto na zo, ni saurayinta ne tun tana ƙauyensu."

Ran Aliyu a matuƙar ɓace ya sauke hannunsa tare da hankaɗa shi gefe yana nuna shi ya ce, "Daga yau kada ka sake zuwa gidan nan! Idan ba haka ba duk abin da ya samu iyalina kai ne. Ita ma wadda ka zo wurin ta kora ta zan yi, sai ku je can ƙauyen ku dinga haɗuwa amma ba a gidana ba. Idan kuma na sake ganin ƙafarka a nan sai na yi maka abin da za ka yi mamaki."

Har ƙasa saurayin ya kai yana roƙon Aliyu ya yi haƙuri ba zai sake zuwa ba. Tare da sanar da shi yanzun ma ba ta da lafiya shi ya sa ya zo yi mata ya jiki.

"Na dai faɗa maka kada ka sake zuwa."

Daga haka ya bar wurin ya koma cikin motarsa, kansa a duƙe yana kiran wayar Hamida saurayin ya wuce aguje da mashin ɗin sa a cikin firgita da kalaman Aliyun.

"Buɗe mini ƙofa!"

Iya abin da ya faɗa kenan a cikin muryar da tana jin sautinta ta ji ƙirjinta yana dakan kuguden uku-uku. Don ba ta yi tsammaninsa ba a lokacin, sannan jikinta ya ba ta cewa wataƙila ya ga saurayin Bintoto a ƙofar gidan shi ya sa kansa ya fara hayaƙi tun kafin ya shigo gidan.

Sanin zafin kishinsa da yadda suke hawa sama su faɗo ƙasa da shi a kan ko 'yan'uwanta maza ba ya so suna zuwa gidan.

Da sassarfa ta isa bakin ƙofar gate ɗin ta buɗe masa, maimakon ya shigo kamar yadda ta tsammata, sai da ya ja lokaci a cikin motar yana ta danne-danne da wayarsa, duk da ya hango ta riƙe da gate ɗin tana jiran shigarsa.

Amma ko kaɗan abin ya yi bai sa ta yi fushi ba, ta fito gidan tare da doso motar tasa don ta ga me ya hana shi shigowa. Sai dai tun kafin ta isa ya fisgi motar da ƙarfi ya raɓa ta gefenta ya shige. Nan take haushi ya kama ta, tana shiga gidan ta rufe gate ɗin zuciyarta babu daɗi.

Lokacin da take ƙoƙarin isa inda motar a cikin rumfa, ya yi hanzarin fitowa ɗauke da jakunkuna biyu ya yi cikin gidan. Babu jinkiri ta rufa masa baya ranta a ɓace ta shiga ɗakinsa, a nan ma yana jin ƙarar buɗe ɗakin ya miƙe daga kan gadon da ya faɗa yana sauke numfashin gajiya. Sannan ya koma cire agogon da ke hannunsa ya yi toilet.

Zaune ta yi a kan gadon cikin sanyin jiki tana jiran ya fito, amma tuno yana buƙatar abinci ta fice da sassarfa ta yi kitchen. Nan take ƙamshin girkinta ya game gidan, saboda ba ta san zai dawo ba, sannan ganin Bintoto babu lafiya ya sa ko girkin ma ba ta yi ba, don da ma ita ce mai cin abincin, ita kuma ba ta cika cin abincin dare ba sai a lokacin da ta ga dama.

Bayan ta gama kammalawa ta ajiye masa centre table, inda ya saba cin abincinsa koyaushe. Sannan ta koma ɗakin ta tarar da shi har ya yi wanka ya sauya kaya kuma yana sallah, jira ta yi har ya gama addu'a ya shafa, sannan ta fara yi masa sannu da zuwan da babu shiri ta tsuke bakinta ganin irin kallon da yake yi mata kafin ya ce,

"Sau nawa zan sanar da ke ba na ra'ayin kowane namiji ya zo mini gida?"

"To ai wannan mutumin Bintoto ne tun a ƙauye. Kankana, lemu da ayaba ya zo kawo mata saboda ba ta da lafiy...."

"Wallahi ko mutuwa ta yi ba a gidana zai zo gaisuwar ta ba! Ballantana wani ciwo can! Ke har yanzu fa ban manta da ɓawon ayabar da ta jefar na faɗi ba. Da ma can jira kawai nake yi na dawo na mayar da ita wurin Hajiya. Saboda ni ba zan iya zama da ita ba watarana ta sa mu karye ko ta zuba mana guba a abincin da muke ta kashe m..."

"Haba-haba Baban Baby, wallahi Bintoto ba za ta kashe mu b..."

Cikin sauri ya katse ta da cewa, "Sau nawa muka ji labarin 'yan aiki suna zuba wa masu gida guba? To idan ma ba ki yarda za ta aikata ba ni dai ba zan iya zama da ita ba gaskiya. Sannan wancan ɗan ƙauyen idan ya sake zuwa wallahi sai na sa an ɗaure shi. Saboda wani lokaci da an san maigida ba ya gari ɓata-garin mutane suna zuwa yin ɓarna, musamman a wannan ƙarnin da muke fama da rashin tsaro. Ko shi kansa ɗan ƙauyen za a iya turo shi don ya san wani abu dangane da gidan a yi makami da shi. To da muguwar rawa gara ƙin tashi, duk wanda ya zo matuƙar kika leƙa kika ga namiji ne, kuma ba ki san shi kada ki buɗe gidan. Ni na ce ki koma kawai idan da hali ma ki ƙara saka kwaɗo ki datse gidan. Saboda shi mugun bai da kama."

Ajiyar zuciya Hamida ta sauke kafin ta ce, "In sha Allah! Ga abinci can yana jiran ka."

Maimakon ya tashi su je sai ya ɓuge da cewa, "Ina Baby?"

"Barci take yi."

Ta amsa masa a daƙile tare da miƙewa ta fice daga ɗakin. Shi ma ya rufa mata baya, yana fita ɗakinta ya nufa, sai da ya dudduba a ya gano babu wani sabon rauni a jikinta, sannan ya yi mata kiss a goshi ya ja ɗakin a hankali ya fice.

Sosai hankalinsa ya kwanta, saboda tunanin da ke ransa a koyaushe, don har mafarki ya taɓa yi a kan cewa Bintoto ta sako ta daga bayanta, tana faɗuwa ta mutu.Tashin hankalin da ya shiga a ranar tamkar ya rufe ido ya buɗe ya gan shi cikin gidan. Amma saboda bai gama abin ya kai shi ba ya dinga damun Hamida a waya, tare da kashedin kada ta kuskura ta bai wa Bintoto ita bai yarda da ita ba, duk kukan da za ta yi ta bar ta a hannunta, sannan ta ƙara ba ta kulawa.

A daren ranar sun nuna juna kaunar ma'aurata, sannan sun nuna sun yi kewar juna, hakan ya sa da safe Hamida ba ta sha wuya wajen shawo kansa ba. Duk da ya so ya yi tirjiya, amma da dabara ta saka ya aminta da zaman Bintoto har zuwa wani ɗan lokaci, don kai-tsaye ta sanar da shi ita ma Bontoton ta ce ta gaji da zama gidan a kai da wurin kakarta. Sannnan ta ƙara da cewa,

"Yanzu idan ta tafi a wannan lokacin, na san bakinta ba zai faɗi alheri a kanmu ba, kuma babu kalar sharrin da ba za ta iya maƙala mana ba. Sannan Hajiya za ta ce cutarta muke yi shi ya sa ta guje mu. Amma idan muka bari ta warware ciwon, kuma ta dawo nutsuwarta ba za ta ta so barin mu ba. Ko gidan muka tura ta, sai ta yi boren a dawo da ita. Kuma daga haka za a gano ba ma cutar ta."

Ajiyar zuciya ya sauke kafin ya ce, "Wannan shawara ta yi. Amma ki ce don Allah babu ruwanta da Baby."

"Babu damuwa."

Daga haka suka jingine zancen Bintoton, ya shiga ba ta labarin tafiyar da ya yi da abubuwan da suka faru. Amma ko kaɗan bai faɗa mata mafarkin da ya yi ba, saboda ba ya so ya tayar mata da hankali a kan shirmen mafarki.

Princess Dija ✍

27.

Kwana biyu Bintoto tana fama da kanta Hamida tana ƙoƙarin ba ta kulawa har ta samu lafiya. Don ko ɗakinta ma ba ta fita ballantana ta yi abin da zai sa a ce ba ta kyautawa. Abinci ma sai Hamida ta matsa take ɗan tsakura, cike da jin daɗi Hamida ta dinga ba ta kulawa, tare da cika baki a wurin Baban Baby a kan cewa Bintoto ta shiryu duk rashin jin da take yi yanzu ta daina. Shi dai kallo ne kawai nasa a duk lokacin da ta faɗi hakan ba ya cewa uffan, saboda har cikin zuciyarsa bai da nutsuwar zama da ita a cikin gidansu.

Malaman makaranta ma da suka kira shi a waya, suna tambayar kwana biyu ta daina zuwa makaranta, bai ja zaren da tsawo ba, cewa kawai ya yi,

"A yi haƙuri zazzaɓi take yi. Idan ta ji sauƙi za ku gan ta."

Daga haka ya datse kiransa, saboda duk abin da ya shafe ta ba ya son shiga, makarantar ma da ya kashe kuɗinsa matsin Hamida ne ya sa ya biya kuɗin don ya faranta mata. Sannan da Hajiyarsa da kullum suka yi waya ba ta bari a kammala lafiya ba tare da ta sako zancen a kula da Bintoton ba. Har da haushin hakan ya sa yake rage manyan ƙudurin da yake da su a kanta, don a ranar da ya faɗi ba don tafiyar gaggawar da ya yi ba; ya so yi mata mugun dukan ko ganin sa ta yi sai ta dinga firgita.

Hakan ya sa tun da ya dawo ko hanyar ɗakinta bai kalla ba, duk da Hamida ta faɗa masa ba ta da lafiya, amma hakan bai sa ya rage jin haushin da take ba shi ba. A gefe ɗaya kuma tsoron ta illata masa Baby.

Kwana biyun da ta yi a kwance ita kaɗai ake bari gidan a kulle ta ta baya, amma tana ɗakinta ko'ina ba ta zuwa. Sai a rana ta huɗu da ta ji sauƙi wato ranar Asssbar. Daga Hamida har Aliyun duka suna gida, shi ma bai fita kasuwa da wuri ba yana ta barcinsa a ɗaki.

Bintoto ta fito daga ɗakinta jiri yana ɗan ɗibar ta saboda ciwo ya tafi da kuzarin. Ta zauna falo tana wara ido zuciyarta cike da son ganin Kanlada.

Ko da Hamida ta fito daga ɗaki ta tarar da ita zaune ta yi tagumi, Hamida ta ƙaraso inda take fuskarta cike da jin daɗin ganin ta wartsake ta zauna tana faɗin,

"Fatima, ya ƙarfin jikin naki?"

Bintoto ta matse hawayen idonta kafin ta ce, "Ni dai don Allah a kai ni inda Kandala. Idan ma mutuwa ce zan na yi a hannunta."

Dariya ta bai wa Hamida, amma ta fuske tana cewa, "Ke da za ki gode wa Allah kin samu lafiya shi ne za ki dinga kiran mutuwa bayan kin ji sauƙi?"

Shiru ta yi mata kafin ta sake share hawaye ta ce, "To ni dai makarantar nan da kuka kai ni ba zan koma ba, tun da yaran nan suka dake ni kuma suka dinga yi mini dariya. Sannan wannan yaron da ya ce shi saurayina ne ƙarya yake yi, don Allah ma ya sani ni ba 'yar iska ba ce."

Dariya Hamida ta fara yi riƙe da baki tsabar mamakin furucinta na ƙarshe, kafin ta ce, "Wa ya ce da ke 'yar isk...?"

"To ai duk macen da take da saurayi 'yar iska ce."

"An shiga uku ko Fatima, shikenan da mace ta yi saurayi ta zama 'yar iska? Ko kin manta ke ma kin sha faɗar kina so ki yi aure ki je Makka?"

"Ai ni miji na ce, miji nake so ba saurayi ba. Amma shi wannan don kawai ya sa a ce ni 'yar iska ce zai zo gaban mutane yana cewa wai saurayina. Uwanin Jimmai Jarka ta garinmu ma ai saurayinta ne ya yi mata ciki har ta haihu. Shi ne ni yanzu zai zo ya yi mini ciki ya ɓata mini suna a banza....yiiiii!"

Ta fashe da kuka iya ƙarfinta, tsabar takaicin da ke cin ranta, tun a ranar da Hamida ta sanar da ita abin da ya faɗa take cike da haushin saurayin da ya kira. Don ita gabaɗaya ta ɗauki zunubi mai girma ta ɗora ga sunan saurayi, saboda a garinsu mijin wance ake cewa, ko a ce mai son ta.

Hamida kallon ta kawai ta dinga yi tana dariya, kafin ta ji motsin Baban Baby zai fito daga ɗakinsa; ta yi hanzarin kai kallonta gare shi dariyar a kan fuskarta.

Cikin falon ya ƙaraso tare da nufar TV ya kunna ya dawo kan kujera ya zauna, ba tare da ya bi ta kan kukan da ya ga Bintoto tana sharɓa ba.

Sai da ya gama kamo tashar da yake son kallo ya kai kallonsa ga Hamida yana cewa, "Ki ce ta bar falon nan idan ba za ta yi mana shiru ba."

Bontoto ta yi masa wani kallon gefen ido mai ɗauke da harara, kafin ta karkace gefe ta sako tusoshin da take ta ƙoƙarin dannewa a gaban Hamida.

Hamida ta ja hannunta cikin sauri suka nufi kitchen, da niyyar su bar masa falon. Bayansu ya bi da kallon yana yatsinar fuska tare da faɗin,

"Kada ta shigar mini kitchen ta je ta yi wanka. Gabaɗaya wari take yi."

Yana gama maganar ya miƙe ya ƙara ƙarfin Ac da fesa abin ƙamsasa wuri. Bayan ya gama ya yi tsaki a ransa yana cewa,

"Fitinanniyar yarinya, ita koyaushe sai ta saka mutane aiki."

Kamar yadda ya hana su shiga kitchen, haka Hamida ta ja ta suka yi ɗakin Bintoton. Bayan sun zauna Hamida ta ce,

"Ba ki yi wanka ba ne?"

Bintoto ta kai mata harara tana faɗin, "Na yi wanka."

"To me ya sa ba ki fesa turarenki ba?"

"Shinshina ni ki ji sau biyar ina tatso shi a jikina. Idan ma kin ji ina wari tusa ce maigidanki ya yi."

"Maigidana kuma?"

"E, tun da ya shigo falun ɗin nake jin wari. Amma shi ne zai ce ni nake wari kada na shigar muku kicis."

"Ke matsalarki shirme ya yi wa kanki yawa. Wa ya faɗa miki babban mutum yana tusa a gaban mutane? To ba shi ba ne, kuma kada na sake jin irin wannan maganar daga bakinki."

"Na bari."

Ta faɗa tana yi mata wani kallon gefen ido mai ɗauke da harara. A ranta tana tuna yadda Kawu Mani ke buga tusoshi a gaban kowa. Har sai Kandala ta kora shi tana faɗa sannan yake barin wurin, amma shi ne za ta ce wai babba ba ya tusa.

"Fatima."

Kiran da Hamida ta yi mata ne ya sa ta kai kallonta gare ta. "Mu dawo zancenmu na farko wanda shi ne ya sa kika ga na zo nan. Saboda ba na so na bar ki a duhu, shi saurayi ba wai yana nufin ɗan iska ba, mu a nan wanda yake son auren mace shi ake kira saurayi kafin su yi aure, amma da an yi auren shikenan ya zama miji. Sannan kuma ita ɗiyar Jimmai Jarka da kika ce an yi wa ciki, ita ce ta so saurayin ya yi mata cikin, don duk macen da take bari namiji ya taɓa jikinta dole ne watarana sai ta yi ciki. Na san ke kuma babu yadda za a yi don kawai wani saurayi ya ce yana son ki ki bar shi ya yi ta taɓa miki ƙirji da wurin fitsari. Don haka kada ki ji wani wuri an ce saurayi ki munana zato ga mutane tun da idan za a yi iskancin ma ba a gabanki za a yi ba, kuma shaidar zur haramun ne. Sannan na san halinki sarai za ki iya jawo mana fitina muna zamanmu lafiya. Kin gane abin da na faɗa ko ƙara yi miki bayani?"

Bintoto ta ɗaga kai cikin sanyin jiki, Hamida ta miƙe da sauri saboda kiran da maigidan ya ƙwala mata. Jin kukan Baby ya sa ta gano dalilin kiran, cikin sauri ta karɓe ta daga hannunsa ta zauna ba ta abincinta. Daidai lokacin aka dinga bubbuga musu gate, Hamida ta ƙwala wa Bintoto kira ta ce ta je ta je ta gani.

Ta fita tana gunguni ta buɗe gidan, wata budurwa ce ta gani riƙe da yarinya. "Lafiya." Ta faɗa tana haɗe rai.

"Wurin Anti muka zo."

Suna ƙoƙarin kutsa kai Bintoto ta sha gabansu tana cewa, "Shin ku dakata na ce, idan ba ta nan wurin wa za ku shiga idan kun je ciki?"

Sai a lokacin budurwar ta ɗan ja ta tsaya tana yi mata wani kallo kafin ta ce, "Allura za a yi wa ƙanwata. Idan tana ciki ki faɗa mata. Don yau Assabar babu inda take zuwa."

Sai da Bintoto ta yi mata wani kallo kafin ta yi ƙwafa ta ce, "To sai me don allura za a yi wa ƙanwarki? To barci take yi, kuma maigidan ma yana gida suna tare. Don haka ki jira na ce na sanar da ita, idan ta amince shikenan."

Budurwar ta yi mata wani kallon raini sannan ta riƙe ƙugu ta ce, "Ke nake jira 'yar aiki. Don dai na san ke 'yar aiki ce daga ganin ki ba ku haɗa komai da ita ba."

Har Bintoto ta yi gaba ta waigo tana faɗin, "Ni kike kira 'yar aiki? Yaushe kika ga na yi miki kama da masu aiki? To billahillazi ban yafe miki ba!"

Ta ƙare maganar cikin ƙwafa ta yi ciki, amma maimakon ta shiga ta faɗa wa Hamida saƙon sai ta ƙi, sai da ta ja sakonni a tsaye sannan ta fito tana haɗe fuska ta ce,

"Ta ce wadda za a yi wa allurar kaɗai za ta shiga cikin gidan."

"Kya ji da shi ciwon ajali a ɗan yatsa. Matsalar baƙauye duk inda yake sai ya nuna halinsa."

Bintoto ta yi kamar ba ta ji ta ba, suna shigewa ta sakar wa ƙanwarta ƙoso biyu a tsakiyar kai. Yarinya ta tsala ihu Bintoto ta toshe mata baki tana zare mata ido kafin ta koma faɗin,

"Ku ji yarinya da sharri, ki buge kanki a bango shi ne za ki yi wa mutane kuka a ce ni ce na dake k..."

Fisgar da ta ga budurwar ta yi wa ƙanwarta ya sa ta tsaya tana kallon ta, a ƙufule budurwar ta ce,

"Dukan ta kika yi ko?"

"A'a kashe ta na yi ta dawo duniya. Daga ke har ita sai na haɗa ku na tumurmusa a wurin nan. Ta buge kanta shi ne za ki ce ni na dake ta? To an dak..."

Ba ta kai ƙarshe ba ta ji budurwar ta shaƙo wuyan rigarta. Daidai lokacin da maigidan ya ƙaraso saboda kukan yarinyar da daɗewar Bintoto sun saka shi fitowa bai shirya ba. Ganin budurwar tana ƙoƙarin kai mata duka ita ma tana harbinta da ƙafa ya daka musu tsawa. Suka rabu babu shiri, bai tsaya binciken komai ba ya hau yi wa Bintoto faɗa, saboda zuciyarsa ta ba shi ita ce da laifi. Hakan ya ba budurwar damar yi masa bayanin komai. Kunne Bintoto ya murɗe tana ihu da roƙon ya yi haƙuri har ta kai ƙasa sannan ya sake ta.

Cikin fushi ya dinga faɗa tamkar ya rufe ta da duka. Saboda yana sanin ko dawowa ba ta yi ba amma ta ce an ce yarinyar kaɗai za ta shiga ban da budurwar. Takaici ya sa ta fashe da kuka ta yi ɗakinta da gudu. Hamida da ke ƙoƙarin lallaɓawa ta ajiye Baby a kan kujera ta tafi ta ga abin da ke faruwa, babu shiri Baby ta farka daga barcin da ta fara, firgicin kalar kukan da Bintoton ta shigo da shi ya sa ita ma ta ci gaba da nata kukan. A kiɗime ta saɓa ta a kafaɗa ta nufi hanyar fita, ganin budurwar da ƙanwarta a bayan Baban Baby ya sa ta gano Bintoto ce ta sake haddasa wani abu.

Babu ɓata lokaci ya yi mata bayanin komai, ranta a ɓace ta yi wa yarinyar allura tare da bayar da haƙuri. Saboda ba ƙaramin mutuncinta 'yan unguwar suke yi ba, musamman ma gidan su yaran, kuma sun saba zuwa tana yi musu allura har Mamarsu ita take yi mata allura. Wani lokaci idan ciwon ya yi nauyi gidan take zuwa ta yi musu komai suna jin daɗi suna saka mata albarka. Amma shi ne Bintoto za ta sa mutuncinta ya zube a kan shirmenta.

Bayan tafiyarsu ta kira ta tana ta yi mata faɗa, Baban Baby gidan ya bar musu don ba ya ƙaunar buɗe ido ya gan ta a tsakiyarsu. Bintoto ko ta ci buri da alwashin sai ta rama duk abin da aka yi mata a kan budurwar ko ƙanwarta. Tun da aka nuna su ake so ita kuma ba a bakin komai ba. Da takaicin abin ta kwana, da Alla-Alla a

kan ganin safiya ta waye su dawo gidan, don ta ji Hamida ta ce gobe ma a dawo da yarinyar akwai sauran allurai.

Uhum♀

28.

Ranar Lahadi, tun da safe aka kira Hamida ana sanar da ita Babansu bai da lafiya. Hakan ya sa ta fara shirin tafiya gida cikin tashin hankali, duk da an sanar da ita da sauƙi, ko a waya tana iya kira ta yi masa sannu ba sai ta je ba. Amma Aliyu ya ce ta dai shirya su je har da shi ya yi masa ya jiki. Ko da ƙarfe goman safiya ta yi har sun gama shiri, Hamida ta so su tafi da Bintoto amma Aliyu ya ce ba za ta shigar masa mota ba, ta ce to ya tafi su biyo shi da motarta ya ce sam bai san da zancen ba. Don tafiyar ce kwata-kwata ba ya so a yi da Bontoton, a cewarsa ba a shiga gidan kunya da ita, saboda kafin a fito ta tafka wata ta'asa.

Ba don ta so ba, haka suka bar Bintoto a gidan tana ɗaga musu hannu, a gefe ɗaya kuma tana aika wa Baban Baby harara a duk lokacin da ta faki idonsa tana muimui da baki.

Bayan sun wuce ta rufe gidan, har da yin tsallen jin daɗin ganin an bar ta ita kaɗai ta yi abin da take so. Cikin sassarfa ta nufi ɗakin Hamida, da ma can tana so ta shiga ta ga ya yake, amma ba ta ga fuskar hakan a wurin masu gidan ba. Tsaye ta yi tana kallon komai na daki-daki riƙe haɓa tana faɗin,

'Hu'um! Lalle ma matar nan, ashe ta san nata ɗakin ya fi nawa kyau, shi ne ko sau ɗaya ba ta taɓa bari na shigo na gani ba. Ji wasu jakunkuna don Allah, sai ka ce sayarwa take yi."

Cikin sauri ta isa ma'ajiyar takalmin Hamida ta tsaya riƙe da ƙugu tana faɗin, "Kai-kai-kai Waɗannan takalman duk me za ta yi da su haka da yawa? Gaskiya matar nan muguwar gaske ce, yanzu tana da irin waɗannan takalmin da yawa shi ne ni ba

za ta ba ni ko da huɗu ba? To billahillazi sai na saka su na gani idan suna yi mini kyau, ita komai nata mai kyau sai ka ce ita kaɗai ake so a cikin duniya."

Haka ta dinga saka takalmin ɗaya bayan ɗaya tana gwada tafiya da su a tsakiyar ɗakin. Da abin ya yi mata daɗi har jakunkunan ta dinga saƙalawa tana yarfi da hannu da yatsine-yatsinen fuska tana ɗage hanci sama tamkar wadda ta ratsa a tsakiyar mutane tana jin warinsu, tsabar kaifi da kurin da take bazawa daga ita sai ɗaki da madubin da take yada zango a gabansa. Don takalmin ma sai ta ɗaga ƙafa ta duba su ta cikin madubi sannan ta cire ta saka wasu.

Tafi-tafi sai ga ta har da buɗe ma'ajiyar tufafin Hamida. A nan kallo ya koma sama, saboda ganin kayan a tsare komai tsaf har da wani ƙamshi ya dake ta a lokacin da ta buɗe. Tsaf ta yi a ranta tana kallon wasu saitin kayan da suka ɗauki hankalinta tun kafin ta gama buɗe wadrobe ɗin. Hannu ta zura ta jawo su, ido ta zaro ganin aikin da ke gaban rigar yana walƙiya tsabar ya ji shuwari stone tamkar an yi ɓari ba hannu ya saka ba.

Jikinta yana rawa ta shiga warware doguwar rigar ta cire kayan jikinta ta saka. Nan take ta fara tsalle tana jujjuya jikinta a gaban madubi tare da ƙiƙƙifta ido ta rufe ta buɗe tana ɗaga ta gira. Daga baya ta koma fashewa da wata mahaukaciyar dariya.

Cikin sauri ta ɗauko ɗankwalin rigar ta dunƙula kamar yadda ta ga Hamida tana yi, sannan ta dinga fesa duk abin da ta gani a a gaban madubin, wanda take tsammanin turare ne. A cikin abubuwan da ta shafa har body lotion da ta gani a cikin kwandon shafe-shafen Baby, oil da cream duk ta goga wa rigar, hatta hoda sai da ta zazzaga a gaban rigar da hamata, fahimtar hoda ce ya sa ta shiga kakkaɓewa tana faɗin,

"Dalla ban da ke tafi can."

Saboda ganin kayan shafar da yawa, man gashi ma ba ta bari ba sai da ta zuba a hannunta ta goga wa rigar tana faɗin,

"Ita wannan komai sai ta nuna ta fi kowa iyawa, idan ba haka ba waɗannan kayan shafe-shafen duk me za ta yi da su idan ba ta yi ta kallon su a banza b...."

Ƙwanƙwasar gidan da ta ji ana yi babu shiri ƙirjinta ya buga dam-dam. Cikin sauri ta shiga mayar da komai a inda ta gan shi. Tana ƙoƙarin cire rigar wata zuciya ta ce da ita,

'Kada ki cire har sai ta gan ki da ita, wataƙila ta yi zuciya ta ce ta bar miki.'

Umarnin zuciyarta ta bi, cikin sauri ta kwashe kayanta da ta cire ta kai ɗakinta, sannan ta fito da takalmin Hamida 'yan tsini waɗanda ta manta shaf ba ta cire ba. Sai da ta fito harabar ta hango su ƙafarta, ta buga uban tsaki tana ƙara sauri ta ce,

"Ba za a cire ba, idan ta gani ta kashe ni."

Sai da ta leƙe ta kussuwar da ake ganin mutum kafin ta yi hanzarin buɗe ƙaramar ƙofar bakinta a washe. Cikin ladabi ta duƙa har ƙasa ta gaishe da matashin da ke riƙe da yarinyar da aka kawo a yi mata allura. Cike da jin daɗi ya amsa mata kafin ya ce, "Matar gidan tana nan?"

Bintoto ta yi hanzarin ɗaga masa kai har da nuna cikin gidan da hannu tana cewa,

"Tana ciki yanzu ta tashi daga barci."

"Yawwa, shi ya sa ba mu zo da wuri ba. Don Allah ki shiga da ita, ina nan ina jira, idan an gama yi mata allurar sai mu wuce. Tun da ita waccan wawuyar yarinyar ba ta san arziƙi ba. Haka kawai ta nemi faɗa masu gida daga taimako."

Maganganun da ya faɗa ya sa Bintoton ta gano da budurwar da suka yi faɗa yake, kuma tun da ta gan shi ta gano kamarsu. Hakan ya sa ta ƙara zama mutuniyar ƙwarai a gabansa tana sunkuyar da kai ta ja hannun yarinyar suka shiga gidan, sai da ta datse ƙofar da sakata sannan ta fara rawa har da ɗaga hannuwa tana faɗin,

"Daga ni sai ni sai ɗan ƙanen abokina ahayye."

Hannunta riƙe da yarinyar tana ta wara ido har cikin falon. Zama ta yi sannan ta karɓi ledar da ke hannunta ta fito da allurar da ƙaramin sirinjin da ta gani. Ranta fes

ta shiga jijjiga ruwan allurar kafin ta saka bakinta ta fasa kwalbar, cikin rashin sa'a ta yanke mata leɓe da gefen harshe fashe. Babu shiri ta jefar da komai ta dafe kai tana kiran wayyo bakina. Nan take jini ya dinga fitowa cikin tashin hankali ta nufi ɗakinta da gudu. Bakin ta tara a fanfo tana runtse ido har sai da ta rage jin jogi jinin ya tsaya sannan ta tofar da ruwan bakin tana faɗin,

"Wai Allah, da na kashe kaina a banza. Amma fa dole ne sai na yi mata allurar nan."

Ta fito tana shafa baki ta isa falon, sai da ta zauna ta huta sannan ta ƙara ɗauko wata kwalbar da ta gani ta saka gefen ɗankwalinta ta fasa. Cikin sa'a ba ta yanke ta ba kuma ruwan bai zube ba.

Jikinta yana rawa ta nutsa sirinjin a cikin kwalbar ta zuƙo ruwan maganin. Cikin nishaɗi ta kwashe ruwan tana 'yan waƙe-waƙenta ta ajiye kwalbar ƙasa. Ba tare da ta saita ruwan ta cire iska ba, a yadda ta zuƙo a haka ta koma kan wata kujera tana nishi ta ce da yarinyar ta zo. Yarinya za ta yi kuka ta zare mata ido ta ce,

"Idan na ji kukanki har a cikin ido sai na yi miki allura. Ai da ma na faɗa, abin da yayarki ta yi mini sai na rama a kanki ko a kanta. Don haka ga shi Allah Ya kama mini ku har gida kin dawo kin same ni. Matso na ce!"

Ta ƙare maganar cikin faɗa, yarinyar ta ƙi zuwa, ta ƙame wuri ɗaya tana ciccika tare da kallon ƙofar shigowa. Bintoto ta taso ranta a ɓace ta dungure mata kai kafin ta ce,

"Wallahi ko mutuwa za ki yi sai na yi miki allurar nan. Da ma kin tsaya na yi miki a hankali."

Yarinya ta fashe da kuka, amma hakan bai hana Bintoto dunƙule ta ta ɗage mata riga da wando ba, kafin ta saita allurar daidai tsinin ɗuwawunta ta tura mata allura. Yarinya ta zabura ta ƙara taushe mata kai, sai da ta juye mata ruwan da iskan duka da ke cikin sirinjin sannan ta sake ta tana faɗin,

"Don ubanki ko gobe kika dawo ni zan yi miki allurar tun da na iya."

Yarinya tana ta kuka ta mayar mata da wandonta, sai da ta gyara falon tana yi wa yarinyar faɗa a kan ta yi shiru sannan ta ja ta tana sosa inda ta yi mata allurar, jini har ya ɓata doguwar rigar atamfar da ke jikinta. Amma ko kaɗan hankalin Bintoto bai kai can ba, a haka ta buɗe gidan tana ta rarrashin ta har gaban yayan nasu. Tana ɓata fuska ta ce da shi,

"Ashe kukan allura take yi. Gabaɗaya ma yau ƙin tsayawa ta yi da ƙyar Anti ta samu ta yi mata allurar."

"Ai babu komai tun da an gama. Ki ce da ita mun gode Allah Ya saka da alheri."

Ya ja hannunta tana ta kuka suka wuce, Bintoto ta rufe gidan tana ƙyalƙyala dariyar mugunta ta koma ciki.

kitchen ta nufa, a can ta tare tana ta tsince naman miyar da Hamida ta rage, wadda ta haɗa tun da sassafe, sannan ta yi pride rice ta cika kula ta tafi ta kai gidansu. Sauran kuma ta bari da niyyar idan ta dawo ta sarrafa ta a ci abincin dare.

Amma gaba Bintoto ta saka nama tas ta cinye, ta nemo wuƙa ta dinga yanka plantain tana ci haka nan ba tare da ta soya ba. Ta buɗe firiza ta hango soyayyen nama, jikinta har rawa yake yi wajen zura hannu fiddo bokotin. Zaman dirsham ta yi a gaban firizar tana tsoma hannu tana ciro shi yana hayaƙin sanyi, ɗaya bayan ɗaya ta dinga ci tana rawar baki tare da runtse ido. Sai da ta ji tana shirin yin amai sannan ta mayar da shi inda ta gan shi, ta rufe tana nishi ta fito kitchen ɗin. Daidai lokacin da ta ji ana ta bubbuga gidan, ƙirjinta ya ƙire ya faɗi dam-dam. Amma hakan bai hana ta buɗe firij ɗin falo ta sha ruwa ba kafin ta fice tana gyatsa.

"Innalillahi!"

Abin da ta furta kenan saboda ganin yayan yarinyar da Innarsu saɓe da yarinyar har lokacin ba ta daina kuka ba, tare da budurwar da suka yi faɗa ta riƙe ƙugu sai ciccika take yi tana bubbuga ƙafa ƙasa. Sannan da wasu mutane a bayan su sun yi cirko-cirko.

Bugun da aka sake yi wa ƙofar gate ɗin ya sa ta yi hanzarin faɗin, "Masu gidan ba su nan."

"Wurin ki muka zo ba wurin masu gidan ba!"

Yayan yarinyar ya faɗa cikin fusata. Bintoto ta leƙo kanta cikin kussuwar gate tana cewa, "To ni me na yi muku da za ku zo wurina? Idan ma allura ce ita yarinyar da kanta ta ce na yi mata tun da Anti ba ta gid..."

Wata kalar ashar da budurwar ta lailayo mata ce ta saka ta zura hannu ta kussuwar gate ɗin ta yi mata daƙuwa tana cewa,

"Ubanki dai ba ubana ba. Ai ba ni na ce ta ce na yi mata allura ba. Da za ku yo gayya kuna muzurai da ido wai har da Innark...."

"Kada ki faɗa mana maganar banza na diro cikin gidan na ci uban kakan Babanki! Wani za ki yi wa iskanci bayan kin gama yi wa yarinya mugunta! To wallahi ko ki buɗe gidan cikin mutunci ko na je na ɗebo miki 'yansanda. Da ma can darajar masu gidan ya sa ba mu ɗauki mummunan mataki a kanki ba, mun zo a yi magana kuma shi ne za ki raina wa mutane hankali don uban Babanki?"

Yayan yarinyar ya faɗa cikin tsananin fushinsa da Bintoto ta gama kai wa bango. Hango motar Aliyu da ya yi ya saka shi ja baya yana gyara rayuwarsa tare da sunkuyar da kai ƙasa. Bintoto kuma jin ya yi shiru tana kumbura leɓo ta ce,

"To ai haƙuri za ku yi. Saboda ni ma ba da son raina na yi mata allurar b..."

Tsayuwar motar da ta ji a ƙofar gidan hantar cikinta ta kaɗa, don a tsammaninta ko 'yansandan ne ya ɗebo mata kamar yadda ya yi iƙirari. Da sauri ta leƙa kanta ido tsakar ka ta dafe kai alamun haushi da takaici, don ba ta so su Hamida suka dawo gidan a daidai lokacin ba. Musamman da take tare da maigidan, saboda ta san ko Hamida ta tausaya mata shi ba raga mata zai yi ba.

Ganin mutane a ƙofar gidan tun daga nesa Hamida ta fara faɗin, "Wallahi yanzu haka Fatima ce ta sake jawo mana jarfa."

"Wace ce Fatima?"

Ya faɗa idonsa a ƙofar gidan, don har ya manta da wata Bintoto da suka bari a cikin gidan. Hamida ƙirjinta yana bugawa ta ce,

"Yar aikinmu mana."

"Mahaukaciyarki dai."

Yana maganar ya yi parking ya fito idonsa a kan mutanen da su ma shi suke kallo, kafin Hamida ta fito kallon ya koma kanta. Cike da mamaki ta dinga taku cikin sanyin jiki ta isa inda Mamar yarinyar tana faɗin,

"Mama lafiya na gan ku a nan haka?"

Kafin su ba ta amsa Bintoto ta buɗe gidan ta fito tana faɗin, "Ita fa ta ce na yi mata allura tun da ba kya gida, amma shi ne don kawai a ce na yi laifi aka zo har nan ana so a kai ni wurin 'yansanda.....yiiiii!"

Ta ƙare maganar cikin fashewa da wani kalar kuka tamkar wadda aka shaƙe wa wuya. Mamakin da ke fuskar Hamida ya ƙaru, ganin Bintoto da tsadaddun kayanta da take mugun so, sannan da takalminta na fita kunya. Ƙarin firgici jin abin da take faɗa, wanda alamu ya nuna ƙarara allura ta yi wa 'yar mutane da ba ta nan.

Kanta kawai ta dafe tare da yin baya taga-taga tsabar fita hayyaci tana faɗin,

"Innalillahi wa inna ilaihirraji'un!"

Cikin sauri Aliyu ya tare ta gudun ta faɗi. Idonsa a kan Bintoto ya dinga wurga mata wani kalar kallon da shi kansa bai san kalar hukuncin da ya dace ya yanke mata ba.

To ni ma na yi kudu

Princess Dija.

29.

"Fatima kin cuce ni. Ban taɓa tunanin haukarki da Baban Baby yake faɗa har ta kai haka ba. Yaushe kika iya allura da za ki yi wa yarinyar mutane?"

Bintoto ta yi tsuru-tsuru da iso tana turo baki tare da sosa kai alamun ta rasa abin faɗa da rashin gaskiya ƙarara. Haushin da ke shirin kai Hamida ƙasa ya sa ta ƙara yin magana a ƙufule tana kallon Mamar yarinyar tana faɗin,

"Mama, ku ɗauki duk hukuncin da kuka ga ya dace a kanta, wallahi babu ruwana saboda ban ma san ta aikata ba. Yanzun nan ma da kuka gan mu daga gidanmu muka fito, na je ganin Babana da ke fama da ciwo kwana biyun nan. Tun da har ta yi gaban kanta, ku ma ku yi mata duk abin da kuke so ita ta jawo wa kanta."

Tana gama faɗar hakan ta buɗe gidan ta shige, ta bar Bontoto da waɗanda ta yi wa laifin suna ta hararar juna, tana yi musu kallon ƙasan ido tana zagin su a zuciya, su ma suna aika mata mugun kallo mai ɗauke da harara, a ransu kuma suna jin kamar su rufe ta da duka har sai ta daina motsi.

Yayin da Aliyu yake gefensu yana waya, saboda tun da Hamida ta fara magana aka kira shi, yana gamawa ya juyo wurin su ransa a ɓace ya shiga ba su haƙuri yana cewa,

"Abin da ta aikata ganganci ne, don haka ko da zan ce ku yi haƙuri; ba zan hana ku ɗauki matakin da kuka ga ya dace ba, idan har kuna da ra'ayin yin hakan. Saboda ni kaina a yau kuma a yanzu za ta bar mini gidana, don na gaji da halinta. Amma idan kuka tashi har garinsu zan iya kai ku matuƙar kuna da buƙatar hakan. Da ma can zaman da muke yi da ita a cikin gidan ba don ina so ba, Hamida ce take son zamanta kuma yanzu ga abin da ta jawo mata. Don haka ku je ku kai yarinyarku asibiti a duba muku lafiyarta, duk abin da ke nan ni zan yi muku jagora har wurin kakartarta a yi duk abin da za a yi, idan ma rufe su kuke so ku yi kuna da damar hakan don sun cancanta."

Daga haka ya ja bakinsa ya tsuke, bayan ya ciro kuɗi daga aljihunsa ya bai wa yayan yarinyar, da nufin a kai ta asibiti gudun a bar abin daga baya matsala ta biyo. Mamarsu ta ce babu komai, amma fuskarta cikin rashin walwala suka tafi, budurwar kuma sai da suka yi gaba ta dawo a fusace ta dinga kai wa Bintoto duka. Kafin ka ce me suka dinga kokawa, nan take ta kai Bintoto ƙasa ta taushe, ko da aka raba su tana saman cikin Bintoto tana ta duka. Don da ma can ta ci burin sai ta dake ta ganin yadda aka bar ta babu wanda ya yi yunƙurin saka mata hannu.

Mutanen da suka taru ƙofar gidan suka dinga yi wa Bintoto saukale kowa da abin da yake faɗa a kan rashin hankalin da ta aikata. Aliyu dai cikin gidan kawai ya nufa, mintuna a tsakani ya fito da jakar kayan Bintoto ya wurga mata a jiki. Ta ƙara fashewa da kuka tamkar wadda aka yi wa mugun naushi. Hamida da ke bayansa ta rufe gidan sannan ta shiga mota, cikin ɗaga murya Aliyu ya leƙo kansa yana faɗin,

"Za ki shigo ko sai na taka kanki wurin nan?"

Sanin da ita yake, ta tallabi jakarta tana haɗe rai ta buɗe motar ta shiga ta zauna rungume da jakar kayanta. A ranta tana faɗin,

'To don kun kore ni sai me? Ai dai ba shi zai sa na mutu ba. Ni ma zama gidan naku ya fita kaina tun da ba mutunci ne da ku ba. Abu kaɗan ku saka mutum gaba ku yi ta masa faɗa sai ka ce ku kuka haife ni"

"Mitsss!"

Ta ƙare zancen da jan ɗan ƙaramin tsaki, wanda ya sa Hamida faɗin,

"Kanki kika cuta Fatima, don wallahi kin gama sire mini a rai gabaɗaya. Wai ma saboda tsabar kin raina ni har ɗakina kika shiga kika ɗauko mini kaya kika saka. To ki je an bar miki idan kika tashi mutuwa a rufe ki da su cikin ƙabarinki."

Aliyu ya yi hanzarin ƙumshe dariyar da Hamida ta so ba shi yana cewa, "Tun farko sai da na ce miki yarinyar nan mahaukaciya ce, amma ba ki yarda ba. Babu yadda ban yi da ke ba a kan ta bar gidan kika ƙi yarda, to ai ga inda rashin hankalinta ya kai ki. Don ta saka ki jin kunya da mutanen da ke ganin mutuncinki, kuma wallahi duk abin da ya biyo bayan hakan babu ruwana. Ki san yadda za ki yi da su kun fi kusa, tun da ke kika ɗaure wa wannan shashashar ƙugu tana ci gaba da iskanci son ranta."

"Wallahi na ɗauka za ta gyaru mu samu lada."

"To ai ta gyarun har kin samu ladar."

Hamida naushin maganar ranta ya ƙara matuƙar ɓaci, har da guntuwar ƙwalla maƙale a cikin idonta tsabar jin takaici da haushin kunyata ta da Bintoto ta yi. Haka suka isa gidan su Hajiya kowanensu zuciya babu daɗi, suna shiga harabar gidan, Bintoto ta ɗaga kai tana so ta gano da gaske wurin 'yansandan ne ya kawo ta. Fahimtar gidan Hajiya ne ta yi hanzarin hararar ƙeyarsa a ranta tana faɗin,

'Yo idan gidan nan ne ai ni na ma fi son shi a kan baƙin gidansu. Ba su da aiki kullum sai masifa yen yen yen.'

Tun kafin motar ta gama daidaitawa ya isa inda ya yi niyyar tsayawa ta ɓalle murfi tana ƙoƙarin ficewa, a fusace ya zuro hannu ta baya ya kai wa kanta duka har sai da ta daki gefen motar yana faɗin,

"Ƙatuwar wawuya! Sai kin kashe kanki garin iskancinki mai lasisi."

Bintoto ta ƙame wuri ɗaya ta kasa gaba ta kasa baya, har ya fito daga motar ya ƙara kai wa kanta bugu ta kauce, bayan ya tura ta gaba yana cewa,

"Wannan shegen kan naki watarana sai na fasa shi idan ba ki yi hankali ba. Kai sai ka ce ƙaton mangwaro babu komai a ciki sai shirme da hauka. Dalla kwashi jakar tsommakaranki mu je ciki a yi ta ƙare da Hajiya, don wallahi kin gama zama gidana daga yau sai ƙauyenku."

Sai da ya saka ta gaba sannan suka rufa mata baya har cikin gidan bai daina sambatun faɗan da yake yi ba. Ai kuwa tana jefa ƙafarta cikin falon gidan ta fashe da kuka, Hajiya ta fara salati a ruɗe tana tambayar wa ya taɓa mata uwa, kuma me ke faruwa ta gan ta da jaka.

Aliyu zama ya yi babu jinkiri ya juye wa Hajiya duk abubuwan da take aikatawa, kafin Hamida ta ɗora da faɗar abubuwan da bai sani ba da wanda ya mance. Salati Hajiya ta dinga yi tana tafa hannu, musamman da ta ji labarin ta yi wa yarinyar mutane allura.

Shiru ta yi tsawon mintuna tana jimamin abin kafin ta kalli Bintoto ta ce,

"Mai sunan uwata me ya sa kika yi wannan shirmen? Yanzu idan ƙafar yarinyar mutane ta lalace ya za ki yi idan an kai ki hukuma? Kakarki tana fama da kanta ki jawo mata fitina, to gaskiya ko ni ba na goyon bayanki a nan. Ba ki kyauta ba, sannan kuma ba ki yi wa uwarɗakinki adalci ba. Tana ƙoƙarin ganin ta gyara ki amma ke kin hana wa kowa zaman lafiya a gidan da maƙota. To yanzu zan kira Hari na sanar da ita komai, su zo su tafi da ke tun da haka kike so sai ki koma gid...."

"Don Allah a yi mini haƙuri wallahi ba zan sake b..."

"Ke ɗin ce ba za ki sake ba? Ai ko kashe ki aka yi kika dawo duniya sai kin tafka tsiya."

Aliyu ya faɗa yana miƙewa tsaye cikin fushi ya ce, "Zo mu tafi Maman Baby."

Hamida ta miƙe da Baby a hannunta suna yi wa Hajiya sallama, kanta a kan waya tana ta ƙoƙarin nemo lambar Hari. Suka fice Bintoto ta raka bayansu da harara cikin haɗe rai ganin da gaske tafiya za su yi su bar ta. Sai a lokacin ta ji takaicin kanta da abin da ta aikata. Ganin da gaske shikenan ta rabu da gidan jin daɗi za a mayar da ita ƙauyensu ba tare da ta yi kuɗin da take buri ba. Asali ma babu wani mai kuɗin da ya gan ta ya ce yana son ta, talakan ma tun da ya zo sau ɗaya bai dawo ba.

Bayan Hajiya ta gama waya da Hari ta ce da 'yan aikinta su kawo wa Bintoto abinci. Tana ci tana gunguni saboda duk abin da Hajiya ta tattauna da Hari tana ji.

Don Hari ta so ko ita Hajiyar ta riƙe ta idan akwai abin da za ta dinga yi mata ko da wanke-wanke ne. Amma Hajiya ta nuna ita sam ba za ta iya zama da ita ba gudun ta jawo mata wata fitinar kamar yadda ta yi wa su Hamida.

Marece sakaliya Hari ta iso gidan ita kaɗai, saboda ba ta faɗa wa Kandala abin da ke faruwa ba, don ko da Hajiyar ta kira ba ta nan tana wurin aikinta. Da niyyar sai idan ta dawo ta sanar da ita duk abin da ya faru, Bontoto tana ganin Harin ta fashe da kuka tana faɗin,

"Wallahi Inna na yi alƙawarin duk abin da nake yi zan daina. Don Allah ki ce ta matsa wa ɗanta na koma gidans...."

"A'a kam ba kya son zama gidan, da kina so da ba ki yi wa 'yar mutane allura b....ni sake ni!"

Ta ƙare maganar cikin ɗaga murya saboda jin haushin an kore ta a lokacin da take son ganin ta shiryu. Hari ta saka Hajiya gaba da magiya tare da ban haƙuri har ta samu ta shawo kanta, a kan Bintoto za ta zauna gidan, amma a bisa sharaɗin duk ranar da ta yi musu rashin hankali a bakin aikinta. Hari ta aminta da sharaɗin, sannan ta ja Bintoto bayan ɗakunan gidan ta dinga zuba mata faɗa, har da ranƙwashi da jan kunne kala-kala, sai da ta tabbatar ta yi laushi sannan ta ja

hannunta suka koma ciki. Inda a gaban Harin Bintoto ta ƙara bai wa Hajiya haƙuri tare da ɗaukar alƙawarin ba za ta sake kwatanta laifin da take yi ba.

A nan Hari ta yi sallama da su ta tafi, Bintoto kuma aka ce ta kai jakar kayanta ɗakin 'yan aikin gidan. Bayan tafiyar Harin ma Hajiya gaba ta saka ta tana ta yi mata faɗa a kan ta bar abubuwan da take yi. Sannan makarantar da aka ce an saka ta za ta ci gaba da zuwa. Tun da an kashe kuɗi ba za a bari su bi iska ba. Bintoto ta yi mata alƙawarin za ta tsaya ta yi karatu.

Daga haka Hajiya ta sauko daga fushin da take yi da ita. Don da ma can takaicin abin da ta ji ta aikata ne ya sa ta nemi rabuwa da mai sunan uwarta, wadda ba ta haɗa ta da kowa a duniya ba. Safiyar Litinin Bintoto ta yi shirin makaranta tun da asuba, ko da bakwai ta yi kowa ya gan ta da shirinta har da jakar makarantarta a baya. Hajiya ta sa direbanta ya kai ta har makarantar, sannan aka yi mata bayanin idan an tashi ta jira Bus ɗin makarantar za ta kawo ta har bakin titin unguwar sai ta ƙaraso. Idan ma ba za ta gane ba za a sa wani ya tsaya wurin da an sauke ta a nuna mata hanyar dawowa gida.

Cikin zumuɗi ta tafi, saboda farin cikin an kai ta cikin motar masu kuɗi. Ko da aka sauke ta tana wani bouncing da hurar hanci don a gano da gaske ita ɗiyar masu kuɗi ce. Kai-tsaye wurin assembly ta nufa, inda ta ga ɗalibai suna ta zuwa suna layi, kasancewar ba ta san kan komai ba ta shige layin da take ra'ayi. Sai dai tana shiga ake ture ta a ce ba layin ajinsu ba ne. Kafin ka ce me a gaban wurin ta yi kokawa da mutum ya kai uku, a ƙarshe wata prefect ta hango ta ta saka ta duƙawa. Ganin ta kamar girmansu guda ta ƙi yin abin da ta ce ta yi, yarinyar ta ɗaga bulala tana zabga wa ƙafafuwan Bintoto. Ita ma ta taƙarƙare ta cakumo hijabinta tana ƙoƙarin kai mata naushi.

Yan'uwanta prefects suka taru a kan Bintoto suna ta jibga, da wani malami ya gan su ya tambayi dalili suka sanar da shi. Da bayanin da Bintoton ta yi masa ne ya gano ba ta san komai a kan tsarin Makarantar ba. Shi ne ya yi mata bayanin komai, sannan ya ba su haƙuri suka ƙyale ta. Amma sun ci alwashin duk ta sake shiga gonarsu sai sun sauya mata fuska.

Lokacin da aka gama assembly aka shiga aji, a nan ma sai da ta yi faɗa da wata da ke yi mata dariya tana cewa babba cikin 'yan yara. Hakan ya sa ko da ta shiga ajinsu kowa ba ta yi wa magana ba. Su ma saboda an hana su tsokanarta babu wanda ya bi ta kanta. Sai da aka tashi break ta ga yadda kowa yake fito da abinci, sannan ita ma ta fito da kular da Hajiya ta saka mata a kwando.

Tana yauƙi take cin dankalin turawan da ya sha jar suya har da wainar ƙwai gefe. Tas ta cinye ta sha ruwa, kuma babu wanda ta yi wa bisimillah. Amma ita idonta yana kan abincin yaran mutane tana dogon wuya. Idan aka taya mata jiki yana rawa take zuwa ta jefa hannu, ko da mai abinci za ta ankara har ta tashi da komai ta bar yara da mamaki. Haka ta dinga yi kujera-kujera tana leƙen me suke ci. Wasu su ba ta wasu kuma su hana ta, ranta fes tana shafa cikinta ta tabbatar da ba ƙaramin ƙoshi ta yi da abincin yaran mutane ba.

Lokacin da aka tashi Bus ta ajiye ta bakin titin su Hajiya. tana tsaka da wara ido ta hango ɗan saurayinta mai jiran dawowarta tsawon lokaci. Tana ƙoƙarin bin wata hanya ta ji magana a bayanta ana faɗin,

"Kada ki je ki ɓata, zo na nuna miki gidan."

Da mamaki ta bi shi da kallo kafin ta ce,

"Amma dai kai aljani ne ba mutum ba."

Yana 'yar dariya ya ce, "Me ya sa na tashi daga mutum na koma aljani?"

"Saboda ban san wa ke faɗa maka inda nake ba sai dai na gan ka kawai."

"To daina mamaki, tun jiya da kika yi laifi aka dawo da ke nan unguwar na biyo ki na ga gidan."

"Kammmm!"

Ta faɗa tare da riƙe ƙugu ta dakata daga tafiyar da take yi. Tsabar mamaki da jin haushin wai har ya san ta yi laifi an koro ta. Hakan ya sa ta haɗe fuska tana nuna shi da hannu ta ce,

"Wai ba na ce kada ka sake yi mini magana ba? Sau nawa zan faɗa maka ban san ka ba? Kai idan ma na san ka ni ba na son talaka yana yi mini magana, haka kawai mutum ya goga mini warin talauci a banza ya sa tsiya ta shafe ni ina cikin arziƙina."

Murmushi a kan fuskarsa ya ce, "Yanzu dai ban da wani laifi a wurin ki sai zamana talaka?"

"E, ka je ka yi kuɗi kamar yadda na yi ka gani idan ban dinga kula ka ba."

"Haka kika ce?"

"E, haka na faɗa ka je ka yi kuɗin ka gani. A duniyar nan me ake yi da talauci? Ai tsananina da shi kallo daga nesa ina yi masa bye-bye."

"Zance ya ƙare, idan na yi kuɗi za ki aure ni?"

Sai da ta yi masa kallon sama da ƙasa sannan ta ce, "In dai kana da kuɗi ko ba na son ka zan aure ka. Amma fa sai idan kana ba ni kuɗin ina sakawa cikin asusuna zan tabbatar da kai mai kuɗi ne."

"To, ga gidan can ki ƙarasa, in sha Allahu daga gobe zan fara zama mai kuɗi."

Ya juya cikin wani yanayi a kan fuskarsa, ita ma ta yi gaba tana hura hanci ta ce, "To ai ka yi kuɗin mu gani tun da kuɗin banza ne."

Ta tafi tana dariya, har da waigawa tana kallon bayansa tana ci gaba da dariya ta ce, "Baƙin aljani, da haka zan kore ka kada ka shafa mini tsiya a banza."

Ba giri-girin ba dai....😄

Princess Dija.

30.

Da wani kalar nishaɗi ta shiga gidan, don tun daga nesa ta gane gidan ne, ta shige tana waige-waige tana cewa,

"Bari dai na ƙara kallon unguwar da kyau kada na ɓace watarana. Ba don wancan mayen ba da yau na ɓace a cikin birnin nan 'yan yankan kai su sha jinina a banza. Tun da Hajiya ta yi mini ƙarya ba ta turo kowa da zai nuna mini hanyar ba."

Tana tafiya tana maganganu har ta shige cikin gidan, kamar almara ta hango Kandala da Hari cikin falon suna hira da Hajiya. Wani uban tsalle ta daka tare da ihun kiran sunan Kandala ta yi kanta ta faɗa a sukwane, tsabar jin daɗin ganin su. Baki har kunne ta dinga matso fatar kumatun Kandala tana faɗin,

"Kandala kun zo gidan amma ko ku ce mini ga ku nan na yi sauri."

Hajiya ta taryi zancen tana cewa, "Ai duka laifin nawa ne uwata, shaf na manta da zancen saka wani ya taro ki. Yanzun nan muke maganar ma, ina da niyyar na tura wani ya zo da ke sai ga ki kin dawo. Amma tun da kin gane hanyar ai shikenan gobe ba sai wani ya yi miki jagora ba."

Bintoto ta ɓata fuska tana wasa da gefen hijabinta tana cewa, "Bayan har na tashi ɓacewa."

Gabaɗaya suka saka dariya. Kandala sai kallon Bintoto take yi tana jin daɗi a ranta. Ganin yadda ta sauya a lokaci ɗaya wani girma ya taso mata na ban mamaki. Ga haske da ta yi jikinta ya mulmule alamun zaman birnin ya karɓe ta. Da ma can ba ta da muni idan aka cire baƙin da Allah ya yi wa fatarta fenti da shi. Amma kuma baƙin mai kyau ga kyakkyawar ƙira irin ta ɗiya mata. Matsalarta ɗaya shirme da wautar da suka yi wa kanta yawa kuma suka zarta shekarun haihuwarta a duniya.

Hajiya ta ce ta tashi ta cire kayan makarantar ta ci abinci ta dawo. Ta miƙe ba don ranta ya so ba tana waigen Kandala tana dariyar jin daɗi har ta shige. Suka bi ta da dariya ganin yadda take yi alamun ba ƙaramin farinciki take ciki ba, saboda ganin ba zatan da ta yi musu kamar almara. Don tun ƙarfe huɗu suke gidan, sun zo bai wa su Hajiyar haƙuri a kan abubuwan da ta aikata.

Saboda Kandala ba ƙaramar kaɗuwa ta yi ba a lokacin da Hari ta rattaba mata duk abin da ya faru. Har ta fara faɗin a dawo mata da Bintoto su koma ƙauyensu tun da zaman birnin bai karɓe su ba. Faɗa ta dinga yi sosai a kan don me su Hamida za su kori Bintoto a gidansu, ba tare da sun yi mata uzuri har sai ta sake ba. Da ƙyar Hari ta fahimtar da ita illa da haɗarin da ke cikin yi wa yarinyar mutane allura ba tare da ta san ƙa'ida da dokokinta ba. A nan Kandala ta shiga tsoro da fargaban kada ƙafar yarinyar mutane ta samu matsala a haɗa su da hukuma, kamar yadda Hari ta tsorotar da ita ganin duk laifukan Bintoto da ta lissafa ba su sa ta gano ta yi kuskure ko wani babban laifi ba.

Bintoto bayan ta cire kayan da abincin ta dawo falon ta zauna saman cinyar Kandala kamar wata 'yar yarinya tana cin abincin, har sai da ta ture ta tana faɗin,

"Saukar mini ƙafa ja'ira! Tun da ba ki jin tausayin tumurmusa ni kamar kin samu jaka."

"Daga ma kin samu na zauna saman ƙasusuwa, cinyar taki ma da ko naman kirki babu."

Dundu Kandala ta sakar mata a baya tare da aika mata daƙuwa tana faɗin, "Rodi ne kika hau ba ƙashi ba, 'yar rainin hankali. Shegen son jiki ko mage albarka."

Ta daina cin abincin tana kumbura fuska tare da ƙamewa wuri ɗaya alamun ta yi fushi. Hajiya ce ta yi saurin faɗin, "Yi haƙuri uwata, ai nan gaba kaɗan 'ya'yanki ne za su hau cinyar har su yi mata fitsari a jiki."

Babu shiri Bintoto ta ƙyalƙyale da dariya tana faɗin, "Wallahi har kashi sai na sa an yi mata a cikin baki."

Gabaɗaya suka saka dariya, daga haka ta saki jikinta tana cin abincin suna ta hira. Har ƙarfe shida da rabi ta buga Hari ta ce su tafi gida kada magriba ta yi musu a hanya.

Bintoto ta riƙe hannun Kandala tana matsar ƙwalla a kan cewa ita sai ta bi su. Hajiya da Hari suka dinga ba ta haƙuri a kan ta bari idan Jumu'a ta yi sai ta je can ta yi hutun ƙarshen mako. Amma atafau ta ce ba ta san zancen ba, ita lalle sai sun tafi da ita. Sai da Hari ta haɗa mata da jan ido sannan suka tafi suka bar ta. Bayan ta sake yi mata faɗa da jan kunne a kan ta nutsu ta yi abin da ake so, idan kuma ta sake yin wani laifi ƙauye za su komawa gabaɗaya a fasa zaman birnin.

Har sun fice gidan Bintoto ta ƙwala wa Kandala kira suka tsaya, ta isa inda suke da gudu ta kama kunnen Kandala tana yi mata raɗar cewa,

"Wani ya ce yana so na, amma talaka ne ba na son shi."

Kandala ta dungure mata kai tana faɗin, "Sannu ɗan wake ka fi ubanka. To Amadun Jaririy ma har gobe da riga ɗaya yake yawo a gari. Amma ke har kin samu wuri kina kiran wani da sunan talaka. To ki jira mai kuɗin da bai da hankali ya zo ya ce ke yake so."

"Ni wallahi sai mai mota zan aura."

"Ki so mai jirgin sama ba mota ba. Mu tafi Hari, wannan 'ya taki watarana sai na ɓalle mata haƙarƙari idan ba ta bi ni a sannu ba. Wai ita nan da ita har ta san ta ce ba ta son talaka, saboda ƙaruna ne uban da ya kawo ta duniya."

Hari dai biye take da Kandala kawai tana dariya, ganin yadda Bintoto ta dinga aika mata harara tana turo baki tun da ta kira sunan Babanta. Da ma ita idan ana son ganin ɓacin ranta a lokaci ɗaya a kira sunan Amadun Jaririya.

A ƙufule ta juya bayan ta ɗaga murya tana cewa, "Na fasa zuwa gidan naku ma ko an kai ni ba zan zauna ba."

"Kada Allah Ya sa ki zo mashirmanciyar banza."

Haka suka rabu suna faɗa, amma hakan bai hana Kandala waigen gidan ba bayan Bintoto ta shige. Da kuɗin da Hajiya ta ba su suka hau abin hawa har suka raba canjin da ya rage. Bayan sabulu da klin da ta ba su ta ce su yi wanki. Har cikin zuciyar Kandala, ta yi farinciki da albishirin da Bintoto ta yi mata a kan mai son ta. Da ma ita babu burin da take kwana take tashi da shi kamar a ce Allah Ya ara mata rai ta aurar da ita, ko da za ta ga ɗiyan da za ta haifa da idonta.

Hakan ya sa tun a kan hanya ta fara yi wa Hari zancen auren Bintoto da abubuwan da ya dace ta saya da ɗan abin da take samu a inda take aiki. Hari ta ba ta shawarar su fara sayen tukane da wasu abubuwan da ba za su yi saurin lalacewa ba. Ai kuwa Kandala ta kwance ƙullin zanenta da ke maƙale a ƙugunta tana faɗin,

"To ke zan bai wa kuɗin ki sayo mata ko tare za mu je na zaɓo waɗanda nake so?"

Hari tana dariya ta ce, "Ƙafata ƙafarki Inna, ai da ke za mu je a yi komai da ke ki gani da idonki."

"To, shikenan Hari. Hakan ma ya fi mini gaskiya, idan kuma sai na koma gida na sayar da akuyoyina da tumaki sai na haɗa kan kuɗin wuri ɗaya mu ga abin da zai samuwa."

Hari ta ba ta shawarar ta bari sai Bintoto ta zo gidan, sai su haɗu gabaɗaya su tafi ƙauyen su yo ganin gida, sannan duk abin da ta ga ya dace ta yi kafin su baro garin sai ta yi. Da haka suka tsayar da magana, ran Kandala fes tsabar farin ciki da jin daɗin ta kusa aurar da Bintoto. Bayan ko mijin ba ta sani ba, sannan kuma ba ta san komai a kansa ba hatta sunansa.

Bintoto kam, ba ta tashi jin kewar Kandala ba sai da dare ya yi. Lokacin da ta kwanta bayan dattijuwar mai aikin Hajiya, ganin ta ɗora mata ƙafa a jiki ta ture ta tana faɗa, sai abin ya ba ta haushi. Cikin fushi ta tashi ta bar mata ɗakin, a ƙarshe a falo ta kwana kan kujera tana juyi tare da mafarkin Kandala kala-kala.

Da safe ma ba don tana so ta je makaranta ba. Gabaɗaya karatun ya fita kanta, saboda matsa mata da ake yi sai sun yi sallar Zuhur da Asr a cikin jam'i. Sannan ga shi ba komai ta sani ba, malamai su yi ta matsa mata da tambaya yara suna yi mata dariya. Amma tana tuna kalolin abincin da take ci daga ɗanɗane ta yi musu wayo; ta dinga murna har da tsalle-tsallenta ta isa bakin titi. Inda Bus ta ajiye ta a nan ta zo ta ɗauke ta suka wuce.

Lokacin da aka tashi ma tana fitowa ta hango wata mota ta nufo ta. Cike da tsoro ta ja baya, abin mamaki ta ga an yi gaba an tsaya, idonta a kan motar har wanda ke ciki ya fito. Babu shiri ta zaro ido tana nuna shi da hannu tana faɗin,

"Wai da ma kai ne?"

"Ni ne."

Ya faɗa yana wani boƙarewa tare da murmushi a kan fuskarsa. Bakinta ya kasa rufuwa har ta isa jikin motar ta shafa ta tana faɗin,

"Wannan motarka ce?"

Ya ɗaga mata kai yana ci gaba da murmushi ya saka hannu cikin aljihunsa ya fiddo dubu biyu 'yan ɗari biyu guda goma ya miƙa mata. Jikinta yana rawa ta karɓe tare da yin wani tsallen jin daɗi tana faɗin,

"Yaushe ka yi kuɗi kai kam?"

"Tun a ranar da kika ce mini ba kya son talaka."

"Innalillahi!" Ta faɗa tare da rufe bakinta cikin tsantsar farinciki tana kallon kuɗin kafin ta koma lissafawa.

"Yanzu don Allah duk ni kaɗai ka bai wa waɗannan kuɗin?"

Ya ɗaga mata kai yana murmushi cike da jin daɗin ya samu kanta cikin ɗan lokaci. Kafin ya nufi motar yana cewa,

"Zo mu je na ajiye ki gidan."

Babu dogon nazari ta buɗe motar ta shige tana kallon sa, cike da mamakin ganin ya yi kuɗi kamar almara. Hakan ya sa ta sake kallon cikin motar da kujerun baya kafin ta dawo da kallonta gare shi ta ce,

"To amma yaushe za mu yi auren?"

"Ko gobe kike so zan aure ki. Saboda ina da ƙaton gidana, kuma ga mota na saya, kuɗi ma ina da su ko nawa kike so zan ba ki."

"Da gaske."

Ta faɗa tana wata zabura, tsabar ya gama kai ta maƙurar daɗi ganin burinta ya cika za ta auri mai kuɗi. Tuno abin da ke ranta ta yi hanzarin gyara zamanta tana cewa,

"Za ka kai ni Makka?"

"Abu mai sauƙi. Har wasu ƙasashen ma zan kai ki mu je mu yi yawon shaƙatawa idan kina so."

"Yeeee!"

Ta yi ihu mai cike da tsalle, daidai lokacin da ya ajiye ta a ƙofar gidan ta fita da gudu, tana ƙoƙarin shigewa ta dawo da sassarfa tana haki ta ce da shi,

"Ba ka faɗa mini sunanka ba."

Yana 'yar dariya ya ce, "Sunana Jabir."

Sai da ta kira sunan sannan ta rufe fuskarta ta buɗe, tana wasar baki ta ruga da gudu ta faɗa cikin gidan. Ko sallama ba ta yi masa ba ballantana godiya saboda murnar banza ta samu burinta ya cika cikin sauƙi.

Baki sake ta samu Hajiya har cikin ɗakinta ta sanar da ita aurenta ya kusa. Mamaki da al'ajabi ya kama Hajiya, saboda ganin idonta ƙyam a kanta babu kunya ko shayi, ta sanar da ita ba za ta sake zuwa makaranta ba ta samu miji mai kuɗi za ta yi aure. Da dabara Hajiya ta nuna mata ai aure dole ne sai ta yi. Amma makarantar ma ba za ta fasa zuwa ba ko da ta yi auren. Kuɗin da ya ba ta ma ita ta miƙawa ta ce ta ajiye mata a hannunta. Hajiya ta karɓa tana dariyar shimenta ta ce ta je ta cire kayan makaranta ta ci abinci. Idan ta gama ta zo su yi labarin ta ji wane ne mijin kuma ɗan wane gida ne a garin. Amma saboda ba ta san komai a kansa ba Hajiya ta tsoratar da ita sosai, gudun ta faɗa matsala idan ba mutumin kirki ba ne a shiga uku. Amma daga bayanin da ta yi mata ne ta fahimci shi ne wanda Aliyu ya ba ta labarin ya je gidansa. Hakan ya sa ta ce mata idan ya dawo ta ce ya zo tana neman sa.

Washegari kuwa, ana sauke ta ya zo da motarsa ya ɗauke ta. Bayan sun isa ƙofar gidan ta sanar da shi saƙon Hajiya. Babu ko ɗar ya fito ta yi masa jagora har cikin gidan, Hajiya ta fito suka yi magana a keɓe, a nan ta fahimci lalle shi ma da tasa hujja karɓaɓɓiya. Ta yi masa addu'a da godiya sannan ta sanar da shi wasu abubuwan da da ma can ya san su. Saboda komai na Bintoto yana biye da shi sau da ƙafa tun daga ranar da ya yi tozali da ita a ƙauyensu har zuwa birnin da Allah Ya sake haɗa su.

A daddafe Bintoto ta ga Jumu'a ta zo, saboda ta matsu ta ga Kandala ta fesa mata labari. Hajiya ta shirya mata tafiyar sosai don Hari ta kira a waya ta sanar da ita za su je ƙauye. Hamida ta karɓo mata ɗinkunanta da ta bayar aka ɗinka mata, amma ko da ta kawo mata ba ta gidan. Don kullum sai ta kawo Baby wurin Hajiya take zuwa wurin aiki, amma da yake Bintoto tana makaranta ba su taɓa haɗuwa ba. Lokacin da za ta dawo gidan kuma Hamida har ta tsufa da barin gidan ta koma gida, don da ƙarfe biyu zuwa uku na rana take tashi daga aiki. Yayin da ake tayar da su Bintoto da ƙarfe biyar na yamma.

Misalin ƙarfe huɗu da rabi na yammacin ranar Jumu'ar, Hajiya ta sa direbanta ya kai ta har gidan su Hari, domin ta kai Bintoto. Sannan kuma da niyyar ta yi musu bayanin saurayin Bintoton mai suna Jabir, don a san abin yi tun kafin tafiyar ta yi ƙwari.

Murnar ganin ta ya sa Kandala fashewa da kuka tana faman fyace majina da gefen zaninta. Saboda ganin ta cikin sabuwar shigar kamala, ta yi kyau tubarakallah a cikin hijabinta sabo tamkar ba Bintotonta ba. Hari ma kanta ta yi farinciki da ganin sauyin da ta samu, shiriyar da take so ta samu Allah Ya fara kawo mata ita.

Bayanin Jabir da suka ji a bakin Hajiya abin ya ƙara faranta musu rai. Bintoto dai sai faman wasar baki take yi, amma ta kasa cewa komai sai ƙunshe fuska take yi alamun kunya.

Hajiya ta sa aka shigo da kayan tsarabar da ta haɗa wa Bintoto, sannan ta kawo kuɗi ta ba Hari ta ce ga shi nan ladar 'yan kujiba-kujibar da take yi musu a cikin gida, saboda watan da suka ɗauke ta aiki ya cika har ya haura, tun daga barin ta hannun su zuwa gidan Hamida da dawowarta hannunta. Duk da ba wani aikinnkirki ta yi ba, amma hakan bai hana Hajiya yi mata ihsani ba.

Su Kandala suna ta godiya da sa albarka, saboda su kansu sun san abin da Hajiyar ta yi mata; ko rabinsa Bintoto ba ta cancanci a ba ta ba. Amma saboda

karamci irin na gidan girma da waɗanda suka san darajar mutane, ta linka musu ladar aikin cike da kyautatawa.

Ashe Bintoto kawaici ne take yi wa idon Hajiya, a lokacin da tana nan shiru take ba ta ko motsin kirki, amma kamar jira take yi ta tafi ta zare hijabin ta jefar tana faɗin,

"To ni Kandala wai yaushe ne za a yi mini auren."

Kangala da Hari suka zaro ido, cikin ƙufula Kandala ta wurga mata daƙuwa a fusace ta ce,

"Ranar da duk Amadun Jaririya ya saya miki gado mai fameka."

Na yi nan ♀

Princess Dija ✍

31.

Nan take Bintoto ta haɗe rai tana kumbura fuska ta ce, "Wai ke Kandala komai aka yi sai kin kira sunan Babana! Wallahi fa idan ba ke ba ce kowace ce sai na rama. Nan fa Abu na gidan su Jamila daga ya ce Ɗan'agunde shikenan kika yi ta faɗa har da kai shi wurin 'Yansandan bakin titi. Amma ni ki yi ta kiran sunan Babana ai ni ma na san zafins...."

"Ni ma ki kai ni wajen 'yandandan tun da kin san zafin a kira sunan ubanki Amadun Jaririy...."

Babu shiri Bintoto ta fashe da wani kalar kuka tare da dunƙulewa wuri ɗaya tana faɗin, "Wallahi-wallahi idan ba ki daina zagi na ba sai na rama."

"Ramawa na nawa kuma? Ai ina jin yanzun nan kika gama kiran Ɗan'agunde ko kuma kina nufin ni ce ban san zafin nawa uban ba?"

Hari ta yi hanzarin shiga tsakani gudun abin ya yi ƙarfi ta raba faɗan, saboda fahimtar idan ta yi shiru rigimar tasu ba mai ƙarewa ba ce. Suna tsaka da harhaɗa kayansu wani yaro ya shigo yana faɗin, an ce Bintoto ta fito ƙofar gida saurayinta kuma wanda zai aure ta ne ya zo. Kandala ta yi tsam da rai cikin faɗa tana cewa,

"To ba za ta zo ba! Shikenan shi ba zai shigo ya gaishe mu ba sai dai ya laɓe ƙofar gida yana mana aike? To ka ce na ce ba za ta zo ba! Ko ita ce za ta aurar da kanta ba mu za mu yi mata auren b...."

"Inna ki sassauta kada ya ji k..."

"Yo idan ma ya ji ni sai me Hari? Ai shi ma ya san bai kyauta ba! Mu ya dace ya zo ya gani ba ita ba, don mu ne za mu ba shi ita, ba za ta iya aurar da kanta gare shi ita kaɗai b...."

"Wai ya ce wurin ku ya zo ba wurin Bintoto ba."

Wani yaron da ya biyo bayan wanda aka fara aikowa ya faɗa yana ƙumshe dariya. Ganin tana lasar bakinta da ya yi dagaje da goro, don garin faɗanta goron da ta kwance a gefen zaninta tana ƙoƙarin kaiwa baki ya faɗo ƙasa, ta sake ɗauka ta nufin bakin a nan ma ya sake faɗuwa, ta duƙa da niyyar ta ɗauke shi cikin rashin sani ta shura shi da ƙafa ya yi nisa. Sai da ta bi shi ta ɗauko tana faɗin,

"Wallahi sai na ci ka. Ku ji mini la'anannen goro!"

Kafin ta dawo bai wa yaron amsa tana cewa, "Ya dai fi masa. Amma tun da yarinya ba ita ce za ta ba da kanta ba ai mu ya dace ya nema ba kowa b..."

Hari ta yi hanzarin tare zancen da cewa, "To ai ke Inna wataƙila niyyarsa sai ta fita sai ya aiko ta a ba shi izinin shigowa, idan ta faɗa mana ga shi nan ya zo. Don na tabbatar da ko shi ba zai zo ya tafi ba tare da ya neme mu ba."

"Ke dai kin kare surukin naki kawai Hari. Amma ni tun yanzu na fara jin kamar kishinsa nake yi."

Hari ta yi hanzarin yin dariya, saboda fahimtar Kangala ta sauko daga dokin fushin da ta fara hawa, sai da ta shimfiɗa masa tabarma sannan ta ce da yaron ya ce ya shigo. Bintoto kam tana ɗaki tun da ta ji shi ne ya zo ta hau sauya kaya, har da shafa hoda da fesa turare kamar yadda Hajiya ta ce ta dinga yi, idan ya zo hira sannan da ƙauyensu idan sun je, kada wani ya ji jikinta yana wari a ce a can birnin ba a koya mata komai ba.

Hakan ya sa ta baje kayan kwalliyarta ta dinga zuba kwalliya har Jabir ya gama gaisawa da su Hari ba ta gama ba. Sai da Kandala ta ƙwala mata kira sannan ta fito tana ɗaura ɗankwali ta tsaya gabansa ko mayafi babu tana kumbura fuska. Hari ta ja ta zuwa ɗakinsu tana yi mata raɗar,

"Saka hijabinki ya daina ganin ki babu abin rufawa a jikinki."

"To ai ni babu komai a jikina Inna."

Ta faɗa tana dudduba jikin nata, Hari ta yi hanzarin miƙa mata hijabi tana faɗin, "Na sani, ke dai saka hijabin kada ya kalle miki ƙirji a banza."

Sai a lokacin Bintoto ta yi dariya tana rufe fuska, bayan ta kai kallonta ga matasan nonuwanta da suka fara kumburowa a cikin riga. Sai da Hari ta ƙara gyara mata ɗaurin ɗankwalin sannan ta ce, ta ɗauki kujerun roba guda biyu ta ajiye cikin a soron gidan, kada su fita waje wani ya gan su suna hira.

Kandala kam gaba ta saka Jabir da tambayoyi har sai da ta ji wane ne shi, ɗan gidan waye da sana'ar da yake yi. A nan ta gano ashe ma ɗan ƙanwar hakimin garinsu ne Lauri, wadda ke aure a cikin birnin.

A nan ta sanar da shi idan sun je ƙauyen shi ma ya tafi don ya gana da dangin mahaifin Bintoto. A cewarta gara ubanta ya sani da wuri ya tanadar mata gadon aure kafin lokaci ya ƙure. Da ƙyar ya samu ya ɗaga daga kan tabarmar da yake kai, saboda hirar Kandala babu aya babu waƙafi, hatta inda zai ajiye Bintoto sai da ta tambaye shi ɗaki nawa ne kuma ya fasalinsu yake.

Bayan ya dawo soron ya zauna, ya shiga goge gumin fuskarsa da Kandala ta saka shi haɗawa cikin ɗan lokaci. Saboda ko kaɗan ba ya son ta ƙure shi, a sanadin tambaye-tambayenta ta rusa masa tsarin da yake kai, gudun Bintoto ta boƙare masa bayan ya fara samun kanta cikin sauƙi.

Sai dai ita ma a cikin hirar tasu babu komai face tambayoyi da hirar yaushe zai kai ta Makka idan sun yi aure. Ya ce mata ta jira su ga lokacin ya zo komai za a bi shi daki-daki, amma ta kafe lalle ita sai ya faɗa mata bayan sun yi aure da kwana nawa za su wuce ƙasashen wajen da ya ce za su je yawon buɗe ido.

Dole Jabir ya gyara zama ya shiga zuba mata dafɗin baki da cin alwashi iri-iri duk don ya ƙara farauto zuciyarta, sannan ya kwantar mata da hankali ta gano ba ƙaramar sa'a ta yi ba, tun da ta samu irin sa a matsayin wanda zai aure ta.

Misalin ƙarfe tara da rabi na dare Kandala ta leƙo tana cewa ya tafi gida kada dare ya yi masa a hanya. Abin da ya riƙo mata ya ba ta, sannan ya ciro dubu biyar ya ce ta ba su Kandala su sha ruwa a hanya. Ta rako shi har bakin ƙofar gidan cike da mamaki ta dinga wara ido tana faɗin,

"Ina motar da ka zo da ita?"

Sai da ya sosa kai sannan ya ce, "Faci ta yi na miƙa ta wurin mai gyara, saboda ba na son lokaci ya ƙure ban zo ba, shi ya sa na yi tattaki a ƙafa na ƙaraso don kawai na gan ki na ji sanyi."

"Wai Allah! Har na ji sanyi! Ba ka ji yadda na ji tsoro ba, kada a ce mutanen unguwar nan sun sace maka mota, ka san duka talakawa ne babu mai kuɗin kirki a cikin su. Ni wallahi yadda zan kwana a nan ma nake tunani. Na saba da kwanciya gidan masu kuɗi, haka kawai na kwana a nan zazzaɓi ya kama ni a banza."

Jabir yana ƙunshe dariyarsa ya yi mata sallama ganin Kandala ta leƙo tana kallon su. Alamun ta gaji da hirar tana son ya tafi Bintoto ta dawo cikin gida. Tana ɗaga masa hannu har ya yi nisa, sannan ta dawo tana kumbura fuska ganin Kandala a bakin gidan tsaye ta kasa tafiyar. Ta gefenta ta raɓa ta wuce tana faɗin,

"Shikenan sai a zo a saka wa mutane ido suna hira."

"Auren ma idan ba ki yi hankali ba da ni za ki je gidan na ga tsiyar da za ki tsinana, ga ɗakina ga na uwar mijinki. Saboda dole sai an saka miki ido a ga yadda za ki yi zaman auren idan kin iya."

Bintoto ta dinga rantsuwar babu inda Kandala za ta bi ta, idan ba gadi za take so ta yi mata a gidan auren ba, sai a ɗauke ta aiki. Hari dai shiru ta yi musu tana ta shirya kaya ba tare da ta bi ta kansu ba. Bintoto ma gajiya ta yi da surutun ta kwanta tana zuba hamma, kafin ka ce me barci ya yi awon gaba da ita bayan ta gama mitar kukan sauro yana damun ta. Kandala ta zo kwanciyar ita ma tana mitar Bintoto ta matse ta kafin ta koma faɗin,

"Ɗiyar Amadu dai an yi kwana kowa ya huta da jaraba."

Hari tana gyara kwanciyarta ta ce, "Inna 'yar nan tawa watarana sai kin nemi ganin ta da kuɗi ma ba ki samu ganin ta ba."

"Sai ka ce abin kirki kuka haifa, wannan sokuwa har wani son ganin ta zan yi? Ni fa mamakin wannan yaron da ke son ta ma nake yi. Ko me ya gani a jikinta da zai wuce matan duniya ya ce sai ita kaɗai yake so?"

Hari tana zuba hamma ta ce, "Shan koko ɗaukar rai Inna."

Daga haka suka yi shiru kowa ya koma nazari kafin barci ya kwashe su duka. Asubar farin suka farka suka yi sallah, sai da suka karya sannan suka yi shiri. Ƙarfe takwas na safe a cikin tasha ta yi musu, a cewar Kandala su tafi da wuri tun kafin munafukan garinsu su fito shan iska.

"Su Mani ana can gindin bishiya, wataƙila ma babu abin da ya sauya."

Kandala ta faɗa tana juye baki gefe, saboda takaicin ya zama ragon ƙarfi da ya ji. Da ƙarfinsa amma ya lalace gindin bishiyoyi yana gulma da sa ido, bayan ga aikin ƙarfi kala-kala wanda zai nemo kuɗin da zai rufa wa kansa asiri da matarsa.

"Da a ce Kulu ba juya ba ce, da tuni asirin Mani ya tonu."

Kandala ta yi maganar cikin ƙunar rai, saboda takaicin Mani ko tuna shi ta yi sai ta ji haushi. Hari da Bintoto babu wanda ya bi ta kan zancenta, saboga gyangyaɗin da suke yi, daga ita har su barcin suka sha har aka isa garin, ba tare da sun sani ba. Alamun rage gudu da saukar motar ya sa suka farka, ɗan dako ya ɗaukar musu kayansu zuwa gida, don a kan hanya suka rabu da Hari ita ma ta nufi nasu ɓangare.

Tun daga nesa da yara suka hango Bintoto da Kandala suka fara ihun murnar ga su nan, nan take gari ya ɗauka Kandala da Bintotonta sun dawo daga birni. Cikin ɗan lokaci gidansu ya cika da mutane ana ta yi musu barka da zuwa. Bintoto kam tun a kan hanya ta fara rabon minti da biskit, yara suka biyo ta buuu a baya suna ta tsalle.

Kandala kuma ta baje saman tabarma har da buɗe ƙafafuwanta a bakin ɗakinta, sai wasar baki take yi ana ta shigowa yi musu barka da zuwa. Kulu ma duk da ta san watan tashin hankalinta ne ya dawo, amma hakan bai hana ta jin daɗin ganin su ba.

Mamaki fal ran Kandala ganin alamun ciki a tattare da Kulu. Hakan ya sa duk ta motsa sai ta kai kallonta gare ta, don tana so ta tabbatar shin cikin ne ko kuwa jin daɗin an bar mata gidan ita kaɗai ne ya sa ta sauya. Babbar ɗiyar Kandala da 'ya'yanta suka garzayo ana ta murnar dawowarsu.

Mani yana tsaka da hira cikin abokansa ya ji labarin zuwan su Kandala. Baki har kunne ya isa cikin gidan abokansa suna zolayar shi da cewa, ya tashi ga rumbun hatsinsa can ta dawo. Sai dai hango Kandala cikin bisashenta tana ta faɗa ya ji ƙirjinsa ya buga. Don bayan mutane sun rage ta nufi wurin da take kiyon, ganin kamar babu uwar garken akuyarta. Jikinta yana ɓari ta shiga ƙwala wa Kulu kira, ta iso wurin cikin faɗuwar gaba ta rusuna tana faɗin,

"Inna ga ni."

Wani kallo ta yi mata mai ɗauke da tuhuma kafin ta ce, "Ina kuka kai mini uwar garkena?"

Kulu ta shiga sosa jiki da kai tana ƙoƙarin magana amma ta koma in'ina, alamun ba ta son cewa komai. Sai da ta buga mata tsawa haɗe da zagi cikin ɗaga murya sannan ta ce,

"Ai...ai...Inna lokacin da kina can ciwo na y..."

"Ciwo kika yi ni na ɗora miki ciwon?"

Kulu ta shiga girgiza kai kafin ta samu bakin faɗin, "Sh...shi ne da aka kai ni asibiti sai likita ya ce sai an yi mini hoto ga ciki. Da muka dawo babu kuɗin Mani ya ɗauki uwar garken ya sayar aka yi mini magan...."

"Na rantse da Allah! Na rantse da kabarin kakana Buba Shagirbi sai kun biya ni akuyata daga ke har shi Manin! Yanzu don ba ku da imani shi ne za ku rasa akuyar da za ku sayarwa sai uwar garken...? Shin ke gidanku babu akuyoyin ne ko ba kina da kaji ba? A kan me za a ɗaukar mini akuya a sayar ba tare da na sani b...."

"Inna cik...ciki ne gare ta, Inna shi ya sa na biya kuɗi likita ya duba ta aka ceto lafiyarta. Kuma wallahi Inna akuyar ma ta kwana biyu ba ta da lafiya, gudun ta faɗi ta mutu a yi biyu babu na nemo Ɗan Alhaji muka daidait...."

Zancen Mani kenan cikin rawar jiki da tashin hankali, don da ma ya shirya wa zuwan ranar, saboda ya sani muddin ta yi ido biyu da dabbobin ba ta hango uwar garken ba akwai matsala. Kafin ta katse shi cikin fusata tamkar za ta kai masa duka ta ce,

"Dole ku daidaita! Lalle dole ku samu daidaito da Ɗan Alhaji a kan akuyata! Tun da ni ce na yi gohon yi wa Kulu cikin. To billahillazi ka kwana da shirin sai ka biya ni akuyata daga kai har ita, ko kuma kolo ya gan ku a cikin faɗin garin nan. Don ficikata ba za ta yi ciwon kai a kan hidimarka ko ta Kulun ba. Ciki kuma idan dare ya yi ka ƙara yi mata wani yau sai ta haɗa biyu, ɗaya a gabanta ɗaya a bayanta, tun da ka tanadi kuɗin abin yankawa da icen yi mata ruwan zafi."

Haƙuri ya shiga ba ta tare da yayarsa da mutanen da ke shigowa yi mata sannu da zuwa. Amma hakan bai hana ta ci gaba da faɗanta ba, sannan ta sanar da shi duk abin da ta tara Bintoto za ta kashewa. Idan ma ya kwana da tunanin yi wa Kulu ciki don ta yi suna ya yaudari kansa.

Takaicinsu shi da Kulun ya sa ba ta kwana ba sai da ta nemo mai sayen dabbobin duka aka yi cinaki. Babu jinkirin komai ya bayar da rabin kuɗi ya ce idan safiya ta waye zai kawo rabi. Da kuɗinta ƙulle a ƙugu ta kwana, zuciyarta cike da saƙe-saƙen yadda za ta sayar da gonarta a sirrance ba tare da Mani ya sani ba. Saboda ko damuna ta kama sai dai ta bayar da ita sufuri idan ba ita ce za ta yi noman ba, amma shi ba ya iya yin komai sai zaman kashe wando a cikin gari.

Saboda ya saba da lalaci auren ma ita ce ta yi masa, hakan ya sa ya yi tsammanin za ta ci gaba da ɗaukar ɗawainiyarsa kamar yadda ta saba.

Tun da safe ta bayar aka sayo mata kaji masu kyau ta shiga aiki Bintoto da sauran jikokinta suna taya ta. A cewarta kada iyayen Jabir su zo neman auren Bintoto Amadu ya kasa yi musu fitar kunya. Da kanta tare da taimakon maƙota aka dafa shinkafa da miya. Bayan ta yi wa Kulu kashedin kada saka mata hannu tun da tofe-tofen yawu take yi. Bintoto ta dinga yi mata gwalo tana dariya ta ce,

"Yelumm! Wata ta ji haushi an hana ta aiki saboda ƙazanta."

Kulu ba ta kula ta ba, gefe ta ja tana kallon mutane ana ta hada-hada, jefi-jefi tana ta tofar da yawun da ko kaɗan ba ta iya haɗa su ballantana su wuce cikin maƙoshinta. Da ma can aikin ƙarfin hali ne ta so yi, saboda ƙarnin naman kajin da aka yanke gabaɗaya ya hana ta jin daɗin zuciyarta. Sai da ta shige bayi ta yi amai sannan hankalinta ya kwanta.

Bintoto kam sai rawar kai take yi tana ta faɗa wa mutane ta kusa aure kuma mijinta mai kuɗi ne, har da Makka zai kai ta. Jamila da sauran ƙawayenta suka cika gidan suna ta kallon ta cike da burgewa, uwa-uba ƙaryar da take ta sharara musu ba ƙaramin sha'awar zuwa birnin ta cusa musu ba.

Musamman da Inna Hari ta zo gidan ta sa Bintoto ta yi wanka ta saka sabuwar atamfarta cikin kayan da Hamida ta kai aka ɗinka mata. Ta yi kyau sosai ga sabon kitson da ke kanta ya ƙara fito da fuskarta. Inna Harin ta ce ta saka mayafi mahaɗin atamfar sai ta fi kyau, fiye da hijabin da ta dunkuma ta ɓoye gayun. Ga sabuwar sarƙa da ɗan kunne sun yi mata ɗas tamkar ba ita ba.

Abokanta sai jan ta suke yi kowa yana so ya yi magana da ita. A ƙarshe wulaƙancin da ta yi musu ya sa suka ja gefe suna kallon ta. Saboda ture Jamila ta yi da ke kusa da ita tana faɗin,

"Ke dalla matsa can, wallahi duk warin talauci kuke yi. Dube ku don Allah gabaɗaya ma ko wanka ba ku yi ba. Ni yaushe zan iya zama cikin ku ku shafa mini ƙazanta saurayina ya zo da motarsa ya ji ina warin dauɗa. Yawwa bari na faɗa muku tun yanzu, idan ya zo kada wadda ta je wurin sa, don ko kin je ni zan faɗa masa ban ma san ku ba."

Haushin maganganun da ta faɗa musu ya sa suka bar gidan suna gulmar ta. Yayin da suka yi dandali a ƙofar gidan suna zancen yadda ta koma 'yar birni daga zuwanta har ta samu miji mai mota. A nan suka yi shawarar su ma za su roƙi Hari ta tafi da su birnin ta samo musu maza masu kuɗi, kamar yadda ta samo wa Bintoto miji mai mota.

32.

Da misalin ƙarfe uku na rana Jabir da iyayensa suka dira gidan hakimi. A can aka gama tantance yadda za a tafi gidan Amadu Baban Bintoto. Don tun kafin zuwansu Kandala ta tafi da kanta ta sanar da shi abin da yake faruwa. Hakan ya sa ko da iyayen Jabir da wakilan hakimin suka isa: sun tarar da tabarma an shimfiɗa musu. Sannan da yayu da ƙannen Amadu waɗanda suka karɓi zancen auren hannu biyu. A nan aka yanka sadaki dubu ɗari Jabir ya biya lakadan. Sannan da kuɗin gaisuwar iyaye ana ta addu'a da sam-barka. Musamman ganin motar da ya zo da ita matan garin sai leƙe suke yi ana ta faɗin Bintoto ta yi goshi, kuma ta taki arziƙi daga zuwa birni aikatau ta dawo da miji mai kuɗi.

Bayan sun bar gidan su Amadun suka nufi gidan Kandala, a can aka yi musu babbar tarba ta musamman. Don ɗakin Kandala aka jera masu kwanonin abincin da ruwa mai sanyi har da zoɓo. Jabir da abokinsa tare da iyayensa biyu maza suka saki jiki suka narki abincin iya cikinsu. Naman kajin ma babu abin da suka bari sai ƙasusuwa tsabar garɗin naman da daɗin miyar Kandala mai wadatacciyar daddawa.

Lokacin da suka gama aka bar Jabir shi kaɗai sannan aka kira Bintoto su gaisa kafin su wuce. Bintoto ta shigo kanta tsaye idonta a kan kwanonin abincin, zuciyarta cike da ɗokin idan sun fita ta hau kan naman kafin a riga ta.

Hango ƙasusuwa a saman murfin kwanon miyar ne ya sa ta shiga satar kallon kwanonin tana dogon wuya, don gabaɗaya hankalinta yana can ba shi take sauraron abin da yake faɗa ba. Fahimtar inda hankalinta yake, Jabir ya yi 'yar dariya yana cewa,

"Gaskiya miyar nan taku ta yi ɗan banzan daɗi. Wataƙila ma ke ce kika yi girkin shi ya sa na ji daɗinsa sosai."

Bintoto ta shiga hararar kwanon miyar tana turo baki ta ce, "Ai ni ba abin da na iya. Duk abin da ka gani Kandala ce ta yi tare da Inna Maimuna."

Baki a sake Jabir ya dinga kallon ta yana ƙoƙarin goge maiƙon bakinsa da hankacif ya ce, "Gaskiya ki koya kafin mu yi aure. Idan ba so kike yi mu fasa zuwa ƙasashen wajen ba mu zauna garin nan Kandala ta dinga ba mu abinci b...."

Wani kallo ta yi masa kafin ta taɓe baki tana cewa, "Hu'um! Ni kam ba zan zauna a garin nan ba sai dai idan kai kaɗai za ka zauna. Yanzun nan ma fa har na gaji da garin, na matsu mu tafi warin talakawa ya fara damu na."

Dariya ta so suɓuce masa, amma dole ya matse ta a bakinsa ya miƙe yana gyara zaman babbar rigarsa ya ce,

"Mu za mu wuce sai kun zo, don na san ku ma ba za ku jima a nan b..."

"Ai gobe-goben nan za mu wuce. Idan ma ba su tashi tafiya ba ni kam na gaji komawata zan yi."

Tana maganar yana saka takalminsa suka fita tsakar gidan, inda mutane suke zazzaune ana hirar kuɗin auren da suka ji labarin har an biya. A nan ya saka hannu aljihu ya fito da kuɗi 'yan naira ɗari sababbi ya dinga raba wa mutanen da ke wajen suna ta murna. Kandala kuma dubu biyar ya ba ta ita kaɗai, suna fita ya damƙa wa Bintoto bandur ɗin naira 'yan ɗari-ɗari sababbi fil tana ta jin daɗi.

Tana tsaye jikin motar yana ƙoƙarin tayarwa su Jamila suka iso wurin cikin sauri suna faɗin, "Mu ƙawayen Bintoto ne, mu ma ka ba mu kuɗin kafin ka tafi."

Sai da ya kai kallonsa ga Bintoto da ke riƙe da ƙugu tana hura hanci sannan ya ciro kuɗin daga aljihunsa ya miƙa wa Jamila. Sai dai kafin su isa hannunta Bintoto ta wafce kuɗin tana aika mata harara tana cewa,

"Ai wallahi ba za a ba ku ba. Ni zan haɗa duka na riƙe tun da ba wani ya samo mini mijin a cikin ku ba!"

Cike da muguwar kunyar waɗanda ya zo da su Jabir ya dinga dariyar yaƙe yana cewa da su Jamilar, "Ku yi haƙuri wasa take yi za ta ba ku idan mun tafi."

Daga haka ya tayar da motar suka bar ƙofar gidan, tana ɗaga masa hannu har suka sha kwana. Kafin ta koma rungume hannu a ƙirji tana kallon Jamila ta ce,

"Wai ke ba ma Innarku ta raba ki da ni ba? Yanzu don yana kwaɗayi shi ne kika ce da mijina ke ƙawata ce. To ni na daina ƙawancen da ke, karɓi ɗaya Amo ke ma Zulai karɓa, ku kaɗai zan bai wa kuɗin ba da ita ba. Idan Innarta ta isa gobe ta sake cewa ta raba mu ƙawancen mu gani."

Haka ta rabar da kuɗin amma ko ficika ba ta bai wa Jamila ba. Takaici ya sa ta yi nesa da ita kafin ta fara ja mata Allah Ya isa tana aika mata daƙuwa tare da faɗin,

"Allah Ya sa yaya Habu ya dawo ya tarar da ke a garin nan ki ga abin da zai yi miki. Don ya ce duk ranar da ya sake kama ki sai ya cire ladar ƙazafin da kika yi masa. Saboda ke ya bar garin nan, don zalunci irin naki kika yi masa sharri kika sa mutane suna ta yamaɗiɗi da zancen har da masu yi masa gori a garin nan. Mijin naki ma da zai aure ki Allah Ya sa kullum ya yi ta dukan ki sai kin some, baƙar muguwa."

Haka Jamila ta dinga jifar Bintoto da maganganu, a ranta tana ji kamar ta bi ta har gidansu ta dake ta kamar yadda suka saba.

Haƙurin da sauran ƙawayen nata suka dinga ba ta ya sa ta yi banza da Jamila, ta shige gida suka rufa mata baya, saboda jin daɗin kuɗin da ta ba su suka tsaya suna ba ta labarin kashin da Innar Jamila ta sha a hannun Jimmai Jarka, a kan kuɗin dashen da ta cinye wa mutane kuma ta ƙi biya.

Dariya suka dinga yi har da riƙe ciki a cikin soron gidan. Saboda Lami ta dinga kwatanta yadda Innar Jamila ta dinga wutsil-wutsil da ƙafa bayan Jimmai Jarka ta taushe mata ruwan ciki daga ita sai buje. Sannan ta yi mata ɗuren garin tuwo har bisa gashin kanta tamkar an barbaɗa mata hoda a kai. Aka yi dace kan nata a kwance yake, wannan dalilin ya sa gabaɗaya Jimmai Jarka ta hautsine shi garin ɗura mata gari a baki ta zuba mata shi har saman kai.

A can cikin gidan kuma Kandala ta fito da kwanoni tana salati. Salatin da ya jawo hankalin Bintoto ta faɗa cikin gidan, hango kwanonin ta isa wurin tana haɗe rai ta ce,

"Ai sai da na duba na gani gabaɗaya sun cinye komai don baƙin kwaɗayi. Ni wallahi da na san duka kika ba su da na shiga na same su na ce su rage mini. Amma yanzu fa sun cinye komai har da miyar duk sun lashe kwanon kamar ba masu kuɗi ba. Wannan ai idan ba don an san suna da kuɗi ba da sai a ce 'yan yunwa n...."

"Ke sun cinye a yi abin da za a yi! Da ma ai don su aka yi." Kandala ta faɗa tana murguɗa baki kamar wata ƙaramar yarinya.

"Ku ji Kandala, ke fa kika fito da kwanonin kina salati. Kuma shi ne don na yi magana za ki ce sun cinye?"

Bintoto ta yi maganar tana aika mata harara. Tsabar ta ji haushin abin da ta yi mata a gaban mutane. Kandala kam barin wurin ta yi ba tare da ta sake cewa komai ba, saboda ranta a ɓace yake da takaicin ganin baƙin sun lashe komai tas ba su bar mata naman ko ɗan kaɗan ba. Don sai da babbar 'yarta ta ce su rage kowa ya saka wa bakinsa, Kandala ta ce ai 'yan gayu ne ba su damu da cin nama ba. Saboda ganin yadda masu sayen wainar Hajiyar a birni wani lokaci ko sun sa an zuba musu naman ba duka suke cinyewa ba. Wainar ma ragewa suke yi a bai wa almjirai ko ita ta ɗauka idan tana so. Naman ma har tara shi take yi wani lokaci ta ƙulle sai ta dawo gida ta ci. Wannan dalilin ya sa ta yi tsammanin su Jabir ma za su rage idan sun tafi kowa ya saka wa bakinsa. Amma maganar da Bintoto ta yi ta saka ta nuna ba ta ji komai ba, saboda gudun munafurcin mutane su je su kai maganar gidan hakimi.

Da dare Hari ta yi gida, bayan sun gama tsayar da maganar komawarsu, da zummar tun da safe za su tafi saboda su isa cikin lokaci. Hakan ya sa ta lissafa kuɗin dabbobin da ta sayar ta bai wa babbar ɗiyarta wani abu ta ce ta riƙe ta ja jari. Tun da abinci ma wuya yake yi mata ita da yaranta, zuwanta gidan da ganin yadda ta koma ɗan lokacin da ba sa tare, hakan ya sa ta ƙara jin tausayin ta a ranta. Sannan ta ci alwashin ko tana can idan ta samu ɗan saƙo za ta dinga aiko mata abin da Allah Ya huwace.

Mani kam, duk nacin da ya yi mata da magiya a kan ta ba shi wani abu a cikin kuɗin; bai sa ta ba shi ko ficika ba. A cewarta kuɗin akuyar da ya ci shi ne rabonsa. Haushin bai samu yadda yake so ba ya bar mata gidan tun kafin su tafi, Kulu ce ta yi musu rakiya har bakin gida tana faɗin Allah Ya kiyaye. Kandala ta shiga maƙota yi musu sallama Bintoto ta tsaya ƙofar gidan tana ta aika wa Kulu harara, sai rufe hanci take yi tana faɗin,

"An bar miki gidan ki ci kanki ke da ƙazantar yawun da kike ta zubarwa."

"Ke ma ai kin kusa yin auren, za ki ji idan da daɗi." Kulu ta faɗa cike da jin haushin rainin da ta yi mata. A fusace Bintoto ta ce,

"Allah Ya raba ni da yin ciki. Ai duk wanda kika ga ya yi ciki ɗan iska ne. Ke ma da kika yi Allah Ya shirye ki ba don halinki ba."

Murmushi Kulu ta yi kafin ta ce mata, "Da iskancin ne ai da ke ma ba a haife ki ba."

Wani kallon sama da ƙasa Bintoto ta yi mata kafin ta ba ta amsa da cewa, "Lelle ma, ni wa ya faɗa miki cikina aka yi? To idan ba ki sani ba ki sani ni daga sama na faɗo Innata da Babana suka tsince ni a daji. Ke kuma a haka za ki ƙare kawu Mani ya mayar da ke 'yar iska har kin bari ya yi miki cik.."

Hango Kandala ta fito daga gidan da ta shiga ne, ya sa ta ɗauki jakarta da ke ajiye tana faɗin, "Mu za mu tafi, ku ma idan ba ku bar garin nan ba sai talauci ya kashe ku."

Wasu yaran da Kandala ta nemo suka riƙa masu wasu kaya suka nufi bakin titi. Inda a can suka iske Hari tana jiran su. Cikin ɗan lokaci suka samu mota Bintoto tana tsaki ta ce,

"Da na sani da ma ni da na ce wancan yaron ya zo da motarsa ya ɗauke ni."

Hari tana daidaita zamanta a cikin motar ta ce, "Wane yaro ne haka?"

"Mai motar da zai aure ni."

Ta ba ta amsa tana kallon gaban motar tare da motocin da ke gabansu suna ta wucewa. Kafin Hari ta yi magana Kandala ta riga ta da cewa,

"To ai ki kira shi ko yanzu ya zo ya ɗauke ki, tun da haifar sa kika yi ai dole ki kira shi yaro."

Hari ta shiga zancen tana faɗin, "Ai ke Inna soyayya babu abin da ba ta sakawa. Kada ki sha mamaki idan ta kira shi ki ga ya dawo ɗaukar ta. Don dai kawai ba ta ce ya zo ba da ya ɗauke ta, ai haka ne ko 'yata?"

Hari ta ƙare maganar tare da kai kallonta ga Bintoto tana janyo ta jikinta cikin kulawa. Bintoto ta lafe tana turo baki ta ce,

"Ki ƙyale Kandala Inna, bayan ya faɗa mini har ƙasar waje zai kai ni na sayo takalmi idan muka yi aure. Shi ne don na ce masa yaro za ta ce ni na haife shi. To ai ko Innarsa ma ya fi so na a kanta, don ya ce a duniya babu macen da yake so kamar ni. Amma dai ita Kandala na san ba za ta yarda ba, za ta ce ƙarya nake yi masa bai faɗa ba, bayan a gaban abokinsa ma ya ce bai taɓa son kowa kamar yadda yake so na b...."

"To shashasha! Wannan son da yake faɗa daban da wanda yake yi wa uwar da ta haife shi. Don babu ɗan da zai ce ya fi son wata ƙatuwa a kan wadda ta kawo shi duniy..."

"Ai ke ma sau nawa kike faɗar Kawu Mani ya fi son Kulu a kanmu? Kuma wallahi ni na yarda da ya fi son ta, tun da har ciki ya yi mata ya sayar miki da uwar garke aka yi mata magani. Idan ba ya fi son ta a kanki ba yaushe zai sayar miki da akuya a kan ya nema mata magani? To ni dai ko za ki ji haushi na sai na faɗi gaskiya

wancan yaron ya fi so na a kan Innarsa, kamar yadda Kawu Mani ya fi son Kulu a kan mu ni da k...."

"To na ji kin faɗa, saura cikin ke ma ki je yaron ya yi miki tun da Mani ya yi wa Kulu, saboda ya fi son ta a kaina."

Wani mugun kallo ta wurga wa Kandala tsawon mintuna ko ƙiftawa ba ta yi kafin ta yi magana cikin murya kuka ta ce,

"Ai ni kuma ba 'yar iska ba ce! Allah ma ya sani ban taɓa yin iskanci ba."

Daga Hari har mutanen cikin motar da ke sauraron su gabaɗaya suka saka dariya. Kandala ce kawai ta yi ƙarfin halin danne ɓacin ranta ta ɓalli goro tana tauna tana faɗin,

"Tun da cikin kike so ai za a yi miki, gaggawar me kike y...."

"Ni ko na rantse da Allah duk wanda ya yi mini ciki sai na kashe shi!"

Ta yi maganar cikin kuka da ɗaga sauti alamun ranta ya kai ƙololuwar ɓaci da maganganun Kandala. Kafin ta dunƙule jikin Hari ta yi ta gunjin kuka ganin har lokacin mutanen cikin motar ba su daina yin dariyar da suke yi ba.

Princess Dija ✍

33.

Da haka suka isa cikin birnin bayan Hari ta shawo kan Bintoto ta daina kukan. Kandala ma da ke ƙara tunzura ta ta sauko daga dokin fushin da ta haye ta rarrashe ta. Tare da sanar da ita babu wanda ya isa ya yi mata ciki har sai idan Allah ne Ya nufa. Daha haka ta kulle mata baki ta koma share hawayenta tana faɗin,

"Ni da mun je ba zan kwana wurin ku ba gidan Hajiya zan wuce."

Kandala tana yi mata hararar gefen ido ta jefa goro a bakinta tana faɗin, "Ki je wurin Alhaji ma idan kina iyawa, ai mu ma ba son zaman naki muke yi ba."

Mai adaidaitasahu yana kai su gidan Hari ta kira Hajiya tana sanar da ita sun dawo. Marece sakaliya Hajiya ta turo aka tafi da Bintoto, da tsarabar ƙauyen da suka yo mata mai yawa saboda jin daɗin yadda take ɗawainiya da su babu nuna ƙyama irin ta masu kuɗi.

Baki har kunne Hajiya ta dinga yi wa Bintoto maraba saboda jin daɗin ganin ta da abin alherin da ta kawo mata. Sai da ta ci abinci ta ƙoshi sannan ta yi wanka ta yi sallah tana ta zuba hamma. Sallah ma sai da ƙyar mai aikin Hajiya ta tirsasa ta yin ta, tana gamawa ta baje a wurin sai barci, ko da asuba ma da ƙyar aka tayar da ita ta yi shirin makaranta.

Cikin zumuɗi da ɗoki ta isa makarantar da kwandon abin breakfast ɗin ta kamar yadda kowa yake zuwa da abin sa. Tana ƙwambo da zuƙe wuya ta shiga ajinsu, ba ta yi wa kowa magana ba ta isa kujerar da take son zama ta zauna tana hararar mutane. Zamanta babu wuya malami ya shigo ajin ya fara yi musu karatu. Amma ko kaɗan hankalinta ba ya kai, hannunta yana ƙasan benci a cikin kularta tana tsamo Irish tana ci da ɗaya-ɗaya, da niyyar idan ta cinye ta koma kan kulolin mutane da take hange tana son ta gano mene ne a ciki.

Hakan ya sa tana cin Irish ɗin tana kallon ƙasan ƙafafuwan masu kulolin, a gefe ɗaya kuma ta koma kallon taga da mutanen da ke wucewa jefi-jefi.

Rubutun da malamin yake yi ya hana shi gano wainar da take toyawa, yana gamawa ya juyowa ya hango kanta a duƙe tana faman tura dankali a bakinta, wanda ta kwaso cike a hannunta don ta matsu ta cinye shi ta ajiye kular.

Babu zato ta ji an daki bencin kujerar da take kai, tana ɗaga kai a firgice ta ga mutum a kanta yana huci. Ita ma ranta a ɓace ta saki kular ɗan sauran dankalin ya zube, tana aika masa harara tare da turo baki ta ce,

"Ni wallahi ka ma ba ni tsoro! Kuma duk abin da ya same ni kai n...."

Cakumar da ya yi wa hijabinta ya jawo ta, ya sa ta yi shirun dole ta koma kokawar ƙwace riƙon da ya yi wa hijabinta. Amma hakan bai hana shi kai ta gaban ajin ba ya wurgar, cikin fusata ya ce ta duƙa, Bintoto ta yi tsaye tana hararar sa tare da rungume hannunta a ƙirji ta ƙi yin abin da ya ce.

Jikinsa yana rawa ya ɗauko bulalar dorinarsa ya shiga zabga mata tana ta tsalle, bayan ta yi durƙushen cikin azama tana roƙon ya yi haƙuri. Amma saboda ta gama ɓata masa rai sai da ya gama sauke fushinsa a kanta, sannan ya jefar da bulalar yana faɗin ta same shi ofis.

Bintoto ta dinga kuka tana tsine masa tare da rantsuwar Wallahi-wallahi ba ta yafe masa ba, kuma ba za ta je ofishin ba. Wasu daga cikin 'yan ajin suka iske malamin har ofishinsa suka sanar da shi abin da ta faɗa. Ransa a ɓace ya nemo wasu manyan prefects ya ce su je su ɗauko masa ita a ka idan ta ƙi zuwa da ƙafarta.

Masu biɗa a duhu ballantana a haska musu, mugayen prefects ɗin suka yi mata kama-kama bayan sun gama zabga mata buloli, suka fito da ita ajin tana ta tirjiya suna jan ta, yayin da masu tura ta ta baya ma suka dinga aikinsu.

A haka suka kai ta har bakin ofishin malamai da ƙarfin tsiya suna nishi. Malamin ya fito yana ba su umarnin su saka ta kamun kunne, azabar da suke ba ta ce ta saka ta yin kamun kunnen dole tana kuka tana faɗin ba ta yafe ba.

A nan suka bar ta cikin rana tana kamun kunne tana kuka, shi ma ya shige ofishinsa yana barci. Tsabar ta ba shi haushi ya kasa yin komai ya koma nazarin wace irin yarinya ce aka kawo musu a matsayin ɗaliba. Saboda ba wannan ne karon farko da suka fara ganin rashin ɗa'a daga gare ta ba. Akwai ranar da 'yan ajin nasu suka kai wa malamai ƙarar tana cinye musu abinci. A nan suka zaunar da ita suna yi

mata bayanin yadda tsarin Makarantar yake da wasu abubuwan da ba ta san kansu ba.

Amma hakan bai hana ta sake gwada musu halayenta ba. A wannan karon ma tana fahimtar babu kowa a wurin da take kama kunnen, prefects ɗin sun tafi ajijuwansu ana yi musu karatu, shi ma malamin ta hango kansa a duƙe alamun barci yake yi. Ta miƙe ta nufi inda ta hango ramin cinnaka da ke ta fitowa daga cikin ramin yana shawaginsa. Leda ta samo ta dinga tsintar cinnakun tana zubawa. Sai da ta tara mai yawa sannan ta nufi bayan ofishin malaman saiti da inda malamin yake zaune ya juya bayansa. Da dabara ta juye masa cinnakun ta saman wuyan rigarsa.

Cikin sauri ya motsa saboda ya ji alamun an taɓa shi ta bayan. Motsinsa ya sa wani cinnka ya gatsa masa cizo. Babu shiri ya zabura yana laluben inda ya ji cizon, kamar almara cinnakun suka dinga cizon shi ya ta ko'ina ya hau soshe-soshe. Bintoto da ke laɓe bayan tagar tana ɗaga kai tana hangen sa ta fito daga maɓuyar tana ƙyalƙyala dariya, ganin yadda yake ta tsalle yana faɗin,

"Subhanallah! Ohh my God!"

Cikin sauri ya cire rigar ya wurgar, sannan ya koma cire dogon wandonsa cikin ɗimaucewa ya wurgar yana faɗin,

"This is serious."

Kafin ka ce me, wasu malamai maza da ke cikin ofishin suka rufu a kansa da tambayar me yake faruwa, saboda mamakin ganin yadda ya birkice a lokaci ɗaya kamar wani sabon kamun hauka. Nan take aka saka shi cikin wani ƙaramin ɗakin ajiyar takardu, saboda gudun hankalin wasu malamai mata ko ɗalibai ya kai a kan abin da yake faruwa. Saboda ofishin malamai mata daban na mazan daban.

Muguwar dariyar da suka ji Bintoto tana yi a bakin ofishin abin ya yi matuƙar ba su mamaki kuma ya ɓata musu rai. Musamman da aka gano cinnaku ne suke cizon

malamin, ganin nan take sun sakar masa ƙolallai kuma wurin ya yi ja kasancewarsa farin mutum.

Wani malami ya kamo Bintoto ya shigo da ita cikin ofishin, sai da ya durƙusar da ita tsakiyar malaman da barazana, sannan ya zare ido yana tambayar me ya kawo ta wurin.

A bayanin da ta yi masu suka gano ita ce ta haddasa wa malamin komai. Malamin ya fito daga ƙaramin ofishin yana muzurai saboda har lokacin bai daina jin zafin cizon cinnakun ba.

Ransa a ɓace ya yi musu bayanin duk abin da ya faru tsakaninsa da ita tun daga cikin ajinsu har zuwa nan ofishin. Bintoto ta hau zarar ido tana ranste-rantsen duk abin da malamin ya faɗa babu gaskiya ƙarya yake yi mata.

A nan suka shiga tattauna matsalarta ta rashin tarbiyya, a nan suka kai ƙarshen bai dace ta ci gaba da zama a cikin makarantar ba gudun ta ɓata musu sauran ɗalibai. Nan take aka kai zancen gaban shugaban makarantar. Bayan doguwar muhawara aka rubuta mata takardar dakatarwa, aka ce idan ta je gida ta bai wa Aliyu.

Sannan ba su bar ta iya haka ba, sai da suka saka ta horo kala-kala, ta sha kuka tare da roƙon a yafe mata amma babu wanda ya saurare ta. Kuma hakan bai hana ta yin aikin da aka saka ta ba, saboda taron da malaman suka yi mata tamkar za su cinye ta da rai. Ko da aka tashi makarantar ta yi tuɓus, tafiya ma da ƙyar ta dinga jan ƙafafuwanta tsabar wahalar da ta sha. Tana kallo Bus ɗin makarantar tasu ta tafi ba tare da ta bi ta kanta ba. Da ƙafa ta yi tattakin fita wajen makarantar tana ta tafiya amma ba ta san inda za ta je ba.

Tsabar kuka sai da idanuwanta suka kumbure, idan ta gaji da tafiya ta tsaya ta huta. Masu bi ta kai idan sun tambayi me take yi wa kuka ta yi banza da sh. Haka ta dinga yi tana ta kalle-kalle a titin tana tafiya, sai ta gaji ta zauna jim kaɗan ta miƙe ta ci gaba da tafiya. Haka ta dinga bin gefe-gefen titi har duhun magriba ya kawo jiki.

A can gidan su Hajiya kuma ganin ƙarfe shida da rabi ta buga har lokacin ba ta dawo ba; ta tayar da direbanta ta ce ya tafi makarantar ya dubo ta. Ko da ya tafi maigadi ya tabbatar masa da cewa lalle babu kowa a cikin makaranta tun da yamma kowa ya watse.

Aka kira shugaban makarantar ya sanar da direban Hajiya duk abin da ya faru, har da takardar sallamar da aka ba ta ta kai wa Aliyu duk ya sanar da shi.

Hankalin Hajiya ya tashi matuƙa a lokacin da direban ya kira ta a waya ya yi mata bayani, ta ce da shi kada ya dawo gida sai da Bintoto, ya shiga neman ta a titunan garin ko Allah zai sa a gan ta. Sannan ta kira Aliyu a waya ta sanar da shi komai da ya faru, yana ƙoƙarin zille wa zancen shi ma ta matsa masa dole sai ya fita neman ta, a lokacin ana ta kiraye-kirayen sallar magriba kowa yana ta haramar arwala.

Wasa-wssa har ƙarfe tara na dare ba a gano inda Bintoto ta shiga ba, hankalin Hajiya a tashe ta kira Hari tana tambayar ba ta je gidan ba? Hari ta koma gefe cikin sassauta murya gabanta yana bugawa, ta sanar da ita ko mai kama da ita ba su gani a cikin gidan ba

Gudun Kandala ta jiyo abin da ke faruwa ta tara mata jama'a ta shiga uku. Don abu ne wanda ta tabbatar muddin ta ji labarin Bintoto ta ɓata sai ta tayar da hankulan mutanen unguwar gabaɗaya sun san halin da ake ciki, tsabar masifa da ruɗun da za ta shiga a kan ɓacewar Bintoto.

Ku fito mu bazama neman matar Jabir.ọ

Princess Dija.

34.

Bintoto kam tsabar tafiyar da ta sha da jigata; tafiya ma ta kai da ƙyar take iya ɗaga ƙafarta. Babu shiri ta ja ta tsaya wurin wata mai soya doya da ƙosai. Ta yi tsaye a gaban kaskon suyar ƙosan tana ta kallon matar tare da ƙura wa ƙosan ido.

Tun matar ba ta ankara da ita ba har ta fara yi mata faɗa tana kora ta, a kan ta bar wurin ganin ta sanye da kayan makaranta. Bintoto sarauniyar kwaɗayi sai da ta yi gaba sannan ta dawo da gudu wurin matar ganin wani ya tsaya zai saya yana miƙa kuɗi.

"Don Allah don girman Ubangiji ka saya mini ko kaɗan ne yunwa nake ji."

Ta yi wa mutumin magana a marairaice tana shafa cikinta. Matar tana aika mata harara ta ce da mutumin, "Wannan bakar yarinya idan ba ta ci kosan nan ba za ta iya mutuwa, tun ɗazu take tsayuwa tamkar ta faɗo mini a ka."

Mutumin ya ce a ba ta ƙosai da doya na ɗari biyu. Haka matar ta wurga mata ƙwarori a leda ta jefa mata. Ta duƙa cikin sauri ta ɗauka tana aika wa matar harara ta ce,

"Ai tun da na rantse sai na ci shi ko ba kya so."

"Mayyar banza! Ki je ki yi ta ci."

Matar ta faɗa tana ci gaba da sallamar mutane Bintoto ta yi gaba tana zagin ta ƙasa-ƙasa tana cin ƙosan. Sai da ta yi nisa da ita ta ɗaga murya tana cewa,

"Mai ƙosai!"

Tana waigowa ta yi mata daƙuwa ta zura da gudu dafe da jakar makarantarta da ke goye a bayanta, sannan kwandon abincinta a hannu. Kai kawai mai ƙosan ta girgiza cike da takaicin wasu iyayen da suke ɓata yaransu, ta yadda yaran ba sa shayin nuna rashin tarbiyyar a ko'ina saboda ba a nuna musu sun yi kuskure a lokacin da ya dace. Sai bayan sun girma a dawo ganin laifin yaran bayan dama ce aka ba su tun suna ƙananu.

Bintoto kam ta ci tafiya sosai kafin ta samu bakin wani masallaci ta kwanta, tana sauke numfashin wahala tana kuka, bayan ta kwankwaɗi ruwan randar masallacin kofi biyu tana nishi. A daidai lokacin ladanin masallacin ya ƙaraso wurin yana ta sauri zai je ya yi kiran sallah.

Hango ta a wurin jikinta da kayan makaranta, ya yi hanzarin isa inda take yana faɗin,

"Ke! Me kike yi a nan wurin?"

Bintoto ta yi banza da shi kamar ba ta ji ba har ya isa kanta yana muzurai ya sake cewa,

"Lafiyarki kuwa? Ko ba kya jin me nake faɗa?"

A nan ma ta yi masa banza, don ko kallon sa ba ta yi ba har lokacin, sai sharar hawaye take yi tana ajiyar zuciya. Fahimtar ba ta da niyyar magana ga lokacin sallah yana ta gudu har wasu sun fara zuwa. Ya yi hanzarin barin wurin ya shiga Masallacin ya yi kiran sallar. Ko da ya fito ya ga mutane har sun fara zagaye Bintoto suna yi mata makamancin tambayoyin da ya yi mata, amma su ma babu wanda ta ce da komai. Hakan ya sa ya yi zargin ko kurma ce wataƙila ba ta ji kuma ba ta magana.

Nan take ya hau yi mata maganar kurame, bayan wasu sun riƙa ta an tayar da ita zaune tana ƙara langaɓewa.

Ɗaga kanta ta yi tana ƙare wa mutanen da suka zagaye ta kallo ɗaya bayan ɗaya. Kafin ta fashe da wani kalar kuka mara sauti tana faɗin,

"Wayyo Kandala ki zo za a kashe ni!"

Maganar da ta yi suka gano ba kurma ba ce, a nan aka rufu kanta da tambayar ina ne gidansu, waye mahaifinta a garin kuma a wace unguwa take.

Sai dai kasancewar ba ta san sunan unguwannin garin ba, ballantana ta faɗi sunan wata unguwa ko ta su Hajiya; zarar ido kawai ta dinga yi kafin ta koma yi musu misalin yanayin gidan su Hajiya da bayyana abubuwan da ke cikin unguwar tasu. Amma ko kaɗan hakan bai sa sun gano unguwar da take ƙoƙarin kwatantawa ba. Don tun da yamma mutane suka dinga tambayar inda ta fito da unguwar da take. Kasancewar ba ta riƙe komai a kanta ya sa ta kasa furta sunan unguwar su Hajiya kamar yadda ta ji Hari tana faɗa.

Ganin an tayar da sallah kuma masu son taimakon ta za ta ɓata musu lokaci; suka bar ta a nan suka shige masallaci. Sai da aka gama liman ya yi sanarwar an tsinci wata yarinya a bakin masallacin, da kalar uniform ɗin da ke jikinta.

A nan take wani bawan Allah ya ce ya san makarantar yana da lambar shugaban makarantar, ɗaga waya ya kira shugaban makarantar. Inda ya yi masa bayanin an ga ɗalibar makarantarsu, kuma alamu ya nuna ɓata ta yi ba ta san inda za ta je ba. Cikin tashin hankali da murnar samun labarinta; ya ce a riƙe masa ita yanzu zai ƙaraso. Saboda tun da ya ji labarin ba ta koma gida ba yake cikin fargaba, gudun wani abu ya same ta a ce su ne sila.

Jikinsa yana rawa ya kira Aliyu ya sanar da shi an gan ta, tare da yi masa kwatancen masallacin da aka faɗa masa don su haɗa ƙarfi su je tare. Aliyu ya nufi inda aka faɗa masa kai-tsaye yana tsaki, tsabar gajiya da gundura da yawon neman ta, wanda Hajiya ta saka shi yi ba don yana so ba. Motarsa kawai ya juya cikin mugun gudu ya isa wurin, da jagorancin wayar da yake yi da shugaban makarantar da ke yi masa kwatance har ya isa. A gefen masallacin ya yi parking, ya fito ransa a ɓace ya isa inda ya ga mutane sun yi cincirindo.

.

Da sassarfa ya isa inda take zauna ta haɗa kai da gwiwa tana kuka. Hango shugaban makarantar a cikin tawagar mutanen ya sa ya yi wurin sa yana miƙa masa hannu suka gaisa. Kafin ya koma kallon Bintoto ya fara faɗin,

"Shashasha! Wato a nan kika ɓoye, gabaɗaya kin ɗaga wa mutane hankali, kin sa an hana ni zama lafiya. Tun kafin magrib nake ta bulayin neman ki, amma don rashin mutunci kin zo nan kin zauna, tamkar wadda ba ta san kowa a garin b...."

"Yanzu dai a yi haƙuri, tun da an gan ta sai a bi ta a hankali har a samo kanta a ji dalilin da ya hana ta komowa gida."

Zancen wani dattijo kenan saboda ganin yadda Aliyun yake yi tamkar ya rufe ta da duka. A fusace ya ce,

"Babu wani dalili illa na rashin mutuncin da ta saba yi."

Shugaban makarantar ya karɓe zancen da bayanin abin da ta aikata wa malaminsu wanda ya sa aka hora ta, sannan suka ba ta takardar sallama, inda ya ƙara da cewa,

"Mu ma fa wannan yarinyar ta so ta goga mana laifin da zai ɓata mana sunan makaranta. Sa'a ɗaya ta ci da take sanye da kayan makarantar da babu yadda za a yi a gane daga inda ta fito. Saboda tambayar duniya an yi mata amma ba ta ce da kowa komai ba, sai sunan Kandala da take ta kira, sannan ta ƙi bayanin da za a gano inda take da unguwarsu ballantana a kai ta gida sai da aka kira ni a waya na z...."

"Ai wannan yarinyar da kuka gani ba ƙaramar hatsabibiya ba ce! Duk abin da take aikatawa da gangan take y...za ki tashi mu tafi ko sai na tattake ki a nan wurin?"

Aliyu ya faɗa yana ƙoƙarin kai mata duka ana rirriƙe shi. Bintoto ta miƙe tana ciccika alamun ta gama yin zuciya, ta nufi motarsa jiri yana ɗibar ta. Tsabar yunwa ta gama cinye cikinta, don rabonta da abinci tun ƙosai da doyar da ta ci. Su ɗin ma ta dai ci ne kawai, amma tayar da kwaɗayi kawai ta yi, saboda ta saba mugun ci, irin wanda sai ta ji za ta yi amai sannan take haƙura.

A cikin motar ma haɗa kai da gwiwa ta yi tana ta shesshekar kuka da ajiyar zuciya. Har ya gama godiya ga mutanen da suka jajanta abin, sannan ya shigo motar yana faɗa ya fisgi motar tamkar zai tashi sama ya kama titi.

Sai da ya gaji da kukanta sannan ya buga mata tsawa ta yi masa shiru ko ya tsayar da motar ya yi mata dukan kawo wuƙa. Dole ta ja bakinta ta yi shiru ganin da gaske zai iya aikata mata abin da ya faɗa, duba da yadda yake a fusace.

Yawan kiran da Hajiya take yi masa yana ƙin ɗagawa, a ƙarshe ya ɗaga cikin muryar mai ɗauke da fushi ya ce mata ga shi nan zuwa gidan ya an gan ta.

Hajiya ta kai zaune babu shiri dafe da kanta tana faɗin, "Alhamdulillah Allah na gode wa Allah."

Hari da ke zaune gaban Hajiyar tana sharar ƙwalla ta yi hanzarin ɗaga kai saboda jin labarin an gan ta. Fuskarta a sake cike da murna ita ma ta ɗaga hannu tana godiya ga Allah.

Don tsabar firgici ba ta san lokacin da ta kawo gidan su Hajiya ba. Ko Kandala ba ta san fitarta cikin gidan ba. Saboda tsoron abin ya yi ƙamarin da dole babu yadda za a yi sai an sanar da ita abin da yake faruwa. Kuma ba ta san da wane kalar yare za ta bayyana mata laifin na Bintoto ne ba na kowa ba. Don Hajiya ta yi mata duk bayanin da ta samu a kan abin da ya faru makaranta.

Ko da Aliyu ya iso gabaɗaya mutanen gidan suna ƙofar gidan ana jiran su.

Saboda Hajiya ta ɗaga wa kowa hankali a gidan, har masallatai aka dinga zuwa ana kai sanarwa, bayan wurin hakiman unguwanni da zummar ko an kai ta can, ko kuma idan an samu wani labarin da ya danganci ɓatan wasu a sanar da ita.

Aliyu ya yi parking motar ya fice a fusace yana cewa, "Wallahi Hajiya idan ba ki rabu da yarinyar nan ba sai ta jawo miki fitinar da ta fi wannan! Ki kore ta kawai ta bar gidan nan kawai kowa ya hut..."

"Yi mini shiru Aliyu! Da ɓatan ta za mu ji ko da surutanka? Ba ka ce an gan ta ba, ina take?"

Aliyu da ya juya yana kallon motarsa ya ce, "Tana jin ki ai ba ta ga damar fitowa ba n...."

Yana maganar ya yi cikin gidan cike da jin haushin Bintoton. Hajiya da Hari tare da sauran masu aikin gidan suka isa inda motar tasa suna kiran sunanta. Ganin ta a dunƙule wuri ɗaya ko motsi ba ta yi Hari ta jawo ta cikin wani sabon fargaba tana kiran sunanta cikin ɗaga murya.

"Bintoto! Bintoto me ya same ki?"

Luu ta yi ta faɗa jikin Hari idanuwanta a rufe tana mashalo. Salati Hajiya ta saka tana kuka ta dinga taɓa Bintoto tana kiran,

"Mai sunan uwata me ya faru da ke? Ki yi mana bayani."

Bintoto ta zame jikinta ta faɗi ƙasa tare da fashewa da wani sabon kuka tana kiran sunan Kandala da ƙara dunƙulewa ciki ƙasa. Hari da 'yan aikin Hajiya suka rirriƙe ta zuwa cikin gidan tana ta tirjiya alamun ba ta son shiga gidan suna shigar da ita ta ƙarfi.

Falo aka ajiye ta, Hajiya ta ce a kawo mata ruwa da abinci. Nan take aka cika mata gabanta da abinci har da su lemu kala-kala. Hakan ya sa duk yadda ta so nuna fushi da abincin dole ta haƙurƙure ta ja abincin tana ci tana kuka. Hari gefe ta ja tana kallon ta cike da takaici har ta gama cin abincin ta koma lasar hannu.

"Yanzu saboda Allah Bintoto ba za ki daina abubuwan da kike yi ba? Kiri-ƙiri kin ɗaga wa mutane hankali cikin dare kin hana kowa zama lafiya."

"Ai mutanen makarantar ne suka tsane ni. Kuma da zan shiga motar da ke kawo mu gida mai motar ya ce kada na shigar masa mota, idan na shiga sai ya ci ubana. Sannan kuma malamai suka yi ta duka na suna zagin Babana. Har da Kamdala ma wani malami mai ƙaton ciki sai da ya zaga. Kuma suka ce kada na sake zuwar musu makaranta tun da ni ba 'yar birni ba c...."

"Maƙaryaciyar banza! Shi malamin da kika yi wa rashin kunya har kika saka masa cinnaku a jiki har kin manta ba za ki faɗa waton? Wallahi ko ki daina halinki ko muguntarki ta zamo ajalinki baƙar munafuk...."

Zancen Aliyu kenan a lokacin da ya fito daga ɗakin Hajiya ya nufo falon, yana kai ƙarshen maganar ya kai mata shuri da ƙafa, kafin ya sauke mata dukan da ya yi niyyar kai wa ƙeyar kanta Hajiya ta dakatar da shi a fusace.

"Wai kai ba ka san a bi komai a hankali ba sai ka yi wa mutane hauka? A tunaninka hakan zai sa ta gyaru har ra daina abin da take yi?"

"Wallahi wannan yarinyar duka kawai ya dace da ita ba wata lallaɓawar da za a yi mata. Amma ni na tafi na bar ku da ita ku yi duk abin da kuka ga ya dace."

Ya fice yana maganar, jim kaɗan sai tashin motarsa aka jiyo alamun ya wuce ya bar su da ita. Shiru falon ya yi babu mai motsi sai Bintoto da ke rusar kuka. Sai da Hajiya ta ja numfashi sannan ta kira sunan da take kiran ta ta ce,

"Daina kukan, yanzu dai duk wata matsala ta zo ƙarshe. Tun da an gano ki kuma makarantar ma sun kore ki shikenan. Sai ki ci gaba da zaman gida tun da shi kike so ba abin da zai tallafi rayuwarki b...."

"A yi haƙuri Hajiya."

Hari ta tari zancenta ganin da gaske Bintoto ta gama ɓata mata rai. Hajiya ta yi wani murmushin takaici kafin ta ce, "Haƙuri ya ƙare Hari, ki tafi da ita gida, gudun wata matsala ta ƙara biyowa mu shiga tashin hankalin da ya fi wannan. Allah Ya gani na so rayuwarta ta inganta, amma hakan ba zai samu ba duk yadda na so kai zuciya nesa. Don yanzu da a ce ba a gan ta ba wane irin tashin hankali kike tsammanin za mu shiga? Kin san duk halin kakarta, komai za mu faɗa ba zai sa ta fahimce mu ba ballantana ta gano laifin na jikarta ne ba namu ba. Saboda haka ki je da ita gida, na fahimci Aliyu da abin da yake son na gane."

Jiki babu kuzari Hari ta shiga bai wa Hajiya haƙuri, sannan da godiya a kan ƙoƙarin da suka wajen ceto rayuwar Bintoto daga duhun ƙauyanci da rashin ɗa'a. Hajiya ta ce babu komai Allah Ya shirye ta, aka harhaɗa mata komatsanta suka bar gidan, misalin ƙarfe tara da rabi na dare.

Bintoto tana matsar ƙwalla suka isa unguwar su Hari. Ko da suka je suka tarar da Kandala tana zaune ta yi tagumi. Ganin Hari da Bintoto a lokacin gabanta ya ƙire ya faɗi, ta miƙe zumbur ta taryi gabansu ido tsakar ka ta ce,

"Wa nake gani kamar Bintoto?"

Princess Dija.

35.

Kukan da ta fashe da shi, tare da rugawa da gudu ta isa inda take zaune ta faɗa jikinta ta ruƙunƙume; hakan ya tabbatar mata da lalle ita ce ba gizon da ta saba yi mata ne a ido ba. Cike da tsantsar mamaki ta bi Hari da kallo a cikin hasken ƙwan lantarkin da ya haska ɗakin, ganin jakar kayan Bintoto a hannunta tana ƙoƙarin kai ta ƙuryar ɗakin ta ajiye. Kandala ta bi ta da tambayar ina ta haɗu da Bintoton kuma har da jakar kayanta. Amma takaici bai bari Hari ta yi magana ba, zama kawai ta yi tare da yin tagumi tana sauke ajiyar zuciya.

"Wai Hari lafiyarki kuwa, ina ta yi miki magana kin yi banza da ni?"

"Ki yi haƙuri Inna, ban san ta yadda zan yi miki bayani ba ne, sannan ban san ta ina zan fara b..."

"Ki fara ta tsakiyar kaina Hari! Don alamunki ya nuna akwai wani mummunan abu da ya faru ga Bintoto, wanda har kike ƙoƙarin ɓoye min...to billahillazi duk abin da ya same ta ba zan yi wa kowa kawaici ba, kuma ban san kara ba ballantana na gwada ta a kan duk wanda ya cutar mini da Bintot..."

"Inna!"

Hari ta kira sunanta cikin wani yanayi na rashin daɗi da fargaba, ganin yadda ta fara yi mata saukalen maganganu tun kafin ta ji abin da ke faruwa. Tana shafa kan

Bintoton ta shiga dudduba jikinta domin tabbatar da babu wani abin da ya same ta. Jin sunanta da Harin ta kira, hakan ya sa ta ɗaga kanta tana kallon ta cikin wani irin yanayi, kafin ta sassauta murya ta ce,

"Ba wata Inna sai gaskiya Hari. Ki sanar da ni kawai na ji me ya samu Bintoto kuma daga ina kika gan ta? Saboda tun da kika saka ƙafa kika fita ba ki sanar da ni inda za ki je ba nake cikin fargaba da tunanin a wane hali Bintoton take. Sannan zuwanki da ita a cikin daren nan ya nuna akwai wani mummunan abu da ya faru a can gidan aikin nata, shi ya sa ba kya son buɗe baki ki sanar da ni saboda an gama cin zalinta."

Shiru Hari ta yi na ɗan lokaci kafin ta sake sauke wata ajiyar zuciya ta magantu cikin yanayin damuwa da ɓacin ran da ya bayyana a kan fuskarta.

"Inna, kin fi ni sanin halin Bintoto da rashin jin da take aikatawa kala-kala tun a can ƙauye har zuwa nan. To a yanzun ma wani sabon abu ne ta sake yi, da ma can ko rikicin da aka yi har yaron Hajiya ya kore ta daga gidansa; ni ce na roƙi alfarmar a yi haƙuri Hajiya ta zauna da ita a gidanta, amma a bisa sharaɗin duk ta aikata wani abin da bai dace ba za su sallame ta. To a wannan lokacin ma ta sake gwada halinta, saboda ba ta dawo gida kamar yadda ta saba yi ba, asali ma har cikin daren nan babu inda ba a je neman ta ba, sai da ƙyar aka gano ta a bakin wani masallac...."

"Dakata Hari! Kai-tsaye ki fito ki sanar da ni ɓata ta yi. Kuma hakan ya faru ne a sanadin sakacin da suke yi wa riƙon nata. Don haka ni da ma can ba son zaman nata wani wuri nake yi ba. Dawo mini da ita da kika yi a nan ya fi mini farinciki da watarana a sanar da ni mutuwarta a hannun sakarkarun mutane marasa tsoron Allah. To ta Allah ba tasu ba, yadda duk suke son su ga ta wulaƙanta a duniya Allah ba zai bari a tozarta marainiyar Allah ba."

Sai da ta ja numfashi ta ɗan tsahirta da maganar kafin ta ɗora da cewa,

Gidansu kuma ko ba su kore ta ba ni da kaina zan je na taho da ita, don ba aljanna ake rabo a cikin gidan ba ballantana a ce rabon lahirarmu yana hannunsu. Hakan da suka aikata ya yi daidai, amma ki sani duk abin da ya samu Bintoto na assha wallahi ba zan ja bakina na yi shiru ba don kawai suna da kuɗi. Dole ne na yi fito na fito da su saboda babu uban da nake tsoro a cikin s...."

"Inna! Don Allah ki san me kike faɗa, idan hankali ya gushe hankali yake nemo shi. Bintoto da kika gani duk abin da ya faru ita ce ta jawo komai. Lokacin da ba a gan ta ba Hajiya har kuka sai da ta yi saboda tashin hankal...."

"Ai dole ta shiga tashin hankali Hari, don ɗan mutum ba tamkar kiyashe ba ne. A ce tun safe har dare ba a ga yarinya ba kuma a ja baki a yi shiru ni ba za a iya faɗa mini na sani ba? Sannan idan sun damu da ita ai ba za ta ɓace ba, don tun da take hannuna ba ta taɓa wuni guda ba a san inda ta shiga b...."

"Daga makaranta fa ta wuce yawonta ba ta dawo gidan ba kamar yadda ya saba, saboda kawai ta yi wa malami laifi an hora ta, shi ne ta zaɓi ɗaga wa kowa hankali ta hanyar ƙin bin motar da ke kai dawo da ita gida. Bayan ita ta saka wa malami cinnaku a cikin riga suka yi ta cizon sa, a sanadin haka shugaban makarantar ya ba ta takardar sallama daga makarant...."

"Sallama? To ai tun da ba takardar barin duniya aka miƙa mata ba da sauƙi." Kandala ta faɗa tana juya kai tare da kwance ƙullin goron da ke haɓar zanenta ta gutsura. Tana ƙoƙarin mayar da goron ta ƙulle Bintoto ta fara sharar ƙwalla tana cewa,

"Wallahi Kandala haɗuwa suka yi daga malaman har 'yan makarantar suna ta duka na da buloli. Sannan suka saka ni shara da wankin bayi har da kamun kunne sai da na y.... yiiiii!"

Ta ƙare maganar cikin muryar kuka, kafin ta fasa wani sabon kuka mai sautin da ya ƙara tunzura Kandala. Cikin fusata ta ce,

"To to! Yanzu na ji yadda kan zancen yake, wato a makarantar ma sun dake ki? To ai da ma can su gidan aikin naki su suka ji za su iya saka ki makarantar, don babu wanda ya roƙe su. Kuma saboda kawai kin saka wa malami cinnaku za a taru a dake ki? Sai ka ce wadda ta ɗauko kunamu ko macizai ta saka masa a rigar, ai wannan zalunci ne da cin amana, don hakan da suka yi miki ba zai hana cinnaka yi wa malamin wani cizon ba, haka kawai a yanke miki irin wann ɗanyen hukuncin? To

wallahi ba zan bar zancen nan ya tafi a banza ba! Sai na je da kaina har makarantar na rama miki duk rashin imanin da suka gwada a kank..."

"To ai ni ban san ta inda ake bi a je makarantar ba. Sannan malamin makarantar mugu ne kamar ɗan Hajiya. Kada ki je don yana iya sa 'yansanda su kama mu a banza."

Bintoto ta faɗa tana ɓata fuska ta tashi daga kan cinyar Kandalar tana goge hawaye. Wani kalar kallo Kandala ta bi ta da shi a lalace kafin Bintoton ta gyara zamanta ta sake cewa,

"Ni babu abin da ya fi ɓata mini rai kamar yadda shi ɗan gidan Hajiyar ya yi ta zagi na, bayan dukan da ya yi mini a cikin motarsa da gabanta da muka zo gidan. Kuma na rantse da Allah ba zan taɓa yafe musu ba dukan su tun da ni ba baiwar gidan uban kowa ba ce a faɗin duniya."

Tsaye Kandala ta nemi miƙewa jikinta yana rawa tana faɗin, "Ai wallahi ba zan bar zancen nan ya tafi a iska ba, dole ne na nuna musu ba su daki banza b...."

"Ki zauna ni dai, ina za ki je a cikin daren nan? Ni fa na faɗa miki babu yadda za a yi na gane inda Makarantar take."

Bintoto ta tambaye ta tana ɗaga kai daga zaunen tana kallon ta saboda ba ta son ta je ko'ina a daidai lokacin, Kandala tana gyara ɗaurin zaninta tana faɗin,

"Gidan tsohuwar banzar Hajiyar zan tafiya. Ai ba baiwa na kai ta yi musu aikatau ba, ke ma kina da gatanki."

"Inna!" Hari ta kira sunanta saboda jin abin da take shirin yi ganin ta ja mayafinta tana ƙoƙarin saka takalmi a ƙofara ɗaki.

"Ke ƙyale ni Hari! Don wallahi ko na je ban gane gidan ba idan na dawo sai na bi dare ina yi musu muguwar addu'a."

"To, ki yi haƙuri ki dawo ki zauna don Allah Inna. Abin nan fa duk bai kai yadda kike kallon sa ba. Aiki dai ne sun ce ba sa so shikenan zance ya ƙare, kuma idan kin fahimci Bintoto da kyau duk abubuwan da ta faɗa an yi mata babu wanda yake gaskiya, ita ce ta tsara abin ta da kanta. Don ga shi ta nuna ba ta so ki tafi, saboda ta san ba ta da gaskiya. Kuma wallahi a yadda Bintoto ta ɓata wa Hajiya rai ɗanta yana iya sa 'yansanda su kama ki su kulle idan kika je yi wa mahaifiyarsa maganganu. Kuma kin ga mu za mu shiga uku, 'yan kuɗin da muke ƙoƙarin tarawa a yi hidimar auren Bintoton su ƙare a wurin 'yansanda."

"Yi mini shiru Hari! Ko lahira za a kai ni ba zan bari a cutar da rayuwar Bintoto ba ina kallo ba!"

Da ƙyar da dabara Hari ta shawo kan Kandala ta dawo cikin ɗakin ta zauna tana haki da ajiyar zuciya, tamkar wadda ta sha gudu tsabar fitinar da ke ranta da faɗar maganganun da duk suka fito daga bakinta. A ƙoƙarinta na son sauke fushin da ke ranta, haka ta yi ta zagin Hajiya, Aliyu da malaman makaranta tare da duk wanda Bintoto ta ce ya dake ta. Tsinuwa kuwa sun sha ta fi cikon kwando. Daren ranar haka Kandala ta cinye rabin sa tana masifa tare da gutsurar goro jefi-jefi tana Allah-wadai da masu kuɗin garin duka. Don tun tana yi Hari tana sauraron ta tana ba ta haƙuri, har ta yi barci ta bar ta tsakiyar shimfiɗarta tana ta mita, Bintoto kam sai faman zuba minshari take yi hankalinta a kwance tana ɗora mata ƙafafuwa duk inda ta ga dama.

Washegari ko wurin aikinta ƙin zuwa ta yi. Ko da Hajiya mai abinci ta kira Hari tana tambayar lafiya ba ta zo ba, cewa ta yi a ce mata zazzaɓi mai zafi ne ya kafce ta, cikin jimami ta yi mata addu'ar samun sauƙi suka yi sallama. Bayan sun karya a gaggauce Hari ta yi wanka ta bar su gidan, saboda ta gaji da mitar Kandala wadda tun asubar farin tana farkawa da zancen ta tashi a bakinta.

Ganin ta fice ta bar musu gidan su kaɗai, Bintoto ta fito ƙofar gida ta zauna tana kallon mutanen da ke ta wucewa. Sannan a gefe ɗaya tana ƙare wa gidanen unguwar kallo tana yatsine-yatsinen fuska tana tsaki. A ranta tana ta faɗin,

'Baƙar unguwa, gabaɗaya talauci ya yi musu mugun kamu. Duk gidajensu tsofaffi babu mai gida sabo, ni yaushe zan iya zama a nan duk ruwan kwatami sun cika musu hanyoyi, mutum yana kallo amai yana shirin zuwa, uhumm Allah Ya ba su kuɗi su huta da warin talauci. Ni dai Allah Ya sa na fita daban, don na samu miji mai kuɗi wanda zai kai ni ƙasar waje mu yi yawo idan na dawo Makka.'

Can ta hango wani yaro yana ta sauri riƙe da leda a hannunsa, tana kallon sa har ya zo daidai ƙofar gidan zai wuce. Cikin sauri ta miƙe tana faɗin,

"Kai zo nan!"

Yaron ya yi mata wani kallo kafin ya ci gaba da tafiyarsa ba tare da ya ce da ita komai ba. A ƙufule ta sha gabansa tana faɗin,

"Don ubanka kana ji ina magana za ka yi mini banza?"

Hannu ya nuna mata yana faɗin, "Ki bari da ni."

Ta buge hannun cikin sauri tana faɗin, "An ƙi a bari da kai, mu ga ledar mene ne a ciki?"

Yana kallon ledar ya ce, "Ƙosai ne na sayo. Ko akwai kuɗinki a ciki na ba ki kasonki?"

"Kan uba! Ni za ka yi wa habaici?"

"Ai ba habaici ba ne baƙar magana ce."

Ya amsa mata kansa a tsaye alamun shi ma jan wuya ne.

"To wallahi yau sai na ga uban da zai hana na dake k..."

Ta cakumo gaban rigarsa tare da ƙoƙarin ƙwace ledar da hannu ɗaya, shi ma yana ƙoƙarin hana ta ta hanyar buge hannun nata da ƙafa. Haushin ya ƙi bari ta karɓa, ta lashe maiƙon ƙosan da ya kama hannunta garin ƙwatar ledar, sannan ta fara kai masa duka. Nan take kokawa ta kacame a tsakaninsu, kasancewar shi ma akwai shi da ƙarfin hali ya dage kare kansa. Amma hakan bai hana ta samun sa'ar kama ledar ta yi ta mammatse ƙosan ba, ganin abin da take yi ne ya saka shi sakar mata ledar ta yi ta mutsuttsukar ƙosan har ta wargaje shi kamar dambu, sannan ta jefar da ledar a ƙasa tana faɗin,

"Gobe idan na ce ka zo ka yi mini gardama."

Ɓacin ran da ya gama kai shi wuya ya saka shi ɗaukar duwatsuna ya dinga jefa mata yana kuka ita kuma tana ta tsallen kaucewa, ko da mutane suka ankara da su har wata sabuwar kokawa ta sake sarƙewa a tsakaninsu. Aka shiga tsakaninsu aka raba damben, bayan yaron ya samu sa'ar yage mata fuska da akaifunsa, wani gefe har ya yi jini.

Kukan da yaron yake ta yi ana rarrashin sa ya sa Kandala fitowa daga gidan, don da ma can hankalinta bai kwanta ba ganin Bintoto ta fita gidan. Hango ta a tsakiyar mutane ya sa ta isa wurin da sasaarfa tana faɗin,

"Lafiya aka zagaye ki haka, me faru?"

A nan take wani matashi ya yi mata bayanin da yaron ya yi musu yana kuka. Bintoto tana riƙe ƙugu ta ce,

"Ai ba ƙosan na ci ba. Ga abin shi nan a ƙasa ya tafi da kayansa. Da ma sai da na ce ya zo cikin lumana amma ya ƙi zuwa har sai da muka yi faɗa."

"To laifin me ya yi miki da za ki kira shi?"

"Aikensa zan yi kuma ya ƙi zuwa shi ne muka yi faɗa."

Daga lafuzanta aka gano ita ce ba ta da gaskiya, mutane suka shiga faɗar maganganu a kan duk abin da ya faru ita ta haddasa komai, duba da bayanin da yaron ya yi. A fusace Kandala ta fisgo hannunta tana faɗin,

"Wuce mu je tun kafin dafin bakin mutane ya kama ki wani abu ya same ki. Saboda mayu sun yi yawa a gari ba a gane su a fuska."

Haushin maganar da ta faɗa ta sa kowa ya hau bakinsa. Ita ma ta shiga mayar musu da raddi, inda ta nuna ƙarara tana goyon bayan Bintoto kuma ba ta ga laifinta ba a kan abin da ta yi wa yaron. Don hatta ƙosan da ke cikin ledar sai da aka buɗe aka ga yadda ta yamutse shi. Kuɗi wani bawan Allah ya ciro ya bai wa yaron ya ce ya je ya sayo wani ƙosan. Shi ya tafi da wanda Bintoto ta hautsine da niyyar raba rigimar ganin yadda Kandala ta hau bakinta, ana ta musayar yawu tsakaninta da masu zafin zuciyar da suka kasa shanye gugar zanar da ta yi musu.

Yaron ya bar wurin yana goge hawaye ya nufi wurin sayar da ƙosan. Sai dai ko da ya je babu ƙosai ya ƙare har wasu suna nema.

"Wallahi idan ba ki rage masifa da jawo mini abin magana ba sai na yi miki dukan kawo wuƙa a cikin gidan nan, baƙar almura!"

Zancen Kandala kenan bayan ta shigar da Bintoto cikin ɗaki tana dungure mata kai. Ganin yadda yaron ya yage mata fuska tana ta yarfa hannu a kan zafin da wuraren suke yi mata.

Sosai Kandala ta ji zafin faɗan da ta jawo mata tun da safe har aka ji mata raunin, bayan takaicin da ta kwana da shi a kan abin da su Hajiya suka yi mata. Tana cikin yi mata faɗan ita kuma tana ƙoƙarin kare kanta da faɗin yaron ne ya ja ta, a daidai lokacin suka jiyo muryar wata mata a sama tana ta rafka sallama a tsakar gidan.

Tare suka fita cikin sauri suna rige-rigen ganin wace ce. Ganin matar da yaron da Bintoto ta gama faɗa da shi; Kandala ta gano dalilin zuwan ta gyara tsayuwarta. Tana haɗe rai ta amsa sallamar alamun duk abin da ta zo da shi za ta same shi.

Bintoto kam baya ta ja, ta bar Kandala ta yi gaba tare da tsayuwa gaban matar suna fuskantar juna ido cikin ido suka dinga yi wa juna kallon hadarin kaji. Kafin matar ta gyara tsayuwarta tana cewa,

"Ƙara na zo kawo miki a kan yarinyar da ta daki Khalifa."

"To idan kin gama sai ki duba fuskarta da ya so fincike mata idanuwa."

Kandala ta yi maganar tana kallon gefe, haushi ya sa matar ta fara magana cikin ɗaga murya ta ce, "Saboda kawai ya ƙi nuna mata ƙosan da ya sayo mana; shi ne fa ta dake shi kuma ta wargaje ƙosan sai da wani ya biya kuɗi, ga shi an je sayen wani ƙosan ba a samu ba, kuma shi kawai ake jira idan sun ci su je makaranta. Yanzu ga shi sun yi latti kuma Babansu bai jira ya yi masa bayanin komai ba ya kama shi ya dake shi, a kan jinkirin da ya yi na dawow..."

"Ni na sa ya yi jinkirin har aka dake shi? Ko kuma ni na ce ya ƙi samo ƙosan? To ba zan yi mata magana ba! Ki je ki yi duk abin da za ki yi tun da ke ma yaron naki ba za ki iya nuna masa girman na gaba da shi b...kuma ba ki ga abin da ya aikata mata a fuska ba!"

Wani kallo matar ta yi wa Kandala cike da mamaki kafin ta fara girgiza kai da jiki tana bubbuga ƙafa ƙasa tana huci ta ce,

"To tun da 'yar haka ce; wallahi, na rantse da Allah idan ta sake taɓa shi hukuma ce za ta raba mu da ku a cikin unguwar nan! Don na gano kawaicin da na so yi a kan Hari ba zai taɓa yiyuwa ba! Sannan na fahimci duk abin da kike nufi, kamar yadda aka sanar da ni ko laifin yarinyar ma ba ki gani ba. To ni babu ruwana da tsufan mutum tun da ba ya son gaskiya, matuƙar aka sake shiga gonata wallahi sai na ɗauki mataki a kanki da ita yarinyar duka!"

Tana gama faɗar maganar ta juya riƙe da hannun yaron za su fice. Kandala ta bi bayansu tana faɗin, "Idan kika kai mu hukumar ki ce su rufe mu ɗan makullin ya ɓace! Ko kuma ki ce su kashe mu tun da rayuwarmu tana hannuns....!"

"Wallahi idan ta kawo iskanci ki dake ta Kandala."

Wani mugun kallo Kandala ta yi Bintoton a kan jin furucinta. A fusace ta yi kanta tana faɗin, "Na dake ta ko ke na ci ubanki? Ai babu wanda ya jawo mini ɓacin ran face ke! Kina ji har da faɗin ba za ta yi wa Hari kawaici ba, to don malfar ubanta ta dawo ta yi duk rashin mutuncin da ta ga dama. Wallahi idan ba ki yi hankali ba a yau ɗin nan sai na kai ki Maidala kin koma hannun Amadu. Shikenan ni babu ranar da zan huta don na haifi uwarki? To ki shiga hankalinki na fara gajiya aure ma zan yi miki na huta da jarfa irin taki. Sai ki je can gidan mijin ki ƙarasa iskancin da ya yi saura. Bari Hari ta zo ta kira mini Jabirun a yi mai yiyuw...."

"Wallahi shi kam ba Jabiru ne sunansa ba. Haka kawai ki ce masa Jabiru sai ka ce talaka wanda bai da gida da mota! Hu'um lalle m...."

Takalmin da ta raruma ta wurga mata a kai ya sa ta yi hanzarin ficewa gidan cikin azama tana gunguni. Kandala ta kai zaune babu shiri tana goge hawayen da take ƙoƙarin dannewa suna ƙin ba ta haɗin kai.

Princess Dija.✍

36.

Wunin ranar gabaɗaya bai yi wa Kandala da Bintoto daɗi ba. Sai da dare Hari ta dawo, a nan Bintoto ta fara kai mata ƙarar Kandala, kafin ita ma Kandalar ta yi mata bayanin duk abin da ya faru.

Hari shiru kawai ta yi tana nazari kafin ta ce, "Inna, wannan dalilin ya sa ban ji daɗin da Bintoto ta bar gidan su Hajiya ba. Saboda zamanta a can zai gyara wasu matsalolin da ake fama da su kanta. Musamman sallah da zuwa makaranta, don na fahimci ko sallah Bintoto buga ta kawai take yi babu sani a kanta. Sannan makaranta, idan tana zuwa yau da gobe tana kama wasu abubuwa su amfani rayuwarta."

"To ya za mu yi? Tun da aikin gama ya gama. A yi mata aure kawai kowa ya huta."

Hari ta ƙura wa Bintoto kallo tsawon mintuna kafin ta ce, "Aure a wannan lokacin da take ciki zai iya kawo wata damuwa. Ganin yadda ko a gida fama ake yi da ita ballantana ta yi aure."

"Idan shi mijin zai taimake ta ai zai fi mu ba ta kulawa. Ko babu komai zai ajiye ta wuri ɗaya babu fita, sannan idan ya so na ga wasu matan aure suna zuwa makaranta a nan birni, sai a saka ta can ta dinga jin wa'azi ko za a samu ta gyara wasu kurakurai."

Ajiyar zuciya Hari ta sauke mai ƙarfi kafin ta ce, "To, babu damuwa, bari idan mijin ya zo sai mu yi magana da shi mu ji yadda za a yi. Amma ni a son raina karatu na fi ra'ayin ta yi saɓanin auren da ake son yi mata a wannan lokacin. Don kwata-kwata ko shekara sha huɗu ba ta ƙarasa ba, kuma auren wuri ko a ilmance an faɗa yana da matsala, musamman a wajen haihuwa a nan yaran mata suke samun yoyon fitsari."

"Laaha'ilaha illalLah! Yoyon fitsari kike yi wa Bintoto fata Hari? Ashe da ma ba kya ƙaunar ta ban sani ba? Cabɗijam! Gara da Allah Ya toni asirinki kika faɗa da bakinki har na ji. To wallahi laƙada ja'akum ki ga yoyon fitsari a kanki ba dai a kan Bintoto b... innalillahi! Lalle Hari ban san ba ki ƙaunar mu tsakani da Allah ba sai a yau. Ikon Allah!"

"Ke ma kin sani Inna tsakani da Allah nake zaune da ku. Sannan ban taɓa yi wa Bintoto wani kallon da ya wuce 'yar da na haifa da cikina ba. To me ma zai sa na yi mata muguwar fatar da ni ma abin zai dame ni idan har wani abu ya same ta?"

"Babu abin da zai same ta sai alheri, tun da ke kin manta lokacin da aka yi miki auren ko girman ta ba ki kai b...."

"To Inna ai kin ga har yanzu ban haihu ba. Ita kuma muna fatar mu ga nata iri a duniya"

"Allah Ya nufe mu da gani Hari. Kin ji abin da za ki faɗa ba ki zauna ki lanƙwashe ƙafafuwa kina yi wa 'yarki baƙin jaye-jaye ba. Allah dai Ya taimake mu mu samu ta sauya rayuwarta ko don gaba."

"Amin Inna."

Daga haka hirar ta tsaya Hari ta miƙe cikin ɓacin rai ta fara dafa musu taliya. Saboda rashin zamanta a gidan ya sa Kandala da Bintoto cin garin kwaki da rana, da daren ma fura Kandala ta sayo ta dama musu. A cewarta ba za ta iya girki da gawayin da Hari take dafa musu abinci ba. Kada ta je garin girkin zaninta ya taɓo gawayin ya kama da wuta ta ƙone a banza.

Misalin ƙarfe bakwai na dare Jabir ya zo, saboda ya tafi gidan su Hajiya direban gidan ya sanar da shi duk abin da Bintoton ta aikata, wanda ya yi sanadin da Hajiya ta dawo musu da ita. Ransa babu daɗi ya fara gaishe da su Hari, ya yi musu jajen abin da ya faru sannan ya koma soron gidan Bintoto ta kai kujerun zama suka zauna.

Fuskarsa babu yabo babu fallasa ya ce da ita, "Za ki koma wata makarantar, amma ta matan aure ce zan saka ki."

Bintoto ta turo baki tana cewa, "To ai ni ban yi auren ba."

"Farawa za ki yi, da mun yi auren sai ki ci gaba. Saboda ba na son a sake kai ki wata makarantar da za ki yi rashin ji a dake ki a banza. Amma ita wannan malamai ba sa duka, sanann kuma 'yan makarantar suna da hankali ba a bari ki yi abin da zai sa a ce kin yi ba daidai ba."

Shiru ta yi masa tana kallon saman rufin soron, har sai da ya gaji da bayanin ta gyara zamanta tana cewa,

"Da mun yi aure da kwana nawa za mu je Makka?"

"Ba zan kai ki ko'ina ba sai kin daina rashin ji, kuma sai kin iya karatun boko da na Islamiyya. Saboda a can Makka kowa da Larabci yake magana, ƙasashen waje kuma inda za mu je shaƙatawa mu huta su kuma da Turanci suke yin magana. Don haka ba za mu je ana yi miki tambayar kalar abincin da kike so ki ci ba ki san komai ba. Haka kawai ki sa na ji kunya kuma su ma su fasa ba ki abincin yunwa ta lalata miki hanji."

"To idan haka ne ai ka saka ni makarantar ka gani idan ban yi karatun ba. Da ma can ni ce nake ƙin tsayawa na gane karatun, amma yanzu zan dinga kallon malamin duk abin da ya faɗa sai na haddace kuma na yi rubutu a littafaina."

Wani farinciki ya kama Jabir, fuskarsa a sake ya dinga zuba mata daɗin baki da kalolin alƙawurran jin daɗi da sharholiyar da za su yi idan suka yi aure, amma sharaɗin shi ne sai ta tsaya ta yi karatu kuma ta gane abubuwan da ake koyarwa."

Ita ma ta yi masa alƙawarin tsayuwar daka ga karatun har sai ta iya Turanci da Larabci. Kafin ta tafi sai da ya ga Hari ya sanar da ita ƙudurinsa, saboda makarantar ta yaƙi da jahilci ce, wadda matan aure da zawarawa suke yi idan ba su samu damar karatun a lokacin ƙurciya ba. Hari ta ji daɗi sosai ta dinga saka masa albarka tana godiya. Ya ce in sha Allahu a cikin kwana biyu zuwa uku yake son ya kammala mata komai ta fara zuwa. Saboda shi ma bai gama gyaran inda za su zauna ba. Kafin ya gama ta samu abin da ta samu a makarantar, don idan sun yi auren ma zai bar ta ta ci gaba har ta samu takardar Sakandare.

"Amma fa inda matsalar take ita Bintoto ba ta da takardu Firamare, ta ya ya za ta shiga Sakandare babu shaidar ta gama Firamare?"

Sai da ya yi jim kafin ya ce, "Zan ga yadda za a yi. Idan ma ba a samu na saye ba sai a sa ta zana jarabawar a wannan shekara wata makaranta."

"To Allah Ya shige mana gaba, kai ma ya saka maka da alheri a kan wannan gudunmawar da za ka yi wa rayuwarta."

***

Kamar yadda Jabir ya shirya haka ta kasance, shiga nan fita nan miƙa kuɗi can bayar a nan, da haka ya samu alfarmar aka bai wa Bintoto takardun Firamare. Sannan ya koma yi mata cuku-cukun samun makarantar koyon yaƙi da jahilcin. Cikin sa'a ya samu ya yi mata registration, sannan ya ɗinka mata uniform masu ɗauke da riga da wando da dogon hijabi har ƙasa, wasu ma har da liƙaf idan suna ra'ayi.

Kandala garin godiya har da kuka ta yi masa tsabar jin daɗin Bintoto ta samu wanda yake son cigabanta. Jabir kam ko godiyar ma ba ya so, saboda tun a ranar da ya fara ganin Bintoto shirmenta da komai nata yake burge shi. Hakan ya sa duk da ya san halayenta ba sa turba mai kyau; amma bai ji a ransa zai iya fasa aurenta ba. Saboda yana so ya gyara mata rayuwa ko babu komai zai yi jihadi.

Bintoto ta fara zuwa makaranta, kuma cikin nasara duk wani rashin jin da take yi a can ba ta yi ba. Saboda manyan mata ne kowa sabgar gabanta take yi. Babu mai damuwa da ita idan ba wani abu aka ga ta yi ba daidai ba a koya mata. Sallah ma a can ta fara sanin yadda ake yin ta, tsakanin raka'o'inta da abin da ake karantawa a cikin gaɓoɓin sallar. Ta ɗauki sati biyu ana koya mata yadda ake yin sallah kafin ta riƙe a kanta.

Sannan malamai da wasu manyan matan da ke bibiyar sha'anin karatun da duk ake koya mata, suna tsoratar da ita sosai a kan hukuncin wanda ba ya cika sallah. Da wannan dabarar Bintoto ta fara cika sallolinta, amma a hakan ma watarana haɗawa

take yi, sallar wuni ɗaya ta yi su a lokaci ɗaya. A cewarta ai wahala ce a ce sai an jira lokaci ya yi kafin a yi sallar. Duk ranar da ba a zuwa makaranta tun asuba take gama sallolinta ta huta. Ba ta faɗa wa kowa sai Kandala a cikin kunne take cewa,

"Kandala na haɗa sallata ta yau duka na yi su na huta."

Kandala ta dungure mata kai tana cewa, "Sannu wadda ta fi kowa sanin yadda ake yin sallah."

"To ai na fi ki, don wani lokaci ma ba duka kike yi ba."

Harara take wurga mata tana muzurai ta ce, "Ku ji mini masharranciyar yarinya. Sai ka ce idan zan je wurin aikina da ke nake zuwa. To na ƙi cika sallar idan ke za ki saka ni aljanna ki fasa."

Hari dai ko shiga maganar tasu ba ta yi, don ita ma ta fahimci Kandala ba kowace sallah take yi a wuni ba. Wani lokaci ma tana jin ana kiran salla amma ta yi zamanta har sai Harin ta yi arwala ta yi sallah ba ta motsa daga inda take ba. Kuma idan ta tashi ma ba sallar za ta yi ba, hidimomin gabanta kawai za ta yi babu zancen yin sallah.

Sau da yawa sai ta so sanar da ita gaskiya, amma tsoron yadda za karɓi abin yake sa ta ji gara yin shiru da fadar abin da zai jawo mata ɓacin rai. Sai dai a hakan watarana take kannewa ta ce,

"Inna ki tashi lokacin sallah ya yi ana ta kira a masallatai."

"Ai ko ba ki ce ba, yanzu nake da niyyar yin ta. Idan ba kafuri ba wa zai ƙi sallah a duniya?"

Hari ta ja bakinta ta yi gum, amma kuma babu jinkiri Kandala take yin sallar saboda gudun sa ido irin na Hari mai gani har hanji.

Bintoto ma mai haɗa sallah wuri ɗaya, idan Hari ta ce ta tashi ta yi sallah, arwala kawai take yi ta dinga doddosawa kamar mai yin sallar gaske. Amma ba ta cewa komai kuma ba ta karanta komai ko a cikin zuciya. A cewarta sallarta ta riga ta kowa kai inda ake so, saboda ta haɗa su gabaɗaya tun asuba ta miƙa.

Ana haka watarana Bintoto ta tashi yin sallar asuba ta ga jini duk ya ɓata mata jiki. Ihu ta fasa tare da ɗora hannu a ka tana kururuwar wayyo ita Allah wani namiji ya shigo cikin dare ya yi mata iskanci.

Hari da Kandala a take suka gano jinin al'ada ne ya fara zuwar mata. Amma ita duk yadda suka so kwantar mata da hankali ƙi ta yi. Kuka ta dinga yi kamar wadda aka ce za a yanka, tsabar tashin hankalin da ta tsinci kanta a ciki. Ta kira innalillahi ta fi sau ashirin tana faɗin don Allah a bincika a gano wanda ya yi mata iskanci, don tsabar rashin imani ya lalata ta cikin dare ba tare da kowa ya sani ba.

Hari ta ja ta zuwa bayi ganin da gaske ba za ta nutsun ba, ballantana ta saurari bayanin da take son yi mata. Ruwan zafi Hari ta saka ta yi mata wanka tas tamkar wata ƙaramar yarinya, ta wanke mata kayan da jinin ya ɓata ta shanya, sannan ta nuna mata yadda za ta kimtsa jikinta, gudun jinin ya ƙara lalata mata kaya ko wuri idan ta zauna.

Bintoto ta shiga tashin hankali sosai, ta yadda ko motsi mai kirki ba ta son yi, ganin jinin ya ƙi tafiya duk ta duba sai ta gan shi. A rana tana shiga bayi ya fi sau goma saboda dubawa ta gani yana nan ko ya tafi.

Kuka kuwa ta sha shi tun suna ba ta haƙuri har suka yi banza da ita. Abinci ma ƙin ci ta yi duk shegen kwaɗayinta tana kallon abincin take yin banza. A cikin kwana ukun da ta yi jinin ko makarantar cewa ta yi ba za ta je ba a dinga kallon ta a ce ga 'yar iska can wadda aka yi wa lalata a cikin dare, har jini ya fito a jikinta.

Don a wunin ranar da abin ya faru zazzaɓi sosai ya rufe ta, ta dinga rawar ɗari bayan Hari ta gama yi mata wankan. Har sai da aka kai ta chemist aka yi mata allura biyu sannan aka samu zazzaɓin ya lafa mata. Sauran allurar ma rantsuwa ta yi a kan ba ta so saboda mai allurar ya leƙa mata ɗuwawu ya gano an yi iskanci da ita.

Ranar da ta kammala kwanakin al'adar kuma Hari gaba ta saka ta da bayani dalla-dalla. Sannan ta nuna mata duk yadda za ta yi wankan tsarki, tana gunguni tana turo baki ta yi wankan tare da cin alwashin duk jinin ya sake zuwa kamar

yadda Hari ta sanar da ita zai zo duk wata; ta rantse da Allah sai ta bar shi ya yi ta zuba a ƙasa tun da mugunta ce kawai za ta sa ya dawo bayan ya tafi.

Ranar da ta koma makaranta faɗa sosai malamai suka yi mata. A kan me ya hana ta zuwa, babu kunya ko ɓata lokaci ta faɗa musu wani mugu ne ya shigo gidan Hari cikin dare ya yi lalata da ita, jinin da ya dinga zuba ne ya sa ba ta samu zuwa makarantar ba. Ganin ya ɗauke ta yi wankan tsarki ta zo, inda ta ƙara da cewa,

"Amma don Allah kada ku ce mini 'yar iska, wallahi daga ni har Kandala da Inna duka ba mu san lokacin da aka yi lalatar da ni ba. Sannan kuma gidanmu a rufe ɗakin ma an rufe da makulli, amma saboda rashin imani sai ya hudo ta bango ya shiga ɗakin ya yi mini iskanci."

Princess Dija.

37.

Mamaki da ikon Allah ya kama su, bayan dariyar da ta bai wa malaman ganin tana hawaye suke ƙoƙarin danneaa. Saboda a bayanin nata sun so su fahimci abin da ya faru. Amma don ƙarin tabbatarwa suka kira wata malama aka ce ta je da ita ta ƙara yi mata bayanin yadda abin ya kasance.

Bintoto tana matsar ƙwalla malamar ta shigar da ita wani ofishinsu ta zaunar da ita sannan ita ma ta zauna. Cikin dabara da nuna damuwa ga halin da take ciki ta dinga yi mata tambaya tana amsawa. A nan malamar ta gano al'ada ce kawai ta zo mata, duba da yanayin girmanta da shekarunta da ta ƙiyasta a ranta.

Duk da ita ma ƙarfin hali ne kawai take yi tana sauraron Bintoton ba tare da ta yi dariyar ba, ganin yadda take ta kuka alamun mai yin iskancin ya ɓata mata rai sosai. Hakan ya sa ta ƙare bayanin nata da rantsuwa tana faɗin,

"Na rantse da Allah duk azzalumin da ya sake dawowa gidanmu ya yi mini iskanci har jini ya fito mini a jiki; ni ko ba zan saka abin da Inna ta saka mini a wando ba. Sai dai jinin ya yi ta zuba tun da so ake yi na mutu a banza jinin jikina ya ƙare."

Dariyar dole malamar ta yi ba don tana so ba, sai da ta gama murmusawa tana ƙoƙarin danne dariyar da ke son haɗa ta da Bintoto. Gudun ta gano abin bai dame ta ba dariya ma take yi. Dole ta saka juriya ta shiga nutsuwarta ta fara yi mata bayanin yadda jinin al'adar yake a ilmance da Addinance. Sannan da dabarar yin sa ga kowace 'ya mace a kowane wata, da kuma yadda za ta dinga tsaftace jikinta idan ya zo kamar yadda Hari ta sanar da ita a gida.

Shiru kawai ta yi tana sauraron malamar, duk da ta so ta amince da zancen nata, amma tuna labarin wata yarinya da aka taɓa yi wa fyaɗe a ƙauyensu, da yadda su Jamila suka ba ta labarin jini ya yi ta fitowa a jikinta yana bin ƙafafuwanta; ta ji a ranta ba gaskiya malamar ta faɗa mata ba. Ita ma kamar Hari ce tana faɗar maganganun ne kawai don ta daina tayar da hankalinta kuma ta bar kuka.

Hannunta malamar ta ja suka fice ofishin, bayan ta ba ta umarnin ta tafi ajinsu za a yi mata karatu. Sannan ita ta koma wurin malaman tana yi musu bayanin yadda suka kwashe. Dariya suka dinga yi dukan su, inda wani daga cikin malaman ya ce, yana ganin kamar kan Bintoto da motsi ba ta da cikakken hankali. Malamar da wasu malaman suka dinga bayyana zallar ƙauyanci ne kawai da ƙurciyar da ke damun ta, don kowa da yadda take zo masa.

A nan hirar tuna baya ta taso a tsakaninsu kowa yana faɗar irin wauta da rashin hankalin da ya tafka ana ta dariya. Shugaban makarantar ya bai wa Malamar nauyin kulawa da Bintoto domin ta wayar mata kai ga duk abin da ya shige mata duhu. Saboda Jabir ya sanar da shi matarsa ce da zai aura lokaci kusa.

Kwanaki da sati-sati suka dinga zuwa suna wucewa. Har ranar da jinin al'adar Bintoto ya sake zuwa bagatatan babu zato. A nan ma an sha fama da ita kafin ta haƙura ta saka audugar da Hari ta tanadar mata saboda irin wannan lokacin. Kandala dai sai murna take yi tana tarairayar ta, har da yi mata farfesun kayan ciki saboda kawai ta rage ƙiyayyar jinin a ranta, bayan ta tabbatar mata duk lokacin da jinin ya zo ba ta tayar da hankalinta ba; sai ta dinga yi mata farfesun kuma ta saya mata duk abin da take so.

Da dabara Bintoto ta saki jikinta har da zuwa makaranta, amma kuma a takure take zama ko fitsari sai ta ji zai ɓalla mata mara ya fito sannan take zuwa ta tsiyaye shi dolenta.

Wasa-wssa Bintoto ta kwashe shekara ɗaya a makarantar ba tare da ta yi wani babban laifin da za a yi mata faɗa ko a ce za a kore ta ba. Saboda su ma malaman kulawar da suke ba ta ba irin ta kowa ba ce, duba da yanayin girmanta a cikin manyan mata, sannan da ƙauyancin da suke so su goge mata shi da ilimin Addini.

Ana haka watarana Kandala ta yi wa Jabir maganar aure, saboda ta matsu ta aurar da ita ganin ta fara hankali ta rage wasu abubuwan da take yi na rashin gaba. Jabir ya gyara zamansa yana yi wa Kandala bayanin halin da yake ciki.

"Ni kaina abin da nake kwana da shi ina tashi kenan. Saboda haka idan kin lura ko gidan nan na rage zuwa. Fafutukata duka ta rataya a kan yadda za a yi na samu abin da zai ishe ni a yi komai a gama. To kin san yanayin kasuwar a yanzu ba kamar baya ba, wani lokaci wuni nake yi ina yawo a cikin rana ba tare da na yi cinakin kirki ba. Amma in sha Allahu a cikin kwanaki kaɗan za a yi komai a gama. Saboda haka a ɗan ƙara mini lokaci."

Kandala tana ƙoƙarin yin magana Hari ta riga ta da cewa, "Babu komai ya ci gaba da nemansa kafin lokacin auren ya yi Bintoton ma ta ƙara hankali."

Jiki babu kuzari ya fice ya bar gidan, ganin yadda Kandala ta damu da dole sai an yi auren a lokacin. Ya shiga nazarin yadda zai samu kuɗi ya gama gyaran da ya ɗebo a cikin gidansu, sannan ya haɗa mata kayan lefen da ya yi niyya.

Zama na musamman ya yi da ahalinsa, suka yi shawara da mahaifiyarsa da ƙanwarsa da ke gidan aure a kan yadda za a ɓullo wa lamarin. A take suka nuna masa kawai ya yi abin da ya gani kada ya jira sai ya yi abin da bai da shi. Amma tuna kalolin dadin bakin da ya dinga yi wa Bintoto da alƙawari kala-kala; yake jin fargaba a duk lokacin da ya tuna ta. A haka ya yi ƙarfin halin ture komai ya nemi a saka masa rana. Cike da jin daɗi aka saka lokacin auren wata ɗaya da kwanaki kamar yadda ya nema ba tare da an ja lokaci ba.

Sannan ya haɗa mata kayan fitar biki daidai abin da ya samu ya bayar aka kai mata. Mutanen ƙauyen da dama sun yi ta sam-barka ganin kaya masu kyau irin na 'yan birni, har da akwaitinta guda biyu masu kyau da wata ƙaramar jakar da aka sako kwalin takalmi taki biyu da jakarsu mahaɗi.

Amma Bintoto tana buɗe ido ta hango kaya kala biyar kacal sai tarkacen su man shafawa da sabulai. Ta fara tijara da borin faɗin ita ba irin kayan take so ba, akwatuna da yawa take so ya kawo mata kowane ya cika shi da sutura.

Ta shiga ɗaga kayan tana faɗar maganganu har ta ci karo da bireziya biyu da ke ciki. Cikin zaro ido ta ɗaga bireziyar sama tana rufe baki ta ce,

"Kan uban nan! Kandala duba ki gani ashe shi ma dai ɗan iska ne. Wai ni ya saya wa bireziya sai ka ce na ce masa ina so. To wallahi ni na ma fasa auren ya zo ya ɗauki kayansa tun da ni zai yi wa rashin mutunci. Bayan maƙon kayan lefen da yake son yi mini har da kayan 'yan iska a ciki. To ba zan aure shi ba ya je wurin 'yan iskan da ya gani suna saka bireziya ya kai musu kay...."

"Wai ke yaushe za ki yi hankali ki gano gaskiya? Ita bireziyar ce iskanci bayan kin gani da idonki ni ma ina sakawa?" Hari ta yi maganar tana haɗe rai ganin abin nata yana ƙoƙarin wuce gona da iri.

" To ai ke ma Inna babba ce ko kin yi iskancin ma ba zan faɗa ki ji da bakina ba. Amma ni yaushe na ce masa ina son bireziya ko ya taɓa ganin ina sakawa da zai siyo ya kawo mini? Gaskiya sai dai ki yi haƙuri Inna amma sai na faɗi gaskiya, duk mai saka bireziya ɗan iska ne."

A fusace Kandala ta mayar mata da amsar cewa, "Ita vest ɗin da kike sakawa tana rufe miki kanun mangwaron da ke ƙirjinki ai a matsayin bireziya take."

"To ke me ya hana ki dinga sakawa? Ai ban taɓa ganin kin saka ta ba shi ne sai ni ake so a mayar 'yar iska haka kawai ina gani na yi shiru a cuce ni a banz...na rantse da Allah ba na son ta sai dai ya zo ya karɓi kayansa."

Ta miƙe cikin fushi tare da ture kayan da ke jikinta ta yi gaba tana turo baki. Kallon takaici Kandala ta bi ta da shi, kafin Hari ta sauke ajiyar zuciya ta magantu cikin wani yanayin damuwa ta ce,

"Ina murna 'yata ta fara girma haƙorin hankali ya fara fito mata ashe har yanzu da sauran aiki a gabanmu. To, bari na cire bireziyar na adana, duk ranar da kika gane gaskiya na san da kanki za ki neme ta."

Daga can inda take tsaye rungume da hannu tana aika wa kayan harara ta ce, "Har da wando fa ya saya mini, sai ka ce an faɗa masa ban da wanduna. Wannan fa wallahi ko ba a so na faɗa sai na yi magana. Kowa ya san akwai iskanci a cikin sayen kayan nan, sai dai kawai a ga laifina a banza. Don ko Babana bai taɓa sayo mini wando ba, Kandala ma wando ɗaya ne ta taɓa saya mini, kuma tun da ya tsufa har yanzu ba ta sake saya mini ba. Sai ke da jini ya fara fito mini a jiki kika sayo mini guda uku. Amma shi yana namiji ko kunya ba ya ji ya saka kuɗinsa a banza ya sayo bireziya da wando don kawai ya raina ni. To ba za a saka su ba, ya je da tsiyarsa tun da kayan ma sai da ya saka maƙo da talauci a ciki. Ko kuma wallahi idan na je gidansa ni babu ruwana duk abin da nake so sai ya saya mini tun da shi ne ya yi mini alƙawari."

"Tun da uwarsa ce ke ai dole ya yi miki duk abin da kike so."

Kandala ta faɗa tana aikata mata harara, "Idan ya ƙi ai sai na dawo gida na fasa zaman auren. Ni fa auren ma ya fita kaina ba na son sa, idan na samu wani Alhaji wallahi ko zai yi kukan jini ba zan taɓa aurensa ba. Sai ya je wurin 'yan iskan da suke saka bireziya ba dai ni ba."

Haka ta dinga surutunta ita kaɗai babu wanda ya bi ta kai, saboda fahimtar halin nata ne ya motsa don da ma can ba inda ya je, ta dai ƙara da sababbin halayen da ta samu suna ƙoƙarin ɓoye na asalin.

Ranar da Jabir ya zo ma da faɗa suka rabu, don kai-tsaye ta nuna masa kayan ba su yi mata ba, kuma ba irin su take so ba. Sannan ta ƙara da bayyana masa abin da ke ranta a kan wando da bireziyar da ya haɗo a cikin kayan, inda ta tuɓure masa da masifa tana faɗin ba za ta aure shi ba, tun da ashe kallon 'yar iska yake yi mata shi ya sa ya saka mata wando da bireziya.

Tana gama faɗar maganganun ta shigo gida ta bar shi a soro da tagumi. Sai da ya kira Hari ya yi magana da ita a kan don Allah ta wayar mata da kai ba wani abu ne mai illa ba. Sannan ya tafi da tunanin yadda za su kwashe da ita idan an yi auren ya nemi kusantar ta.

Kwanakin bikin suna ta ƙaratowa ita ma tana ta ƙara borin ba ta son auren. Har aka zo wata rana tana kan hanyar dawowa gida a cikin adaidaita sahu, jar danja ta tsayar da su suna jiran a ba su damar wucewa. Garin kalle-kallenta kawai sai ta hango Jabir rungume da kayan da yake sayarwa, bulawus da moper tare da makwashin shara da tsintsiya. Yana ta kutsawa cikin abubuwan hawan da ke wurin yana yi wa mutane talla. Ƙara gwalalo ido ta yi tana kallon sa har ya kusa isowa inda adaidaitasahunsu. Daidai lokacin aka ba su damar wucewa mai adaidaitar ya yi gaba tana ƙoƙarin yi masa magana ba tare da ya ji ta ba. Saboda hankalinsa gabaɗaya ya tafi a kan neman halaliyarsa da yake yi babu safiya babu rana, ruwa ko sanyi ba sa hana shi fitowa neman na kansa.

Yatsa ta dinga cizo tana ƙwafa har aka ajiye ta ƙofar gida. Ta fito ranta a matuƙar ɓace ta shiga gidan tana ranste-rantsen ba za ta taɓa auren Jabir ba. Kandala wani mugun kallo kawai ta yi mata ba tare da ta ce mata komai ba. Hari ce kawai da ke ƙulƙulen daddawa a cikin turmi ta samu tambayar wa ya taɓo ta.

Bintoto da ta yi zaman dirsham a tsakiyar gidan ta haɗa kai da gwiwa tana matsar ƙwalla ta fara magana cikin muryar kuka tana cewa,

"Ashe ma ba mai kuɗi ba ne tsintsiya yake sayarwa da wani abu dogo da wani a cikin leda. Na rantse da Allah ba zan aure shi ba don ni mai kuɗi nake so ba irin shi b....."

Kukan da ta fashe da shi ya sa Kandala jefa goro a bakinta tana faɗin,

"Sannu ɗanwake ka fi ubanka! Hamshaƙiya mandiya! To billahillazi ko Habi ta dawo duniya ta ce ba za a yi auren nan ba sai dai ta koma inda ta fito, amma sai kin aure shi. Ba tsintsiya ba ko kashi kika ga yana kasawa a kan hanya sai kin aure shi mara kunyar banza da ta wofi. To sai in ga uban da zai sa a fasa auren tun da kin raina mutane. Haka kawai za ki saka mu zama ƙananun mutane bayan an gama magana? To ai mu mun jima da sanin sana'ar da yake yi, ke ce kawai dogon burinki

ya hana ki gano irin baiwar da a Allah Ya yi miki kina ta hauka. Buɗe kunnuwanki da kyau ba za a fasa auren ba! Uban da duk ya fasa rashin mutunci a kan auren nan malfar ubansa uban da haife sa shi ma ubansa!"

Haka Kandala ta saka ta gaba da masifa tamkar za ta cinye ta da rai. Don da a ce kusa da ita take babu makawa sai ta kai mata hannu ba tare da ta san ta aikata ba. Bintoto ta ja jakar makarantarta ta shige ɗaki tana rantsuwar da take ji a ranta ita ce kaɗai makaminta da za ta nuna ba ta ra'ayin auren.

Tuwon dare ma da Hari ta zuba mata ƙin ci ta yi. Sai da fitsari ya sa ta farka tsakiyar dare ta buɗe kwanon ta cinye abincin sannan ta sha ruwa ta koma ta kwana. Da safe Hari tana ganin babu tuwon ta yi dariya, don ko ba a faɗa ba ta san aikin Bintoto ne. Saboda Kandala ba koyaushe ta damu da cin abincin ba, wani lokaci fura kawai take sha ta yi kwanciyarta.

Bintoto har ta gama shirin zuwa makaranta ba ta ce da kowa komai ba. Sai da za ta fita ta tsaya kan Kandala da ke ta shirin ficewa wurin aikinta ita ma, kai ta juya gefe ta rungume hannu a ƙirji tana cewa,

"Ba ni kuɗin tafiya zan yi."

"Au! Ashe fa kina magana ba kurma kika koma ba."

"Ni dai ki ba ni."

Kuɗin kawai ta wurga mata a ƙasa ta duƙa ta ɗauka ta fice. Sai da ta fita sannan ta dawo tana haɗe rai da maƙale murya ta ce da Hari,

"Inna na tafi."

"Allah Ya kai ki lafiya 'yata."

Hari ta faɗa cikin sakin fuska. Bintoto ta fice bayan ta ce da ita a faɗa wa Kandala ta tafi. Hari tana 'yar dariya ta sake cewa da ita,

"Ita ma ta ce Allah Ya dawo mana da ke lafiya ya ba da sa'ar karatu."

'Amin.' Ta faɗa a zuciya ta fice tana haɗa rai har ta samu abin hawan da zai kai ta makaranta. Lokacin da aka tashi kuma ta jima a bakin titin tana neman abin hawa ba ta samu ba. Tana tsaye rataye da jakarta wata mota ta yi gaba, sannan ta dawo a hankali har ta tsaya daidai saitinta aka fara zuge gilashi. Wani babban mutum kuma dattijo ta gani, mai farin haƙorin Makka biyu a bakinsa yana ta murmushi kafin ya ce,

"Sannu ustaziya. Zo mu je na rage miki hanya."

Jikinta yana rawa cike da jin daɗi ta buɗe gaban motar ta shige babu ɓata lokaci ko wani jinkiri. Fuskarta a sake take kallon sa yayin da shi kuma ya koma kallon titi yana faɗin,

"Ya sunan Malamar? Kuma ina ne unguwarku?"

Sai da ta gyara zamanta cikin zumuɗi sannan ta faɗa masa sunan unguwar su Hari kafin ta koma faɗin,

"Amma ni ba malama ba ce. Malamanmu sun fi ni girma."

Wata kalar dariya ya yi kafin ya kalle ta ya sake cewa, "Da alamu kamar kina da aur...."

"A'a ban taɓa aure ba, ko miji ma ban da shi sai Allah Ya kawo."

Amsar da ta ba shi kenan da hanzari ganin har ya fassara ta bayan ba ta yi auren ba.

"To amma ya na gan ki da kayan makarantar masu aure?"

Sosa kai ta shiga yi kafin ta ce, "Wani ne ya saka ni makarantar, wai don an taɓa kora ta a wata makaranta."

"To fa!"

Dattijon ya faɗa yana 'yar dariya saboda a lokaci ɗaya ya fahimci ƙaramar yarinya ce kuma mai shirme. Ganin yadda ba ta ɓoye masa komai ba, har abin da bai tambaya ba sai da ta faɗa masa. Tun daga kan laifin da ta yi a gidan Hamida har zuwa saka wa malami cinnakun da ya yi sanadin aka kore ta, Hajiya ma ta kore ta gidanta, duk sai da ta faɗa masa.

Dariya ya dinga yi ita ma tana taya shi ta hanyar ƙara yi masa bayanin wace ce ita da faɗace-faɗacen da ake yi da ita, har suka kai bakin jar danja. A daidai lokacin da Jabir ya iso wurin motar saitinta yana faɗin,

" Hajiya ga shi a yi wa gida tsarab...."

Bakinsa ya datse sauran maganar ta maƙale ganin Bintoto a cikin motar Alhajin suna ta dariya.

Princess Dija.

38.

Cikin sauri ta juya kanta suka haɗa ido. Ƙirjinta ya faɗi dam-dam! Amma hakan bai hana ta buga wani kalar tsaki tana maka masa harara ta juya masa baya ba. Daidai lokacin da aka ba da hannu Alhajin ya ja motar cike da mamakin ganin yadda Jabir ya saki baki yana kallon su, yayin da ita kuma yanayinta ya nuna masa ƙarara akwai wani abu a tsakaninsu.

"Wancan kin san shi ne?"

Abin da ya faɗa kenan bayan ya kama titi yana zuba gudu. Hannuwa ta rungume a ƙirji tana huci kafin ta ce,

"Ban ma taɓa ganin mai irin fuskarsa ba."

"Allah Sarki, har na tsammanin yayanki ne. Ganin yadda ya yi kamar akwai wata alaƙa a tsakanink...."

"Babu alaƙar komai ban san shi ba. Wataƙila kuma kama na yi da wadda ya sani."

"Ok."

Alhajin ya faɗa, amma bai yarda da zancenta ba. Saboda ya sani ruwa ba sa tsami a banza. A take ya saka wa ransa Jabir yayanta ne ko kuma saurayinta. Hakan ya sa ya juya kansa yana ƙare mata kallo kafin ya yi dariya. Saboda gabaɗaya ta canza a lokaci ɗaya ta ji ranta ya ɓaci, hakan ya jawo ta haɗe fuskarta tare da cika kumatunta da iska hannuwanta a rungume tana kallon abubuwan hawa ta gaban motar ko ƙiftawa ba ta yi.

Dariyar da Alhajin ya ya sa ta lalle shi ta gefen ido kafin ƙara tsuke fuska ta ce, "Wallahi wancan mutumin ko kaɗan ba na son sa. Ko ganin sa na yi haushi yake ba

ni. Kamar na samu ƙaton dutse na fasa masa kai sai ya fashe ya mutu kowa ma ya hut...."

"Subhanallahi! Wane mutume ne ba kya so har haka?"

Alhajin ya tambaye ta cikin sauri saboda mamakin furucinta. Banza ta yi da shi ba ta ce masa komai ba, ganin fuskarsa a cure kuma ta ƙi cewa komai, ya yi shiru bai sake tankawa ba. Har ya shiga unguwar su Hari ta nuna masa ƙofar gidan ya durfafi wurin.

Motar ya tsayar daidai bakin gidan yana kallon ta da riƙe baki ganin sun kawo amma ba ta yi yunƙurin motsawa ballantana ta fice ya juya.

"Tun da ba za ki faɗa mini wane ne za ki fasa wa kai ba, ki shiga gida kada a yi miki faɗan kin shiga motar wanda ba ki sani ba."

Hawaye ta fara gogewa kafin ta kai kallonta gare shi ta ce,

"Don Allah za ka aure ni?"

"Aure?" Ya faɗa cike bakinsa a buɗe tsabar mamaki. Kafin ya ji wata kalar dariya ta zo masa babu shiri. Kallon sa ta dinga yi hawaye yana zuba a kan fuskarta ya ce mata,

"Ni ba yaro ba ne, kin ga na tsufa har da hurhura a kain..."

"Ai kuma kana da kuɗi. Ni kuma mai kuɗi nake so na aura wanda zai kai ni Makka."

"Wata sabuwa yanzu ni za ki aura?"

"E, saboda ba na son na auri wanda bai da kuɗi."

"To ya yi, ki shiga gida idan na yi shawara zan dawo mu ƙarasa maganar."

Cikin zumuɗi ta ɓalle murfin motar ta fice, shi ma ya yi ribas ya juya tana ɗaga masa hannu har ta daina ganin motarsa. Juyawar da za ta yi ta ci karo da Kandala da ke bayanta tsaye cike da mamaki. Saboda ta ji tsayuwar mota a ƙofar gidan, fitowar da ta yi don ta tabbatar gidan ne aka zo ka ya ya, ganin Motar ta juya Bintoto tana ɗaga hannu zuciyarta ta ba ta ita aka kawo a cikin motar.

Sandarewar da ta yi ne ya sa ta kasa furta mata komai. Zabura Bintoto ta yi cikin matsanancin tsoro ganin Kandala a wurin. Fuska ta haɗe tana turo baki ta nemi raɓawa ta gefenta ta wuce. Caraf Kandala ta cafko hijabinta tana faɗin,

"Wancan da ya kawo ki ƙanen Amadu ne ko yayansa?"

Wani kallo Bintoto ta yi mata kafin ta ƙwace riƙon da ta yi wa hijabinta ta yi ciki tana cewa, "Taimako na ya yi don haka ki daina kiran sunan Babana, amma kuma ni aurensa nake so na yi alamunsa ya nuna mai kuɗi ne."

"Tabbatacciya! Ai har kin aure shi ma ba za ki yi ba! Wallahi na rantse da Allah idan na sake ganin shi a ƙofar gidan nan; ko kuma kika sake shiga motarsa sai na yi miki abin da ba ki yi zato ba. Idan ban da kin rasa mafaɗi wancan garsaƙeƙen ƙaton shi kike kwatantawa da mijin da za ki aura?"

"Yaushe kika gan shi da za ki ce masa ƙato?"

"Na hango gingimemen kansa da ya kusa yin girman motar tasa baƙar kwaɗayayyiya!"

"Wallahi kanki ma ya fi nasa girm..."

"Ke! Ko ma wane iri ne daga yau kada na sake jin ko hirarsa a bakinki, ballantana ya sake yi miki taimakon. Don idan ba ki sani ba ko sani, wallahi zai iya yi miki fyaɗe ya tona masa asiri muna zamanmu lafiy...."

"Ni da ma zai yi mini fyaɗen ina so in dai zai aure n...."

"Innalillahi wa inna ilaihirraji'una! Yanzu Bintoto ke kike faɗar wannan maganar a bakinki? Kin ko san ma'anar fyaɗen da kike zance? To daga kada na sake jin irin wannan mummunan lafazin daga bakinki, Allah Ya daɗa ba ki kariya da duk abin da zai jawo miki naƙasu a rayuwa mu ma ya jawo mana fitina da jin kunyar duniya. Zo..zo na ji me ke faruwa?"

Hari ta ƙare maganar tana jan hannun Bintoto suka zauna, don dawowarta gidan kenan ta ji maganganun da suke yi, amma ba ta fahimci komai a kan rikicin nasu ɗan kullum ba. Don babu safiyar da za ta zo ta wuce ba tare da sun yi abin da suka saba ba. Bayani Bintoto ta fara yi mata tana hawaye.

"Wai Inna wani ne fa ya kawo ni gida, saboda ban samu abin hawa ba ya taimaka mini. Shi ne fa Kandala ta dinga zagin sa wai zai ɓata ni. Bayan shi har furfura na gani a kansa da gemunsa. Amma motarsa mai kyau kuma yana da kuɗi."

"Tooo! Yanzu na gano silar faɗan naku. Wato saboda yana da kuɗi kika shiga motarsa ya kawo ki gida. Ita kuma Inna tana faɗa saboda ba ta so a ce wani abu ya same ki. To bari ki ji, ire-iren waɗannan masu motar a garin nan su suke yanka 'ya'yan mutane. Yanzu idan aka yanka ki mu shiga ina fisabilillahi?"

"To ai ni aurensa nake son yi."

Hari ta ja numfashi kafin ta ce, "Irin su ai ko auren ba sa yi, don duk wadda suka aura sai dai su kashe ta sun sha jininta namanta karnuka su cinye, shi ya sa ma ko auren ma mata ba sa yi da su. Kowa tsoron take yi a kashe ta."

"To ni dai gaskiya ba na son wancan mutumin."

"Wane mutumin kike zance kuma?"

"Talakan da yake so na."

"Amma kuma shi ne masoyinki na gaskiya. Saboda shi yake ƙoƙarin sada ki da rahamomin Allah ga shi kina zuwa makaranta kina samun lada. Sannan kina yin sallah kowane lokaci, to me ya rage miki a yanzu ban da ki yi aure ki haihu mu ci naman suna?"

Cikin sauri Bintoto ta rufe fuskarta da hijabi saboda kunyar zancen nata, musamman da ta ce wai ta haihu. Fuskarta a lulluɓe ta ce,

"To ni Inna ina ma na iya haihuwar."

"Idan lokaci ya yi zan gwada miki yadda ake yi. Don ki haifa mana 'ya'ya goma sha biyu mu yi ta shagalinmu mu kaɗai."

A haka Hari ta ture zancen mai motar suka koma hirar da ta fahimci ta samo kan Bintoto da dabara. Kandala dai tana gefe tana aikin maka wa Bintoto harara zuciyarta tana zafi, a ranta tana ji kamar ta nemo bulala ta zane ta. Saboda rashin hankalinta da dogon burinta ba ƙaramin ƙona mata rai suke yi ba.

Marece sakaliya Jabir ya diro gidan, don ba ƙaramin ƙarfin hali ya yi ba da da bai biyo matar Alhajin ya murɗe masa wuya ya mutu ba. Saboda zuciyarsa babu abin da ba ta nuna masa ba tsabar zafin kishin da ya rufe shi ya haifar masa da zazzaɓi babu shiri.

Kai-tsaye gida ya koma ya kwanta, sai da ya ji ƙarfin jiki da kuzari bayan fushinsa ya faɗa, sannan ya yi wanka ya fito zuwa gidan. Bai nemi ganin Bintoto ba, Hari ya nema, ya bayyana mata abin da idanunsa suka gani. Sannan ya nemi alfarmar yana so a rage kwanakin bikin saboda tsoron abin da zai je ya dawo. Ko kuma a ɗaura auren kafin zuwan lokacin haka zai fi kwantar masa da hankali.

Hari ta faɗa wa Kandala buƙatar da ya zo da ita, ita ma ta yi na'am da zancen, saboda ba ta da nutsuwar zuciya ganin mutumin da shigar ɓurtun da yake son yi a rayuwar Bintoto.

Nan take Jabir ya aika ƙauye wurin dangin Amadu. A gaggauce cikin kwana biyu aka ɗaura auren, ba tare da an sanar da Bintoto ba. Makaranta ma daina zuwa ta yi kwana biyun sai da aka ɗaura ya zo tun da safe ya ɗauke ta ya kai ta. Kuma ya ce idan an tashi ta jira zai zo ya mayar da ita gida. Amma saboda ba ta son ya ɗauke ta, ta fito bakin titin makarantar ta tsaya tana neman abin hawa. Kwatsam sai ga Alhaji mai mota ya durfafo bakin titin, ya tsaya saiti da ita yana murmushi bayan ya zuge gilashin ya ce ta shigo su tafi.

Babu shiri ta washe baki tsabar farin ciki da jin daɗi ta yi hanzarin buɗe motar ta shige. Ya ja suka tafi yana cewa da ita,

"Amaryar mai kuɗi. Yaushe kika ga ya dace a saka ranar auren namu?"

Ta yi hanzarin rufe fuskarta da tafin hannayenta tana leƙensa ta kussuwar 'yan yatsunta tana dariya. Alhajin yana dariyar shi ma sannan ya ce,

"Ina so idan muka je gidan ki haɗa ni da wani a gidanku za mu yi magana."

Cike da farin ciki ta ce, "Inna Hari kake so na kira maka ko Kandala?"

Yana kallon titi ya ce, "Babu wani namiji a gidan naku?"

"Mu kaɗai ne a gidan, saboda gidan Inna Hari ne muka zo ni da Kandala. Amma Kawu Mani yana can garinmu da Babana."

"Na gane, danginku suna ƙauye zama kawai kuke yi a nan garin, haka ne?"

Ta ɗaga masa kai tana 'yar dariya ta ce, "Amma fa ni Na fi son zama garin nan saboda 'yan gayu ne. A can garinmu kuma 'yan ƙauye ne ko Makka ba sa zuwa. Ai kai za ka kai ni Makka idan ka aure ni ko?"

"Makka da Umrah duka zan kai ki idan kina so. Har da wasu ƙasashen ma za mu je yaw...."

"Hu'um! Haka Jabir ya faɗa amma daga baya na gano ashe talaka ne bai da kuɗi. Allah Ya sa kai ma ba ƙarya ce kake yi mini ba."

Ta yi maganar tana gyara zamanta tare da haɗe fuska tana murguɗar baki. Jim ya yi kafin ya yi magana saboda rashin jin daɗin abin da ta furta ya ce,

"Ƙarya kuma?"

"E, ita ya yi mini, ba ka ga lefen da ya kawo mini ba kayan ma kala biyar ne, kuma abin haushi har da bireziya da wando ya saka mini. Sai ka ce an faɗa masa cewa ni 'yar iska ce kamar sa."

"Lefe?"

"E."

"Kina nufin an kawo miki lefe?"

Tana murguɗa masa baki ta ce, "Amma ai ba na son auren. Ni kai nake so na aura shi bai da kuɗi talaka ne."

Shiru kawai ya yi mata ba tare da ya ce komai ba, saboda ya shiga nazarin yin abin da ya dace. Hakan ya sa ya ji ya dace ya ga wata a cikin mata biyun da ta kira

sunansu. Bai sake cewa da ita komai ba har suka isa ƙofar gidan, kai-tsaye ya ce ta shiga ta kira masa Kandala ko Hari. Ta fita da gudu ta faɗa gidan, mintuna a tsakani ta fito da gudu ta koma cikin motar ta zauna tana haki.

"Bari na fita kafin su zo. Ke ma ki fit...."

Zancen Alhajin ya katse saboda kiran sunan Bintoto da Kandala ta yi dafe da ƙirji a cikin tashin hankali ta gefenta.

Daga ita har Alhajin suka kai kallonsu gare ta babu shiri. Kafin Kandala ta riƙe abin buɗe motar tana ƙoƙarin buɗewa da niyyar ta jawo Bintoto ta fito da ita ta ƙarfi. Bintoto ta murɗa abin buɗewar ta ciki da karfi ta turo ƙofar har sai da ta ƙwale wa Kandala kai. Ihu da salatin da ta yi ya sa Bintoto saurin kai hannunta ga goshin nata tana shafawa cike da fargaba ta dinga faɗin,

"Wayyo Allah yi haƙuri. Ke ce ba ki janye ba har na ƙwale ki."

A fusace Kandala ta kai mata dundu a baya kafin ta cakumo hijabinta tana jan ta tana faɗin, "Yau sai kin faɗa mini uban me mai motar nan ya aikata da ke a cikin motar."

Haka ta dinga jan Bintoto tana tafiya tan tirjiya tare da faɗin, "Wallahi ni aurensa zan yi yana da kuɗi kuma ya amince zai aure ni."

Tana maganar tana turo baki, yayin da Kandala ta dage sai ta saka ta gidan ta ƙarfi. Ganin ba za ta iya da ita ba ya sa ta rarumo wani ƙaton dutse ta yi kan motar Alhajin ta sauke a gilashinsa na gaba. Ji kake fassss ta rugurgutse masa kaya, sannan ta koma borin faɗin,

"Sai na yi shari'a da kai matuƙar ka ɓata mini rayuwar Bintoto. Baƙin mugu azzalumi mai furfurar 'yan iska! Irin ku ne ke ɓata yaran mutane! Yarinya da aure a kanta amma kake bibiyar ta? Munafuki ɗan iska mai ruwan la'anannu! Uban me za ka yi da ita idan ba so kake yi ka cuce mu a banza ba? An yi mata auren ma ba za

ka bar ɗaukar a mota ba sai ka yi mana shaiɗanci da baƙar manufar da kake bin mu da ita! Wallahi Allah Ya saka mana a kan duk abin da ka aikata sai mun yi shari'a da kai a gaban Allah. Don haƙƙin aure ba zai bar ka ka huta ba har abada tsinannen Allah da Ma'aiki."

Haka Kandala ta dinga yarfa masa miyagun maganganu tana kuka har ya bai wa motarsa wuta ya juya. Ta bi shi da ruwan duwatsu tana jifar sa kamar wata mahaukaciya har sai da aka riƙe ta.

Nan take mutane suka taru a kanta suna ba ta haƙuri tana ta kuka Hari tana rarrashin ta da maganganun kwantar da hankali suka shige gida. Turus suka yi suna kallon Bintoto, wadda haushin abin da Kandala ta yi wa Alhajin ya sa ta ji gara kawai ta bar musu gidan ta tafiyarta ta huta da halinta.

"Ina za ki je da jakar kaya haka?"

Bintoto tana gunguni ta ce, "Wurin Babana zan koma garinmu. Na gaji da halin Kandala ba zan iya zama da ita ba."

Princess Dija

39.

Hari ta sandare wuri ɗaya tsabar takaici da rasa abin yi, dangane rashin hankalin da Bintoton take shirin aikatawa.

Cikin muryar kuka Kandala ta zagaye su ita da Bintoton ta shige ɗakin Hari tana faɗin, "Ai sai mu tafi tare a yi bikinki a kai ki ɗakin mijinki haka ma ya fi mini alheri."

Hari ta yi saurin karɓe jakar da ke hannun Bintoto ta ja hannunta zuwa cikin ɗakin ranta a ɓace. Zaunar da ita ta yi saman gado sannan ita ma ta zauna bayan ta mayar da jakar inda ta ɗauko ta. Daidai lokacin da Kandala ta gama lalubo wasu kuɗi a inda ta ɓoye su tana ƙoƙarin kwance mugun ƙullin da ta yi wa kuɗin tana cewa,

"Hari, kira Jabiru ki ce masa ya shirya za a kai masa amaryarsa a cikin kwanan nan. Sannan ki karɓo kayan da muka saya a wurin masu shago. Waɗanda kika kai ajiya ma ki karɓo su duka a je a yi mata jeren ɗaki. Da ma sai da na faɗa miki, gara a miƙa masa ita tun lokacin da aka ɗaura musu auren kowa ya huta da mugun halinta. Amma kika ce a jira shi bai gama nasa shirin ba, to ni dai na shirya kai masa ita sai ya ƙarasa shirin tana can gidan nasa."

Hari ta yi shiru ba ta tare da ta ce da ita komai ba, sannan ba ta iya motsawa daga zaman da take yi ba. Har Kandalar ta gama kwance ƙullin ta shiga lissafin kuɗin tana goge hawaye da gefen hannunta tana cewa,

"Abin da ya dace kenan tun da har ta iya haɗa kaya ta ce za ta bar gida ta koma gidan ubanta. Da ta faɗa mugun hannu gara a kai ta gidan mijin kawai a wuce wurin."

Shiru ɗakin ya yi kafin Bintoto ta gyara zamanta tana cewa, "Wai wane aure ne ake zancen an ɗaura? Kuma ni ce ake nufin za a kai gidan miji?"

Wani kallo Hari ta yi mata kafin ta ce, "Aure dai da kika sani ana yi tsakanin mace da namiji shi aka yi miki da Jabir. Kuma tun da kika san salon ki bar gida gara a kai masa ke kawai, da ki je ki faɗa baƙin hannu abin ya zo ya dame mu gabaɗay...."

"To ni yaushe ma aka yi mini auren ban sani ba? Ni fa na faɗa muku ba zan auri talaka ba mai kuɗi nake so."

"Idan kika je gidan nasa za ku yi kuɗin tare idan Allah Ya haɗa arziƙinku wuri ɗay...."

"Wallahi ni ko na je gidansa idan na ga bai da kyawu dawowa zan yi."

Zabura Hari ta yi tana nuna ta da hannu cikin ɓacin rai ta ce. "Wai ke wace irin ɗiya ce ana taro ki kina ƙara botsarewa! Shikenan ke ba ki san kin yi kuskure ba ballantana yanzu ki gano laifinki ki bai wa Inna haƙuri? Ana gabas kina yamma tsabar kin raina mutane! To ki shiga hankalinki tun kafin ki kai ni bango na yi miki mugun dukan da sai an rasa gane kamannink...."

Hari!"

Kandala ta kira sunanta da ƙarfi saboda ganin yadda ta tunzura za ta iya yin abin da ta furta. Cikin sauri Hari ta ce,

"Inna ki bar ni da ita yau na nuna mata ni ma na iya tijara tun da ba ta gane kowane yare sai na ɗaga murya! A kan me za a bar ta tana gwara kanmu ta inda ta ga dama? Gaskiya ni kam haƙurina ya kusa ƙarewa, don haka ki yi shiru ki bar ni da ita Allah ma ya sani kin yi iya ƙoƙarinki a kanta. Yaushe za a zuba mata ido ana tausar ta ana nuna mata hanya amma a ce sai abin da ta ga dama take yi?"

"Haƙurin dai za mu ƙara yi da ita Hari. Saboda na fahimci tun farko ita Allah bai yi ta kamar sauran mutane b...."

"Ba haka ba ne Inna, wallahi tun farko don ba a nuna mata ta yi kuskure shi ya sa rashin hankalinta yake ƙara yin gaba. Amma da a ce an tanƙwara ta tun tana ƙarama da yanzu ba a dinga shan wahalarta da yawa har haka b...."

"Dakata Hari!" Kandala ta faɗa tana mayar da kuɗin inda ta ɗauko su bayan ta sake ƙulle su tamau tana cewa,

"Kada dai a ce da ni kike waɗannan maganganun naki duka. Saboda ni ce na ƙi tanƙwara ta tun tana ƙarama ba ita ce ta ƙi tanƙwara kanta ba. Idan ma don muna zaune cikin gidanki ne kika gaji da mu kika koma faɗa mini magana a fakaice; to kin yi haƙuri tafiya za mu yi mu bar miki gidan gobe-goben nan, gara ki sani ni ma na

gaji da zaman da nake yi a garin nan. Saboda ga shi da aurenta Alhazawa suna ƙoƙarin ɓata mata rayuwa a banza garin son abin duniya da shegen kwaɗayi irin nata."

"To ni dai Allah Ya san komai Inna, tun da ba ki son a yi wa Bintoto faɗa na bar ki da ita ki yi duk abin da kika ga ya fi. In sha Allahu daga yau ba zan ƙara shisshigin saka kaina cikin sha'aninku ba. Na karɓi ƙaddarar rashin haihuwar da Allah Ya ɗora mini na yarda da Habi ta haifi Bintoton ba ni ba. Kuma in sha Allahu ni ma aure zan yi a cikin wata mai kamawa, idan da rabon na haihu zan haihu. Da ma saboda ku na ƙi amincewa da zancen auren, amma tun da haka ta faru babu komai kowa ya yi abin da ya ga zai fisshe shi."

Tana gama maganar ta fice ta bar musu ɗakin. Aikace-aikace ta tsiro a tsakar gidan cikin zafin nama, saboda ranta ya gama ɓaci da halin Kandala da na Bintoton duka. Kuma ta saka wa zuciyarta ko ba su bar gidan a goben ba kamar yadda Kandalar ta faɗa, ita za ta yi aurenta kurkusa ta huta da ajiyar su cikin gida suna caza mata kai a banza.

Sororo Kandala ta yi naɗe da hannuwa tana kallon bakin ƙofa, saboda tun da ta bi Hari da kallo lokacin da za ta fita daga ɗakin; ba ta ɗauke idonta wurin ba tsabar mamaki da wani sabon imanin da ya shige ta nan take. Musamman zancen rashin haihuwar da ta yi, da auren da ta faɗa za ta yi saboda su ta ƙi amincewa.

Ajiyar zuciya ta sauke mai ƙarfi tsabar sanyin da jikinta ya yi a lokaci ɗaya. Don nan take ta ji rashin daɗin fushin Harin da ɓacin ran da ta gani kwance a kan fuskarta, cikin raunanniyar murya mai ɗauke da nadama ta ce,

"Ikon Allah! Ashe Hari kina son mu har haka da yawa ban sani ba? Ni kam da kin faɗa mini wannan maganar tun kafin yanzu ai da tuni kin yi aurenki kin gama. Ina ni ina hana ki yin sunnar Ma'aiki? Ai ko yankan namanmu ake yi a garinmu gara mu koma mu bar ki ke ma ki sarara a cikin gidanki."

Hari ta yi banza ba ta ce mata komai ba, ganin Kandala tana ta jimamin abin tare da maimaita maganar da ta yi mata bayanin barin gidan ta yi aurenta. Hakan ya sa daga can tsakar gidan ta ɗaga murya tana ce mata,

"Idan ma lokacin auren ya yi ai ba a nan zan zauna ba Inna. Ya ce gidana daban zan zauna ba tare da sauran matansa ba."

"To shi wannan gidan sai ki yi ya ya da shi? Ko sayarwa za ki yi?"

"Idan kina da ra'ayin ci gaba da zama garin nan za ki iya zamanki, don ba sayar da shi zan yi ba. Idan kuma ba kya son zaman shikenan sai na zuba 'yan haya su dinga biya na kuɗi duk shekara."

"Allahu Akbar Hari. Ubangiji Allah Ya yi miki albarka. Ban san da wane baki zan nemi yafiyar ki a kan ɓacin ran da na saka ki ba. Ni kaina ban san wane irin hali ne da ni ba, idan na ji ana yi wa Bintoto faɗa sai na ji kamar ana yankan naman jikina. Don Allah ki yi haƙuri da halinmu daga ni har ita Hari. Don yanzu na tabbatar ko ni ce na durƙusa na haife ki iya biyayyar da alherin da za ki yi mini kenan. Wataƙila ma ko Habin ba za ta iya yi mini irin ladabin da kike yi mini b...."

"Za ta yi fiye da haka ma Inna."

Hari ta yi saurin faɗin hakan saboda ganin kukan da Kandala take yi, wanda da ma can a kusa ruwan hawayen nata yake jira kawai take yi a kira shi ya ƙaraso. Daga haka komai ya wuce tamkar babu abin da ya faru. A nan suka shiga tsara yadda za a yi taron bikin Bintoto da zuwa yi mata jere.

Ita dai shiru kawai ta yi musu ba tare da ta ce da su komai ba. Ta jawo littafinta na makaranta tana ta bitar karatun da aka yi mata aka ce ta haddace. Saboda fushin Hari da faɗan da ta yi mata ya shige ta sosai kuma ya kama jikinta. Don koyaushe cikin rarrashin ta take ba ta taɓa ɗaga mata murya ba sai a ranar.

Zuwan Jabir ya sa Hari ƙwala mata kira, a lokacin ta gama sallar magriba ko tashi ba ta yi a kan sallayar ba, saboda tun da rana ya kira Hari a ruɗe yana tambayar ta ta dawo gida. Bayan ta sanar da shi lalle ta dawo sannan ta ce ya zo tana son ganin shi.

Ana gama magriba ya zo, bayan sun tattauna da Harin a kan maganar bikin da tsayar da ranar bikin ta kira masa ita suka gaisa. Duk da ba wata doguwar hira suka

yi ba, ganin ba ta son yi masa magana shi ma ya shafa wa kansa lafiya. Saboda ya tambaye ta ya aka yi ba ta jira shi ya kawo ta gida ba. Ta yi banza da shi ba tare da ta ce masa komai ba, jiki babu kuzari ya yi sallama da su a kan zai dawo wurin Hari su ƙarƙare magana ko bayan sun tafi ne.

Tun da sassafe Kandala ta bai wa Hari kuɗin sayen wasu kayan da suka rage ba a saya ba. Sannan ta ce ta raba alawa da dabino ga mutanenta saboda idan an gama shagali a can ƙauyen a nan za su dawo a gama harhaɗa komai, sannan a kai Bintoto daga nan gidan nata zuwa gidan mijinta. Hakan ya sa suka bar Hari da komai suka nufi ƙauyen.

Suna zuwa Kandala ta iske dangin Amadu ta sanar da su bikin Bintoto ya tashi, ba tare da dogon bayani ba ta ce mijinta ne ya nemi a yi komai a gama yana buƙatar matarsa.

Kasancewar sun bar mata wuƙa da nama a kan hidimar Bintoto da duk abin da ya shafe ta; ba su ja zancen da tsawo ba suka ce Allah Ya sanya alheri. Da ma can sun haɗa abin da Allah Ya hore musu na gado da kujeru daidai ƙarfinsu sun aika mata kuɗin tun lokacin da aka ɗaura auren.

Hari kuma ta kai ta wurin masu gadaje aka zaɓar mata gado na daidai kuɗinsu har da kujerunsa guda uku, kujera ɗaya mai zama mutum biyu, sai ƙwara biyu masu zaman mutum ɗaya-ɗaya. Hari ta ce a bar musu kayan har zuwa lokacin da aka tashi buƙatarsu a karɓa.

Hakan ya sa Kandala ta bar mata sallahun ta yi komai a can birnin yadda ya dace. A nan garin nasu kuma aka fara shagali nan take aka raba goro da alawa. Mutane suka dinga kawo wa Kandala gudunmawar bikin tamkar ba ta taɓa aurarwa ba sai a kan Bintoto. Saboda mace ce mai ƙoƙarin miƙa abin ta a duk inda ta ji hidima ta tashi. Da ma can al'ada ce irin ta mutanen garin duk wanda ya yi maka kai ma idan tasa hidimar ta tashi sai ka mayar masa. Don wani lokaci ma har gida ake zuwa a yi wa mutum takakkiya idan bai biya bashin bikin da aka yi masa ba lokacin hidimarsa. Gudun jin kunya ke sa kowa yake yin ƙoƙarin rama biki tun kafin a yi wa mutum tonon sililin da zai jawo masa ɓacin suna, wanda zai sa a daina ba ka bikin idan an gano kana da matsala ba ka mayarwa.

Tsakanin atamfofi, kuɗi, shinkafa ɗanya, farin wake, manja, manƙuli da dawon fura; haka aka bai wa Kandala su har sai da ta rasa bakin godiya, tsabar ganin su a baje kowa da kalar tasa bajinta. Tukuici ta dinga bayarwa cikin farinciki da jin daɗi, bakinta ko rufuwa ba ya yi ganin duk wannan taron na Bintoto ne.

Ga al'ada irin ta ƙauyen ba sa komai na shagulgula a aure sai a ranar wunin bikin. A safiyar bikin aka dinga ɗora manyan tukane ana ta girka wa mutane abinci. Bayan an gama masu kiɗan ƙwaryar da aka gayyato suka baje tsakar gidan Kandala suna ta kiɗa, mata suna rawa gwanin burgewa. A gefe ɗaya kuma amarya ta ci kwalliyarta tare da ƙawayenta suna cikin ɗaki ko kallon masu rawa ba a bari ta fito yi. Saboda a wurin su amarya ba ta rawa, ko fitowa tsakar gida ba ta yi sai dai mai son ganin ta ya shiga ɗakin da take ya gan ta ya fito.

Bintoto kam duk da ta sha kwalliyarta irin ta amare mai ɗige-ɗigen baƙin kwalli da janbaki a saman goshi da kumatu, bayan ƙamshin da ke tashi a jikinta, amma fuskarta a cure take ko magana ba ta yi wa kowa, har ƙawayen nata su Jamila ƙirjin biki. Kwanciyarta kawai ta yi tana ƙunci saboda tun abin da Kandala ta yi wa Alhajin da ya rage mata hanya, ba ta sake sakin jiki ta yi hira da ita sosai ba. Harin ma ban da ina kwana da sallama da ta yi mata lokacin da za su baro garin ba ta ce da ita komai ba. Duk yadda ƙawayenta suka so ta saki jiki ta ba su labarin birni ƙin kula su ta yi. A haka suka zauna cikin ɗakin jugum-jugum tamkar masu zaman makoki. Sai idan an shigo ganin amarya idan an ce ina take su nuna ta.

Da marece bayan 'yan kiɗan ƙwarya sun haɗa kayansu masu kalangun suka dasa nasu kiɗan a ƙofar gida.

A nan ma mata suka firfito bakin ƙofar gidan suka fara rawa ana zuba musu liƙi. Kandala ta yi ɓarin kuɗin liƙi a ranar kamar ba ta san zafinsu ba. Tsabar jin daɗi da farincikin ganin Allah Ya gwada mata auren Bintoto.

Kula ma da ɗan cikinta amma sai da ta fito ta yi rawar kalangu saboda kawai ta faranta wa Kandala ta ji daɗi. Ganin yadda tun da ta zo garin babu wata matsalar da ta haɗa su. Lafiya lau take yi mata magana cikin fuska tamkar ba ita ba, ganin haka ya sa ita ma ta shiga duk dafe-dafen da aka yi sai da ta sa hannunta. Bintoto ce kawai har lokacin magana ba ta haɗa su ba, asali ma ko inda take ba ta zuwa gudun ta ce ga wani laifin da ta yi mata ta sa Kandala ta ci mata zarafi a cikin jama'a. Mani kuma sai kwanonin abinci yake fitarwa a waje da tire-tire yana kai wa abokansa ganin banza ta faɗi gasasshiya.

Sai da aka kira sallar magriba sannan masu kiɗan kalangun suka kwashe kayansu. Taron bikin ya fara watsewa ana ta yi wa Kandala sallama, saboda ba garin za a kai ta ba, don da a ce cikin garin za a kai ta ana gama sallar Isha mata za su dawo a yi sabon zama don zuwa yi wa amarya rakiya zuwa gidan mijinta idan 'yan ɗaukar amarya sun zo biko.

****

A can birni kuwa, Jabir ya nemo babbar mota aka kwashi kayan Bintoto zuwa gidansa, tare da Hari da wasu mutanen arziƙinta. Maza aka nemo majiya ƙarfi suka shigar kayan gadon da kujerun har cikin ɗakin da Jabir ya nuna musu. Hari ta jinjina wa Jabir ganin yadda ya shafe gidan fes da siminti tare da sabon fenti har a cikin ɗakin Innarsa. Gidan ƙarami ne amma an keɓe wa Bintoto ciki da falo har da madafi da ban ɗakinta cikin ƙuryar ɗaki.

A gefe ɗaya kuma ɗakin mahaifiyarsa ne a jere da nasu katanga kawai ta shiga tsakaninsu. Innarsa tana ta yi wa su Hari sannu har aka gama saka gadon da kujerun da labulanta guda huɗu, aka koma ɗauko kwalayen kuloli aka dinga jerawa cikin madaidaicin kitchen ɗin, sauran kwanoninta cikin ƙuryar ɗakinta aka saka cikin wardrobe don babu wurin ajiye su.

Hari ta shimfiɗa ta sa aka share ɓangaren duka suka saka turare aka rufe aka bai wa Jabir makulli. Sannan ta sallami abokan aikin da abin da ya samu Jabir, Innarsa da ƙanwarsa suna ta godiya. Tare da wasu daga cikin danginsa da suka zo gidan suna ta hada-hadar nasu shagalin bikin da za su yi washegarin ranar, wato ranar da aka yi shagalin bikin Bintoto a ƙauyen nasu.

Tun da safe Jabir ya samo mota uku aka ɗauko Hari daga gidanta suka nufi ƙauyen. Kasancewar mota biyu bus ne na jigila, ɗaya ce kawai wadda ya aro a inda ake bayar da hayar motoci, don a saka masa Bintoto a ciki. Haka suka ɗunguma zuwa ƙauyen Maidala, misalin ƙarfe goma na safiya. Zuwa lokacin gidan Kandala ya ɗauki taron mata ana zaman jiran zuwan 'yan ɗaukar amarya.

Ihu da sowar yara ta sa aka gano sun iso. Nan take gidan ya ɗauki guɗa mata suka cika gidan da guɗa ta ko'ina ana kiran ina amarya ta fito ga masu kai ta nan sun zo. Bintoto da ke cikin ɗakin Kandalar ƙunce saman gado ta dunƙule tana ƙunci. Wata ƙanwar Amadu waton gwaggonta ta isa bakin gadon cikin farinciki ta fara kiran sunanta. Ganin ba ta motsa ba ta jawo ta jikinta tana faɗin,

"Tashi 'yar albarka mai goshin arziƙi ga mijinki nan ya aiko da motoci. Ki gode wa Allah duk ƙauyen nan ba a taɓa samun miji irin naki ba. Don ita uwar Jabirun a bakin titi aka nemo motar da ta kai ta gidan miji. Amma ke ga motoci can a ƙofar gida har guda uku an turo duk wanda yake son zuwa zai samu mazauni."

Tsaki kawai Bintoto ta yi ta yunƙura gwaggon tata ta sauko da ita daga kan gadon tana faɗin, "Ina turare a ƙara fesa miki?"

Kandala ta yi gaba tana tura baki saboda ba ta da niyyar yin magana. Ganin za ta fice fuskarta a buɗe saɓanin lulluɓin da ake son gani ta yadda babu mai ganin fuskarta. Ta yi hanzarin riƙo ta baya tana rufe mata fuska ta ce,

"Don Allah tsaya kada ki jawo mana abin gori a cikin garin nan. Kowace amarya tana kukan barin gida ke idonki ƙamas kuma ki fita haka?"

Tana ƙoƙarin fita da ita Inna Hari da Kandala tare da wasu yan'uwa na jini suka kutso ɗakin. Hari ta ce da da ƙanwar Amadun ta mayar da ita a yi mata huɗuba. Aka zaunar da ita bakin gadon Kandala kowa yana ta faɗar abin da ya iya dangane wa'azin aure da nasihohin zama da miji. Yayin da Kandala ta koma gefe tana ta sharar ƙwalla cike da kewa da alhinin rabuwa da ita.

Sai da kowa ya tofa albarkacin bakinsa a kanta tare da bayyana mata gidan miji ba kamar gidan da ta bari ba ne. A can dole ta yi wa mijinta biyayya matuƙar tana so ta gama da duniya lafiya. Komai ya ce ta yi masa ta yi ba tare da ta yi jayayya ba. A ƙarshe suka rufe nasihohin da yi musu addu'ar zaman lafiya.

Princess Dija.

40.

Kandala tana ta sharƀar kuka tamkar wata ƙaramar yarinya ana ta rarrashin ta. Haka aka fito da Bintoto daga gidan zuwa gidan Amadu. A can ma wasu nasihohin

aka yi mata kafin a kama hanyar birni. Ganin da gaske an rabo ta da garinsu kuma an raba ta da Kandala, ta tuɓure wa mutane a cikin mota da borin ita sai an mayar da ita gida, tana ihun kiran wayyo ita Kandala take so ta gani.

Gwaggwanninta ne suka dira kanta da faɗa tamkar za su cinye ta da ranta, yayin da Hari ta koma 'yar kallo. Saboda ganin yadda suke sakin maganganun da ke nuna ƙarara su ba za su ɗauki iskancin da take yi wa Kandala ba.

Tana sharar hawaye da gunguni a bakinta har aka isa birni. Sannan ta ware tana kallon garin tana ƙiyasin yadda unguwar da za a kai ta take, cikin takaici ta ja tsaki saboda ganin sun saki titi da wucewa unguwannin masu kuɗi, sun kama wani lugu mai gangara suna ta gangarawa. Sannan suka dinga bi ta bakin ƙofar wasu gidaje, waɗanda a ranta ta dinga faɗin,

'Mutanen wannan unguwar ko ya ya suke iya rayuwa a cikin ta?'

Tamkar za ta yi ihu, a lokacin da ta ga mai motar ya tsaya a cikin unguwar, a gefen wani gida mai dogon kwatami, wanda ya ratsa tsakanin gidajen da ke layin har zuwa bakin gidan. Cike da mamaki ta kai kallonta ga Inna Hari, bakinta yana rawa tana cewa,

"Inna wurin wa muka zo a baƙar unguwar nan?"

Hari wani kallo ta yi mata kafin ta girgiza kai ta yunƙura za ta fice ta ce, "Fito mu je ki ga inda muka zo da idonki ki huta da tambaya."

Babu shiri ta ɓata fuska tana yatsine-yatsinen ta ce, "A'a ku tafi dai, zan jira ku a nan."

"Ke dalla fito malama kada ki raina wa mutane wayo. Gidan uban wa n muka zo ba gidan mijinki ba? Ko so kike yi ki nuna wa mutane halinki tun a nan ƙofar gida ki nemi tara mana jama'a? Wallahi ki shiga hankalinki saboda yanzu da baya ba ɗaya ba ne girma ya hau kanki."

Zancen wata ƙanwar Amadu kenan tana maka mata wata kalar harara, da ma can ba sa shiri da Bintoton, saboda ko a cikin dangin Baban nata ita ce masifaffiya kuma ta jima da sanin ba ta son ta.

'Ki ci kanki ba dai ni ba uwar masifa.'

Abin da Bintoto ta faɗa kenan a ranta tana fitowa daga motar, saboda mugun kallon da take wurga mata mai kama da shirin kai mata duka. Inna Hari ta rufa mata fuska sannan ta ja ta sauran matan suka rufa musu baya. Bintoto da ƙyama ya tsallake kwatamin ƙofar gidan tana toshe hanci har suka shiga cikin gidan. Ƙamshin fentin da gidan ke yi ya sa ta ɗan ware bayan an kai ta ɗakin Innar Jabir an zaunar da ita. Mata suna ta guɗa ana ta ihu sannan ana ta leƙen ta saboda kowa yana so ya ga fuskarta.

Kanta a duƙe tana sauraron muryar Innar Jabir da wasu daga cikin danginsu suna ta zuba addu'a da nema musu zaman lafiya da albarka a cikin auren nasu. Kafin wata taubashiyar Jabir ta isa inda take ta yaye rufin fuskarta tana faɗin,

"Ke buɗe idonki mu gani wa kike jin kunya a nan?"

Bintoto ta ɗaga kai tana wurga mata harara da jajayen idanuwanta da kuma ruwan hawayen da ya gama ɓata mata fuska. "Ashe amaryar ma ta Jabir ƙwaila ce, to kalle ni da kyau kafin ki ba shi abinci sai kin fara zuba nawa kin aika mini har gida. Ba harara ba ko cire idon za ki yi babu ruwana tun da kika yi gangancin aurens..."

"Na rantse da Allah ki rufe mini fuskata ni ba na son rashin hankali. Tun da na zo kike ta mini surut... wallahi zan cire mayafina mu dambatu da k..."

Kukan da ya taso mata gabaɗaya ya hana ta ƙarasa maganar. Cike da mamaki sauran mutanen da ke cikin ɗakin suka dinga kallon ta. Yayin da kunya ta rufe danginta da suka kawo ta har cikin ɗakin. Inna Hari ta miƙe da hanzari bayan ta wayance maganar da cewa,

"To tashi mu je tun kafin tsautsayin amarci ya sa garin damben a buge miki fuska."

Tana gama maganar ta mayar mata da lulluɓin fuskar, sannan ta kama ta suna ƙoƙarin ficewa daga ɗakin. Abokiyar wasar Jabir ta biyo su tana faɗin,

"Idan damben kike son yi ki jira mijinki ya dawo ku yi ta fama, ni kam ba zan yi kokawa da ƙwaila ba ta cije Ni a banza ta bar ni da allurar totunos."

Dariya wasu suka saka, yayin da suka bar wasu da tunanin Bintoton wace irin kala ce a cikin mata. Saboda ganin yadda ta furta maganar cike da rashin kunya, babu shayin kowa ballantana ta ji nauyin surukantaka.

Har ƙuryar ɗaki Inna Hari ta kai ta, mata da yara suka dinga tururuwar zuwa ganin ta. Aiko ta shiga aika musu harara duk wanda ya haɗa ido da ita a kallo ɗaya yake juyawa, saboda mugun kallon da take bin kowa da shi tana kumbura fuska.

Da dabara Inna Hari ta samu yaran suka fice daga ɗakin ta rufe ƙofar ƙuryar tana haɗe fuska ta isa gabanta tana faɗin,

"Wallahi-wallahi sai kin gyara halinki matuƙar kina so ki yi zaman lafiya da kowa a cikin gidan nan. Saboda rashin hankalin da kike yi a can gida wannan gidan babu wanda zai ɗaukar miki shi. Ki duba ki gani tun kafin a je ko'ina har kin fara raba wa kanki abin magana cikin dangin mijinki. Yanzu idan ban da rashin mutunci ita wannan baiwar Allah da kika gwaɓa wa magana tsararki c....?"

"To ita ba ki ji irin maganganun da take yi mini ba? Haka kawai har da ce mini ƙwaila."

"To ai ke ƙwailar ce, don kin tabbatar mata ba ki da cikakken hankali ta hanyar amsar da kika ba ta. Tun da ke ba ki san wasa ba, daga magana ki hau kanta da zancen dambe a gaban sarakuwarki? To billahillazi idan ba ki iya sarrafa fushinki da kame bakinki ba ke ce a ruwa. Don mu tafiya za mu yi mu bar ki da su, ba zama za mu yi muna yi miki nasiha ko rabon faɗa ba idan kin jajibo. Sannan Kandala da ta saba tare miki rigima ba ta san ma an yi ba, ke kaɗai za ki zauna kuma ke za ki ji da kanki, mijin ma da kike gani ba zai taɓa shiga cikinki ba ya bar 'yan'uwansa. Sannan

ba ki kyautata musu ba shi ma ba za ki ji daɗin zama da shi ba. Saboda haka tun wuri ki kama kanki da aikata abin da zai dame ki, kuka ki kulle bakinki matuƙar kika san ba alheri ne za ki faɗa ba."

Zancen wata yayar Amadu kenan saboda ita kanta ba ta ji daɗin abin da Bintoton ta faɗa ba. Haka suka saka ta gaba kowa yana tofa albarkacin bakinsa. Kafin su buɗe ɗakin a dinga shigowa ana yi mata Allah Ya ba da zaman lafiya.

Da misalin ƙarfe ɗaya na rana aka kawo musu abinci. Suna ci suka yi sallah kowa ya fara haramar tafiya. Daidai lokacin Jabir ya shigo gidan mata suka dinga yi masa guɗa, abokiyar wasarsa kuma ta dinga tsokanar sa da mijin ƙwaila. Yana ta dariya baki har kunne ya isa sashensa, inda aka sanar da su Hari ga shi nan ya zo su yi sallama. Da ma can ita ta kira shi saboda kunyar mutane ta hana shi shiga gidan.

Kansa a ƙasa ya shiga gaishe da su suna ta amsawa cikin sakin fuska. Kafin su koma ba shi amanar Bintoto tare da nuna masa sai ya yi haƙuri kuma sai ya dinga ɗora ta a hanya. Duka ya ce ya ɗauka ai aikinsa ne tun da shi ne mijinta. Ya ciro kuɗi ya damƙa musu suna ta godiya ya ce idan sun tashi tafiya motocin da za su mayar da su suna ƙofar gida. Suka shiga yi wa Bintoto huɗubar zama da miji da haƙuri da duk abin da ta gani, ta ji ta yi kamar ba ta ji ba, idan ta gani ma ta yi kamar ba ga komai ba. Saboda zaman lafiya da neman albarkar auren.

Ita dai kallon su kawai take yi, duk da sosai faɗan da suka yi mata na raina manya ya shige ta. Kuma ta ci burin gyara halinta don Allah ba don tana son zaman auren ba. Haka suka tafi suka bar ta tana gungunin cewa ita ma tana tafe da an kwana biyu don ba za ta iya rayuwa a gidan ba.

Da ma can ko ƙawayenta da aka zo da su ba a bar kowa ba, duk da sun so tsayawa su yi sayen baki kamar yadda aka saba yi a al'adance. Ƙanwar Amadu ta ce babu wanda za a bari gidan, tun da ba gari ɗaya ba ne ballantana idan dare ya yi su nemi gidajensu. Amma a haka sai da abokan Jabir suka ba su kuɗin sallamarsu kamar yadda shi ya buƙata, saboda ya san Bintoto ba za ta ce a yi musu wani abin kirki ba.

Haka suka Hari suka koma ƙauyen kowa yana faɗar albarkacin bakinsa, dangane halayen Bintoton da yadda suke jin fargaba da tsoron ta'adin da za ta yi idan ta samu dama. Duk da Hari ta ja Jabir gefe ta ja kunnensa a kan ko da wasa kada ya

bari ta raina shi, sannan ya tirsasa ta yin abu matuƙar shi yana so. Sannan kada ya ɗaga mata ƙafar da za ta dinga jayayya da shi gudun ta kunya ta shi a idon mutane.

Ta ɓangarensa kuma, har dare ya yi bai daina tunanin huɗubar Inna Harin ba. Saboda shi kansa ya san aiki ne ja a gabansa zama da Bintoto a wuri ɗaya. Amma dole ya ƙarfafa kansa a matsayin shi ne mijin, saboda fita kunyar masu ganin wautarsa na auren ƙaramar yarinya. Duk da shi ɗin ma ba wani babba ba ne, don duka shekarunsa a duniya ashirin da bakwai ne, amma abokansa da yawa sun tsani auren ƙwaila, kuma sun nuna masa wani lokaci rainon ma wahala ne, gara yarinyar da ta gama girma a gaban iyayenta. Musamman ma ita tashin ƙauye, wadda ba ta san komai ba sai rayuwarsu ta ƙauyanci.

Shi kam ya ce shan koko ɗaukar rai, ya ji ya gani idan ba Bintoto ba sai rijiya. Dole suka bar shi da kayansa saboda ganin shi ne mai yi su 'yan Allah Ya sanya alheri ne.

***

Bintoto tana zaune ita kaɗai cikin ƙuryar ɗakinta da tagumi don ta kasa kwantawa, misalin ƙarfe tara da rabi na dare Jabir ya shigo ɗakin da ledodinsa ya ajiye a bakin gadon. Bakinsa har kunne ya dinga yi mata wani kallo kafin ya isa ya zauna kusa da ita yana cewa,

"Amarya ba kya laifi ko kin kashe ɗan masu gida."

Ba ta ɗaga kai ta kalle shi ba, kamar yadda ba ta motsa daga zaunen da take ba. Hannunsa ya kai ya nemi jawo ta jikinsa, ta zabura babu shiri tana kallon shi bayan ta buge masa hannun ta ce,

"Na shige su! Mene ne haka kuma?"

Guntun gemunsa ya shafa kafin ya yi mata wani kallo ƙasa-ƙasa da ido yana sake cewa, "Mijinki ne Fatima. Buɗe idonki da kyau ki gan ni yau ranar farinciki ce gare mu duka."

Wani kallo ta yi masa mai ɗauke da harara kafin ta ce, "Ni tun ranar da na gano kai talaka ne na daina son ka. Sannan don mugunta kai da su Kandala kuka haɗa kai kuka yi mini aure ba tare da na sani ba. Alhajin ma da ya so ya aure ni Kandala ta kore shi har da fasa masa gilashin mota. Don haka ni ba matarka ba ce, kuma kada ka sake taɓa mini hannu ko wutar hawuya ta cinye naman jikinka."

Shiru ya yi na ɗan lokaci kafin ya sauke ajiyar zuciya ya ce, "Muhimmancin miji a wurin matarsa ya wuce haka Fatima Don komai na yi da ke lada zan samu, hannunki ma idan na riƙa lada akwai ladar da Allah zai ba ni, ballantana na yi kwanciyar aure da ke kin samu rabo."

Kallon mamaki ta dinga yi masa kafin ta ce, "Shi auren ma har da wata kwanciyarsa ake yi? To ni ban iya kwanciyar ba, rabon ma da ka faɗa ba na so na samu a bar ni a haka, iya cutar da kuka yi mini ta kawo ni wannan unguwar ma ya is..."

Rungumo ta ya yi gabaɗaya a jikinsa, babu shiri ta ture shi ta miƙe tsaye jikinta yana rawa ta shiga nuna shi da hannu idonta a zare tana cewa,

"Wai ashe da ma kai ma ɗan iska ne ban sani ba?"

Fuskarsa ya haɗe wuri guda shi ma ya miƙe yana cire babbar rigarsa yana faɗin, "Idan ma ɗan iskan ne ni zan koya miki yadda ake yi mu iskance tare. Ga kaza da doya da ƙwai nan na sayo mu ci idan muka yi sallah."

Zancensa na ƙarshe ya hana ta ficewa daga ɗakin kamar yadda ta yi niyya. Don batun iskancin da ya ce zai koya mata ya ba ta tsoro matuƙa, amma kazar da ya faɗa da doyar sun saka ta jin wani sanyi a zuciya. Tana laɓe jikin ƙofar ƙuryar tana satar kallon ledodin ya shige bayi, cikin sauri ta rarumo leda ɗaya ta buɗe, jikinta yana rawa ganin banza ta samu ta fara yago cinyar kaza ta kai bakinta. Ko da ya fito daga bayin ya hango ta tsaye tana ƙoƙarin taune ƙashin cinyar. Dariya ya so yi, amma ya basar yana faɗin,

"Ki shiga ki yi arwala ki zo mu yi sallah."

Tana lasar hannunta ta ce, "Ai sai ka jira na cinye ledata sai mu yi sallar."

"Ledarki kuma?"

"E." Ta amsa masa tana murguɗa baki.

"Ai ledodin duka namu gabaɗaya kuma tare za mu ci. Ki ajiye idan muka gama sallah sai mu ci."

Tana hararar shi ta ajiye ledar ta nufi bayin tana gunguni saboda jin haushin ya hana ta cinye kazar, don salon rowa kuma wai har da shi ba ita kaɗai ba.

Ta yi arwalar tana ɓata fuska ta fito, hijabi ya miƙa mata ta karɓa ta saka. Suka yi sallar daban-daban, bayan kuma ya yi mata bayanin tare da za su yi duk abin da ta ga ya yi ita ma ta yi. Amma ita kaɗai ta yi tata a ranta tana faɗin,

'Ku ji mutum, sai ka ce wani liman a masallaci. Ai wallahi ba zan bi ka ba don ko kiran sallah ban ji ka yi ba, amma don don girma haka kawai ni zan bi shi.'

Addu'a ya shiga yi musu tare da fatar zaman lafiya da zuri'a ɗayyiba. Amma har ya shafa ita ba ta shafa ba, sai da ya juyo yana kallon ta sannan ta shafa tana haɗe fuska ta miƙe. Hijabin ta cire ta faɗa kan gadon ta kwanta tana rufe ido.

Jim ya yi na ɗan lokaci kafin ya nemo plate a kitchen cikin kayanta ya zube musu doyar da ƙwan, sannan ya shiga ɓalle kazar da ta fara ci yana ɗorawa saman doyar.

Saman gadon ya ɗora plate ɗin bayan yana kai doyar bakinsa yana faɗin, "Ki taso mu ci ko na cinye kayana."

Zumbur ta zabura cikin fushi ta zaune tana kallon Plate ɗin tana kumbura fuska ta ce,

"Raba ka ba ni nawa ban yarda da cin zalin ba."

"Ai tare za mu ci. Idan kina so na bar miki duka kuma sai idan kin yarda mu kwana a kan gado ɗaya."

Girman gadon ta kalla kafin ta ce, "To kada ka kuskura zuwa kusa da ni a cikin barci. Idan ka yarda ba za ka matso inda nake ba ni ma na yarda."

"To shikenan, ga shi ki cinye duka bari na je na yi wanka na dawo."

Cike da jin daɗi ta ja plate ta dinga ci tana rawa da kai har da 'yar waƙarta alamun tana cikin farinciki. Ko da ya fito daga wankan ya tarar da har ta cinye ta juya kwanciyarta. Murmushin mugunta ya yi bayan ya sauke plate ɗin daga kan gadon ya ajiye ƙasa yana goge ruwan jikinsa.

Princess Dija.